**COURSE GUIDE**

# HAU 201
# SURVEY OF THE LITERATURE IN HAUSA

**Course Team** Professor Ibrahim Malumfashi (Marubuci) -
Kaduna State University Kaduna
Professor Atiku Dunfawa (Wanda ya tace Rubutu)
Usmanu Danfodiyo University -Sokoto

**NATIONAL OPEN UNIVERSITY OF NIGERIA**

© 2023 by NOUN Press
National Open University of Nigeria
Headquarters
University Village
Plot 91, Cadastral Zone
Nnamdi Azikiwe Expressway
Jabi, Abuja

Lagos Office
14/16 Ahmadu Bello Way
Victoria Island, Lagos

e-mail: centralinfo@nou.edu.ng
URL: www.nou.edu.ng

All rights reserved. No part of this book may be reproduced, in any form or by any means, without permission in writing from the publisher.

Printed 2023

ISBN: 978-978-058-848-9

**CONTENT** **PAGE**


Gabatarwar Darasi…………………………………..…. iv
Manufar Darasi (Course Aim)………………………… iv
Yadda Za a Nazarci Kwas (Working Through the Course) iv
Kashe-kashen Kwas (Study Units)…………………….. v
Jarrabawar {arshen Darasi (End of Course Examination).. vii

**Gabatarwar Darasi**

Wannan darasi mai sunan HAU 201, darasi mai ƙunshe da kashi biyu (Two credit units) na shekarar karatu ta ɗaya, musamman ɗaliban nazarin Hausa. Har wa yau, darasin yana ƙunshe da rukunai uku masu ƙunshe da kashi goma sha huɗu (14 units) wanda a ciki aka gabatar da bayanin a kan amfani da harshen Hausa. An samar da wannan abin da karatu ne don ya dace da ɗalibai na shekarar karatu ta ɗaya a jami'a.

Bugu da ɗari, wannan bayani shimfiɗa ce a kan darasin da yadda ya kamata a yi amfani da wannan abin karatu wato hanyar bin su daki-daki a natse domin ƙaruwa da ilimin da yake cikinsu. Kowane kashi akwai buƙatar a yi nazarin sa, sannan an goya shi da tambayoyin auna fahinta, waɗanda amsa su, zai sanya a riƙe karatun da kyau don samun abin rubutawa wanda zai ga samun gagarumar nasara ga jarrabawa. Kar a manta cewa, ayyukan auna fahinta suna samar da kashi talatin cikin ɗari na sakamakon da ake buƙata. Ita ko babbar jarrabawa tana da kashi saba'in, wanda zai ba da kashi ɗari cif! Saboda haka, yana da matu}ar muhimmanci a mayar da hankali ga ayyukan auna fahnita, domin da su ne za ka auna ƙwazonka kafin babbar jarrabawa. Sannan littafan ƙara nazari suna da matuƙar muhimmanci, a nema su a karanta don ƙara ilimi, musamman na ɗakunan karatu da waɗanda suke jibge a kafar samun bayanai ta intanet. ƙofa buɗe take, domin neman ƙarin bayani ga duk wani abu da ya shige duhu.

**Manufar Darasi (Course Aim)**

Kowane darasi akwai wasu saƙonni da suka zama su ne ake son isarwa ga ɗalibai. Saboda a sami ingantaccen karatu da koyarwa, an fitar wa da kowane kashi manufa ta gaba ɗaya tun daga farkon darasi. Kawo wannan manufa daga farko za ta ba ɗalibai damar sanin inda kwas ɗin ya fuskanta tun farkonsa, da abin da ake sa ran su gane cikinsa. Wannan zai taimaka wa ɗaliban su san cewa ga abin da kwas ya ƙunsa da abin da ake son su sani ko su yi. Darasin ya ƙunshi darussa masu yawa, to amma muhimmai daga ciki su ne kamar haka:

1- Mene Ne Adabi?
2- Mene Ne Zube?
3- Ire-Iren Zuben Hausa
4- Hukumar Ƙasa Da Ƙasa Da Samuwar Rubutaccen Zube

**Yadda Za a Nazarci Kwas (Working Through the Course)**

Darasin yana da tsari wanda zai ba ɗalibai damar yi wa kansu jagoranci cikin sauƙi ba tare da wata matsala ba. Hakan zai samu ne ganin an yi wa kwas ɗin tsarin rukuni-rukuni mai ƙunshe da kashi-kashi da suke bi-da-

bi. Kowane kashi yana da dangantaka da ɗan'uwansa bisa rabon da aka yi masu. Don haka, natsuwar ɗalibi zai taimaka wurin gane darasi tare da auna fahimta ta yin la'akari da auna fahimta da jingar da ake gabatarwa a ƙarshen kowane darasi. Jingar da ke zuwa a duk ƙarshen kowane kashi, za ta taimaki ɗalibai yin hasashen irin tambayoyin da za a yi na jarabawa a ƙarshen kwas. Bin wannan mataki dama ce wadda idan an bi, ɗalibai suna iya dogaro da kansu ba tare da neman gudummuwar Malami ba. Kwas ɗin yana da lokaci na tsawon sati 15, wannan ya nuna cewa kowane kashi na kwas za a koyar da shi a kowane sati. Hakan ya sa aka yi jadawalin kwas ɗin daidai da lokacin da zangon karatun ya ƙunsa.

Idan ɗalibai suka dage da nazarin kwas lokaci bayan lokaci, dama ce wadda ba sai ɗalibi ya dinga kasancewa tare da malami ba a kowane lokaci. Wato ɗalibi zai sauƙaƙa wa kansa ba tare da ya yi ta tuntuɓar malamansa domin neman ƙarin bayani ba. Bin kowane kashi mataki-mataki zai taimaka tare da amfani da jerin abubuwan da malami ya bayar domin yin jagoranci wurin samun ƙarin bayanai na faɗaɗa bincike da nazari. Akwai abin da ya dace ɗalibai su mayar da hankali kansu.

Waɗannan abubuwa su ne:

1. Duk darasi ko kwas ya ƙunshi rukuni 4.
2. Kowane rukuni yana da kashi 3 ko 4 ko 5.
3. Kowane kashi yana da sashen auna fahimta.
4. Kowane darasi yana da jingar da za a yi a gida.
5. Kowane darasi ko kwas akwai manazarta da wasu wuraren da ake iya nemo ƙarin bayanai domin yin nazari.

**Kashe-kashen Kwas (Study Units)**

An raba wannan kwas zuwa rukuni huɗu, kowane rukuni yana ƙunshe da kashi huɗu in ban da rukuni na huɗu wanda kashi biyu ne rak. Kowane rukuni yana matsayin darasin da za a gudanar a sati (mako) guda. Ke nan ana da darussan sati 14 kafin kwas ɗin ya kammala. An yi tambayoyin auna fahimta a ƙarshen kowane kashi. Waɗannan tambayoyi idan ɗalibai suka nazarce su tare da yin jingar da ke biye, darasin zai yi taushi ƙwarai ga ɗalibai.

A ƙoƙarin ganin ɗalibai sun fahimta tare da samun cikakken bayani, an kawo manazarta domin ta taimaka wurin samun bayanai game da darussan da aka gabatar. Neman su tun wuri zai taimaka, ba sai lokaci ya ƙure an nema a rasa ba. Sauran litatafai masu bayanin hanyar amfani da harshen Hausa waɗanda ba a ambace su ba, su ma za su taimaka ƙwarai in an same su.

**Auna Fahimta (Assignment)**

Fasalin irin wannan karatu ya nuna cewa ɗalibi ba sai ya ga malami a zahiri ba, don haka ne aka samar da hanyoyi na jaraba fahimtar ɗalibi. Hanyoyin da ake amfani da su suna da yawa. Daga cikin hanyoyin akwai kawo tambayoyin auna fahimta a ƙarshen kowane darasi, daga bisani a bayar da jingar wadda ɗalibai za su yi a ƙarshen darasi; daga ƙarshe kuma a gabatar da jarabawar ƙarshen zangon karatu mai nuni da darasi ya ƙare.

Zubin auna fahintar da ake yi a duk ƙarshen darasi, tamkar wata jarabawa ce ƙarama; to sai dai tana ɗauke da maki 30 daga cikin kaso 100. Wannan ya nuna idan dalibi ya amsa tambayoyi 2 cikin uku da za a bayar, ke nan kowace tambaya tana da maki 15. Ragowar maki 70 su ne za a samu daga jarabawar ƙarshen kwas ɗin.

Tsarin hanyar da aka yi amfani da ita wurin koyar da ɗalibai ba tare da dole sai sun ga malami ba, haka ya sa ana yin jarabawa daga gida, amma ba a cikin ajin darasi ba. Za a tsara rana da lokacin da za a gudanar da jarabawa kamar yadda aka tsara koyar da darussa a wasu ƙayyadaddun lokuta. Ana yin jarabawar ta hanyar intanet. Hakan ya nuna tilascin sani da naƙaltar na'ura mai ƙwaƙwalwa abu ne da ya zama wajibi baya ga muhimmancinsa ga ɗalibai.

**Jinga (Tutor Marked Assignment)**

A duk lokacin da aka bai wa ɗalibi jinga, to ya sani cewa, wani shiri ne da zai ba ɗalibai dama ta ganin yadda tambayoyin jarabawa za su iya kasancewa tun kafin zuwanta. ƙoƙarin iya amsa jingar kowane kashi na darasi ga ɗalibi, dama ce gare su da su fara naƙaltar yadda jarrabawa za ta kasance a ƙarshen zangon karatu. ɗaliban da suka yi azama wurin yin ƙoƙarin amsa jinga, sun sauƙaƙa wa kansu fuskantar amsa tambayoyin jarabawa wadda za a yi a ƙarshen darasi. Saboda haka, yana da kyau idan an bayar da jinga a yi mata nazari mai kyau tun daga fahintar tambaya, da irin bayanai da misalai nagartattu da suka dace. Jingar da ake bai wa ɗalibai tana da wani kaso a matsayin ~angare wanda shi zai samar da kasha 30 cikin ɗari na makin wannan kwas. Yin aikin jinga a tsarin karatu wajibi ne. Tsallakewa ko cin kwas ga ɗalibi ba zai yiwu ba, sai ya kasance ya yi aikin jinga. Rashin yin aikin jinga a kwas yana iya kawo cikas ga tsallake jarabawa ko da kuwa ɗalibi ya cinye kaso 70 na makin jarabawa. Don haka, yana da kyau ɗalibai su kula da wannan, a yi ƙoƙarin yin duk wata jinga da malami zai bayar.

**Jarrabawar {arshen Darasi (End of Course Examination)**

Kowane kwas da ake yin darasinsa, ana yi masa jarabawa a ƙarshen zangon jaratu. Burin malami a ƙarshen wannan jarabawa shi ne dalibansa su amsa tambayoyin da aka umarce su domin samun damar tsallake wannan kwas. Tsallake kwas ga ɗalibai alama ce da ken una an fahinci darasi. A wasu lokutan, rashin tsallakewar yana nuna akwai yiwuwar ɗalibai bas u fahinci darussan wannan kwas yadda ya kamata ba. Don haka, ƙarshen zangon karatu hanya ce wadda ake yin awon fahimtar ɗalibai dangane da abin da aka koyar da su. Ta wannan hanya ake fahimtar ko sun gane darasin, ko kuwa wani ~angare kaɗai da suka gane. Wannan wani mizani ne inda malami zai auna fahimtar kowane dalibi dangane da abin da aka karantar da shi. A nan malami zai naƙalci ganewar kowane ɗalibi, da yadda kowa yake fahimtar tambaya. Ta wannan hanya za a bi domin bai wa ɗalibai ƙwarin guiwa na ƙara dagewa da kuma gyara wuraren da suke yin ba daidai ba.

Jarabawar takan kasance ta ɗauki kaso 70 cikin kashi 100 na kwas. Wannan fasali abin da dalibai ba su gane ba game da shi, ana samo tambayoyin ne daga cikin tambayoyin auna fahinta ko jinga. Bisa wannan dalili ake ganin cewa duk wanda ya yi ƙoƙarin naƙalta tare da iya amsa waɗancan tambayyoyi, lokacin da jarrabawa ta zo; zai tunkare ta ba tare da fargaba ba. Abin da ya kamata dalibi ya kula dangane da yadda zai tunkari jarabawar ƙarshen zangon karatu shi ne, tambayoyin da ake yi suna fitowa ne daga cikin darussan da aka koyar a cikin kwas ɗin. Ba a sa ran a ga wani abu wandabai shafi kwas ba.

**MAIN COURSE**

**CONTENTS** **PAGE**


| | | |
|---|---|---|
| **Rukuni Na 1** | **…………………………………….....** | **1** |
| Kashi Na 1 | Mene Ne Adabi?......................................... | 1 |
| Kashi Na 2 | Mene Ne Zube?........................................... | 7 |
| Kashi Na 3 | Ire-Iren Zuben Hausa……………………. | 12 |
| **Rukuni Na 2** | **……………………………………………….** | **20** |
| Kashi Na 1 | Fasalin Zuben Gargajiya……………. | 20 |
| Kashi Na Biyu | Ci Gaban Ire-Iren Zuben Gargajiya…. | 35 |
| **Rukuni Na 3** | **……………………………………………….** | **43** |
| Kashi Na 1 | Bayani Game Da Samuwar Rubutun Zube….. | 43 |
| Kashi Na 2 | Hukumomin Inganta Adabi Da Samuwar Rubutaccen Zube……………………………. | 56 |
| Kashi Na 3 | Rawar Hukumomin Inganta Adabi Wajen…… | 64 |
| Kashi Na 4 | Shekarun 1980 Da Samuwar Sabon Fasalin Rubutu……………………………………….. | 76 |
| **RUKUNI NA 4** | **………………………………………….** | **82** |
| Kashi na 1 | Mene ne Adabin Kasuwar Kano?....................... | 82 |
| Kashi na 2 | Ci gaba da wanzuwar Rubutaccen Zuben Hausa.. | 93 |
| Kashi na 3 | …...………………………………………………… | 104 |
| Kashi na 4 | …………………………………………………….. | 109 |

# RUKUNI NA 1

Kashi Na 1 Mene Ne Adabi?
Kashi Na 2 Mene Ne Zube?
Kashi Na 3 Ire-Iren Zuben Hausa

Hukumar Ƙasa Da Ƙasa Da Samuwar Rubutaccen Zube

## Kashi na 1: Mene Ne Adabi?

### Abin Da Ke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Mene Ne Adabi?
1.3.1 Ma'anar Adabin Hausa A Zahiri
1.3.2 Ma'anar Adabin Hausa A Luggance
1.3.3 Ma'anar Adabin Hausa Daga Bakin Masana
1.4 Kammalawa
1.5 Taƙaitawa
1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

A ,ams (1965) duk ba su zo da ma'anar adabi ba domin a lokacin ba su shiga ciki taskar nazari sosai ba. Amma idan aka dubi Ƙamusun Jami'ar Bayero (2006), za a ga ya bayyana adabi da cewa:

Fannin ilimi ne wanda ya ƙunshi labarai da waƙoƙin baka da rubutattu da wasannin kwaikwayo da al'adu da abubuwan fasaha da na hikima.

Shi kuwa ƙamusun Literary Terms ad Literary Theory na Cuddon (1976) ya bayyanna Literature, wato adabi da cewa:

Kalma ce da ba ta da wata ma'ana ɗaya tsayayya. Sai dai ta fi tafiya da ayyukan da suka shafi waƙa da wasan kwaikwayo da zube da gajerun labarai. A nan ana nufin aikin adabi ya fi wanda ba shi ba, musamman a rubuce armashi da nuna gwaninta wajen amfani da salo da bayanai na burgewa… da kuma sa nishaɗi.

1.3.3 Ma'anar Adabin Hausa Daga Bakin Masana
Daga irin yadda a zahirance da kuma a luggance aka ga ma'anar adabi, shi ya sa masana wannan fage daga cikin masanan Hausa suka kalli adabin ta waɗannan fuskoki. Ga wasu kaɗan daga cikin su.

Farfesa Abdulƙadir ɗangambo a cikin littafinsa Rabe-Raben Adabin Hausa Da Muhimmancinsa wanda aka buga a 1984 ya bayyana adabi kamar haka:

Ma'anar kalmar da Larabci, 'ita ce 'halin ɗa'a, fasaha, ƙwarewa. To amma a Hausa, har ma da Larabcin, wannan kalma, tana nufin abubuwan da suka shafi al'adu da rayuwa da fasaha na al'umma; wani lokaci da kuma nazarinsu. A taƙaice, munna iya cewa, adai, shi ne maudu'i ko hoton rayuwa na al'umma. Wannan ya ƙunshi yadda al'adunsu, ɗabi'unsu, harshensu, halayyar rayuwarsu, abincinsu, tufarsu, makwacinsu, hulɗoɗinsu, tunaninsu, da ra'ayoyinsu da sauran abubuwan da suka shafi dabarun zaman duniya don ci gaba da rayuwa; kai har ma da abubuwan da suka shafi mutuwa.'

Daga abin da muka gani za mu iya cewa, ba wani abu ba ne adabi face waɗannnan ayyuka da al'umma ke gudanarwa da suke ɗauke da al'adu da halaye da ɗabi'u da nishaɗi, kumasuke kasancewa tamkar madubi ko hoto na kallon rayuwar al'ummar tun daga haihuwa har zuwa mutuwa.

Auna Fahimta
Bayyana abin da ka fahimta dangane ma'anar waɗannan abubuwa da ke biye?

1. Adabi a zahirin tunanin Hausawa
2. Me ƙamusun Hausa na Bayero ya ce game da ma'anar adabi?
3. Me HOTO da MADUBI ke nuni game da ma'aar adabi a Hausa?

## 1.4 Kammalawa

A wannan darasi mun kawo bayani ne game da adabin Hausa da yadda ake gane ma'anarsa ta zahiri da ta lugga da kuma ta bakin masana adabin na Hausa. An yi haka domin ka fahimci gundarin abin da ke jan ragamar tunanin masana game da matsayin waƙa da zube da wasan kwaikwayo da wasu batutuwa irin su.



## 1.5 Taƙaitawa

A wannan darasin ana fatar ka fahimci:

- Mene ne adabi?
- Da yadda Hausawa da masana ke kallon adabi, wato ko dai a matsayin baƙuwar kalma ko 'yar gida.
- Da kuma yadda ma'anar adabin take a cikin littattafai na lugga da kuma daga bakunan wasu masana adabin Hausa.

Jinga

1. Ashe kalmar adabi ba ta Hausawa ba ce? Tattauna
2. Kawo maánar adabi kamar yadda ɗangambo (1984) ya bayyana.
3. Me ya bambanta ma’anar adabin Hausa a luggance da kuma r a’ayoyin masana Hausa?

A zahirance adabi ya shafi wata gwaninta da Hausawa ke yi ta amfani da sarrafaffun zantuka don nuna iyawa ko gwaninta ko kuma isar da saƙo.

## 1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan {Arin Nazari


bambadiya.blogspot.com

www.rumbunilimi.com.ng

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language, London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory, Oxford: Penguin Books

Magaji, A. (1982); ‘Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa.’ Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Yahaya, I.Y. (1988); Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa. Zariya: NNPC

Malumfashi, I. (2009); Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Ashe kalmar adabi ba ta Hausawa ba ce? Tattauna

Kalma ta ADABI ba Bahaushiyar kalma ba ce. Ke nan Kalmar baƙuwa ce wadda Hausawa suka aro daga Larabawa, bayan cuɗanya da juna tun da daɗewa. Tushen kalmar dai shi ne ADAB, Hausawa ne suka yi mata kwaskwarima daga baya ta ƙara mata wasalin (i) ta koma ADABI, domin ta dace da yanayin ginuwar kalmomin Hausa.

2 Kawo ma'anar adabi kamar yadda ɗangambo (1984) ya bayyana.

A fahimtar ɗangambo (1984) adabi ba wani abu ba ne face, ca abubuwan da suka shafi al'adu da rayuwa da fasaha na al'umma; wani lokaci da kuma nazarinsu. A taƙaice, muna iya cewa, adabi shi ne maudu'i ko hoton rayuwa na al'umma. Wannan ya ƙunshi yadda al'adunsu, ɗabi'unsu, harshensu, halayyar rayuwarsu, abincinsu, tufarsu, makwacinsu, hulɗoɗinsu, tunaninsu, da ra'ayoyinsu da sauran abubuwan da suka shafi dabarun zaman duniya don ci gaba da rayuwa; kai har ma da abubuwan da suka shafi mutuwa.'

3 Me ya bambanta ma'anar adabin Hausa a luggance da kuma ra'ayoyin masana Hausa?

A luggace adabi fannin ilimi ne wanda ya ƙunshi labarai da waƙoƙin baka da rubutattu da wasannin kwaikwayo da al'adu da abubuwan fasaha da na hikima. A fannin masana kuwa adabi na nufin ayyuka da al'umma ke gudanarwa da suke ɗauke da al'adu da halaye da ɗabi'u da nishaɗi, kumasuke kasancewa tamkar madubi ko hoto na kallon rayuwar al'ummar tun daga haihuwa har zuwa mutuwa.

## Kashi Na 2 Mene Ne Zube?

### Abin Da Ke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Mene Ne Zube?
 2.3.1 Ma'anar Zuben Hausa A Zahiri
 2.3.2 Ma'anar Zuben Hausa A Luggance
 2.3.3 Ma'anar Zuben Hausa Daga Bakin Masana
2.4 Kammalawa
2.5 Taƙaitawa
2.6 Muhimman Wasu Kalmomi
2.7 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa

A darasin farko, wanda ya kasance tamkar shimfiɗa ce ta gane mene ne adabin Hausa domin ya yi mana jagora kafin mu shiga tattauna ainihin batun da muka sa gaba, wato zuben Hausa da rarrabe-rarrabensa. Mun dai gane yadda Hausawa suka ɗauki adabin nnasu a wancan darasin. Yanzu kuma a wannan ga~ar za mu tattauna me ake son ka sani game da zuben Hausa.

A nan za a ƙoƙarta gabatar da zube a Hausa da ma'anarsa shi ma ta fuska uku kamar yadda muka yi game da adabi. Wato mu san ma'anar zube a zahirance da ma'anarsa ta lugga da kuma abin da masana zuben suka fasalta mana shi.

Kawo wannan yanayi zai taimaka wajen fahimtar yadda za a iya bambanta zube da 'yan uwansa irin su waƙa da wasan kwaikwayo. Daga nan kuma sai a gane ire-irensa, wato na gargajiya da na zamani. A tuna, shi wannan bayani game da zube shi ne zai iya ba mu damar fahimtar inda darasin zai fuskanta baki ɗaya. Idan har ba mu san zube ba, to kuwa da wuya mu fahimci sauran sassa da suka gina darasin baki ɗaya. Saboda haka, sanin ma'anar zube da irin hanyoyin da ake bi a gane zube da ire-irensa da kuma yadda ya sauya kamannnu a tsawon rayuwar Hausawa, abu ne mai fa'ida da alfanu.

## 2.2 Manufar Darasi

Babbar manufar wannan darasi ita ce a fahimci abubuwa da suka haɗa da:

- Ma’anar zube a tsakanin Hausawa
- Ma’anar zube a zahiri
- Ma’anar zube a lugga
- Ma’anar zube a adabance

## 2.3 Mene Ne Zube?

Kalmar zube kamar yadda za mu gani nan gaba kaɗan tana da fuskoki mabambanta, amma a wannan darasin an ajiye ta ne a matsayin aikin adabi. A bisa wannan mizani ne za mu dubi lamarin. Abin da ke da muhimmanci dai shi ne, zube ba baƙuwar kalma ba ce a Hausa, tun asali Hausawa sun san da ita, suna kuma amfani da ita ko kafin zuwan ilimi da sani irin na adabi ko boko.

Sai dai kamar yadda a kowane harshe na duniya ake da irin wannan fasali na adabi, zube na nufin mabambantan abubuwa ga kowace al’umma, ba dole sai ta adabi ba. Sai dai abin da aka fi amincewa da shi shi ne, dukkan zancen da mutane ke yi a rayuwa shi ne ake wa laƙabi da zube, wato zance sakaka. Sai dai ba kowane zance ne, kamar yadda za mu gani yake iya zama zube na cikin adabi ba.

A wannan darasin za mu dubi yadda Hausawa suka ɗauki zube a zahiri da lugga da kuma ta albarkacin bakunan masana wannan fage, domin a ga yadda fasalin yake.

### 2.3.1 Ma’anar Zuben Hausa A Zahiri

Zube kalma ce ta Hausa da ke da fuskoki guda biyu, da farko akwai fuskar nahawu, sa’annan akwai fuskar zahiri. Bari mu soma bayani da ma’anar tukuna kafin mu dubi ta Zahiri.

Idan muka koma cikin harshen Hausa za mu ga cewa kalmar zube tana da matsayi a cikin harshen a nahawun Hausa Zube na cikin rukunin aikatau na Hausa. Kalmar tana kuma cikin abin da ake kira ta tushe ko asali. Akwai ajin aikatau guda bakwai, huɗu su ne na asali, sauran ukun su ne waɗanda aka tsamo daga tushen asalin. Alal misali.

1. Zubaa
2. Zuba
3. Zubi
4. Zube
5. Zubar
6. Zubo
7. Zubu

Kowane rukuni na aikatau za a ga cewa yana da aikin da yake yi. Ajin aikatau na huɗu inda 'zube' ya faɗo shi ne ke nuna an gama aikin, ba saura da ya rage. Ke nan kalmar 'zube' a ~angaren aiki take, ba suna ko bayanau ba.

A zahirance kuwa zube na nufin abu ne a watse ko wanda bai da wani tsari ko dokoki da ke tafiyar da shi. Alal misali, za aji Hausawa na cewa abu 'kara a zube', wanda yana nufin yadda karan da ake zance ke warwatse ba tare da wani shiri ko tsari ba a lokacin da aka watsar da shi. Wannan yana nuna cewa an gama aikin, kamar yadda muka gani a baya. Ke nan zube na iya nufin duk wani abu da aka yi shi ko aka tsara shi ba bisa bin wasu ƙa'idoji ko tsari ba.

Kamar yadda Cuddon (1976) ya ce, asalin kalmar 'zube' a Ingilishi, wato 'prose' daga Latin ta keto, wato 'prosa' zancen da ke tafiya warwatse ko rubutun da ke zuwa a barbaje. Ya ƙara da cewa ba wani abu ne 'prose' ba sai harshe ko magana da ba sa ɗauke da kwalliya, wanda shi ya bambanta shi da 'waƙa' ko 'wasan kwaikwayo' da ke ɗauke da salo da burgewa. Idan kuma aka sami zube mai ɗauke da fasalin waƙa to shi ne ake kira da waƙaƙƙen zube, wato 'poetic prose.'

### 2.3.2 Ma'anar Zuben Hausa A Luggance

Ita kuwa ma'anar 'zube' a luggance ana iya ganin ta a cikin ƙamus-ƙamus ne da kuma wasu littattafai na ke~a~~un kalmomi. Alal misali, ga abin da ƙamus ɗin Bargery ke cewa game da kalmar, wato ko dai watsar da abu ko kuma riƙe linzami a lokacin tafiya da doki ko zama a ƙasa a ƙofar gida ko zubewar ciki ko mantuwar karatu ko inda tsuntsaye ke haɗuwa ko tattaruwa ko na tsaga ko kuma aikatau da ake samu daga zuba.

Ga kuma abin da ƙamus na Jami'ar Bayero ya ce game da zube, wato kalma ce mai bayyana bazuwar abu da yawa a wuri, ko kuma zurarewar abu ko tsiyayewarsa ƙasa daga cikin wani mazubi ko kuma rushewa ko faɗuwa ko kuma gungun tsuntsaye da suka sauka a ƙasa ko kuma tsage mai yawa da tsawo a fuska.

Daga abin da muka gani za mu iya cewa zube ko 'prose fiction' wani nau'in rubutu ne da Cuddon (1976) ya kira da 'ƙagaggen labari" ko 'ayyanannen labari,' wato abin da aka tsara a ka aka fitar da shi ta fatar baki, kuma abin ba gaskiya ba ne. Kodayake wannan ma'ana ma na iya faɗawa ga waƙa da wasan kwaikwayo, tun da su ma "ƙaga' su ake yi, amma shi 'fiction' ɗin ya fi zama a gidan labari.

### 2.3.3 Ma'anar Zuben Hausa Daga Bakin Masana

A adabance kuwa, zube na nufin guntattakan jawabai ko bayanai da ke zuwa kara zube ba tare da wasu dokoki ko ƙa'idoji ba, sa'annan ana yin su ne domin a sa nishaɗi ko jin daɗi ga mutane. A nan ana iya bambanta zube da waƙa da wasan kwaiwayo ta fuskar adabi, wato ana iya cewa a waƙa da wasan kwaikwayon sai an tsara, an kuma shirya, sa'annan kuma a daidaita tunani kafin a aiwatar da su, shi kuwa a zube ba a buƙatar waɗannan abubuwa.

Ke nan zube na na nufin abubuwa irin su tatsuniya da karin magana da tarihi da tarihihi da kirari da **zambo** da almara da ƙissa da ƙarangiya ko salon magana ko baƙar magana. *********

A nan bari mu bi masana adabin Hausa mu ji me suka ce game da zube a Hausa. ɗangambo (1984) yana cewa bisa jimla, rubutun zube shi ne duk wani rubutu ko wallafa da ba ta waƙa ba ce ko kuma ba wasan kwaikwayon ba ne….ya haɗa da ƙagaggun labarai da rubutun tarihi da rubuce-rubucen siyasa da kimiyya da harhi kan fannoni.

Shi kuwa Malumfashi (2009) cewa ya yi:

A zahirance zube na nufin abu ne a watse ko wanda bai da wani tsari ko dokoki da ke tafiyar da shi, alal misali kara a zube, na nufin yadda karan ke warwatse ba tare da wani shiri ko tsari ba. Ke nan zube na iya nufin duk wani abu da aka yi shi ko aka tsara shi ba bisa bin wasu ƙa'idoji ko tsari ba.

**Auna Fahimta**

- Me ake nufi da zuben Hausa a zahirin magana?
- Ya {amusun Bayero ya bayyana ma'anar zuben a Hausa?
- Yaya ma'anar zube take daga bakin masana?

### 2.4 Kammalawa

A wannan sashe an yi ƙoƙari ne wajen bayyana ma'anar zube ta fuskoki uku; wato zube a zahirance da kuma zube a luggance, sa'annan aka rufe

da bayyana ma'anar zube daga bakin masana adabin Hausa. An yi haka ne domin a yi shimfiɗa game da darasin baki ɗaya.

## 2.5 Taƙaitawa

A wannan darasin ana fatar a fahimci:

- Mene ne zube?
- Yaya zube yake a tsakanin Hausawa kafin zuwan baƙi?
- Yaya ma'anar zube take daga littattafan lugga da sauran bayanai?
- Yaya masana adabin Hausa suka ƙalailaice zube da kuma misalai.

## 2.6 Jinga

1. Yaya mace mai sayar da tuwo a bakin titi za ta bayyana zube a zahirance? Tattauna.
2. Me {amus na Bargery ko na Bayero suka ce game da zube a Hausa?
3 Me Malumfashi (2009) ya bayyaa game da zuben Hausa?

## 2.7 Manazarta Da Wasu Ayyukan {Arin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language, London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory, Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari), Zaria: Amana Publishers

Gusau, S. M. (1995). Dabarun Nazarin Hausa. Kaduna: Fisbas Media Services

Magaji, A. (1982); 'Tasirin Adabin Baka A Kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa.' Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2002). "Adabi da Bidiyon Kasuwar Kano a

Bisa Faifai: Taƙaitaccen Tsokaci". Maƙalar da aka gabatar a Cibiyar Hausa, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sokoto.

Malumfashi, I. (2009); Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd.

Umar, M.B. (1985). Dangantakar Adabin Baka Da Al'adun Hausawa. Kano: Shaguna Commercial Press

Umar, M. B. (1987). Dangantakar Adabin Baka Da Al'adun Gargajiya. Kano: Triumph Publishers

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa**.** Zariya**:** NNPC

bambadiya.blogspot.com
www.rumbunilimi.com.ng

## 2.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Yaya mace mai sayar da tuwo a bakin titi za ta bayyana zube a zahirance? Tattauna.

   Mace mai sayar da tuwo a bakin titi za ta xauki Kalmar zube a matsayin wani abu da yake kara zube ko a watse ko wanda bai da wani tsari ko dokoki da ke tafiyar da shi.

2. Me {amus na Bargery ko na Bayero suka ce game da zube a Hausa?

A ƙamus na Jami'ar Bayero zube kalma ce mai bayyana bazuwar abu da yawa a wuri, ko kuma zurarewar abu ko tsiyayewarsa ƙasa daga cikin wani mazubi ko kuma rushewa ko faɗuwa ko kuma gungun tsuntsaye da suka sauka a ƙasa ko kuma tsage mai yawa da tsawo a fuska.

3. Me Malumfashi (2009) ya bayyana game da zuben Hausa?

Malumfashi (2009) ya ce "A zahirance zube na nufin abu ne a watse ko wanda bai da wani tsari ko dokoki da ke tafiyar da shi, alal misali kara a zube, na nufin yadda karan ke warwatse ba tare da wani shiri ko tsari ba. Ke nan zube na iya nufin duk wani abu da aka yi shi ko aka tsara shi ba bisa bin wasu ƙa'idoji ko tsari ba."

## Kashi Na 3 Ire-Iren Zuben Hausa

**Abin Da Ke Ciki**

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Ire-Iren Zuben Hausa
  3.3.1.1 Zube Na Gargajiya
  3.3.1.2 Zube Na Zamani
3.3.2 Dangantakar Zuben Gargajiya Da Na Zamani
3.4 Kammalawa
3.5 Taƙaitawa
3.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan {arin Nazari
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa

A wannan darasin za ka fahimci abubuwa guda uku da suka shafi ire-iren zuben Hausa, wanda aka rarraba zuwa na gargajiya da na zamani, sa'annan aka zo maka da dangantakar da ke tsakaninsu, musamman ta irin yadda suke wa juna shigar giza-gizai daga zamunnan baya zuwa yau.

A cikin wannan darasi za a bayyana maka me ake nufi da gargajiya da kuma zamani, da yadda gargajiyar da kuma zamanin suka bambanta saboda irin yadda suka wanzu a cikin tarihi.

Idan har ka fahimci wannan rarrabuwa muna fatar ka kuma natsu ka gane yadda zuben gargajiya yake, musamman ganin cewa shi ne za a fara nazarta nan gaba kaɗan. Sa'anan kuma ka ga ya aka yi zuben ya bar kai, ya koma cikin takarda. Saboda haka, sanin ma'anar zube da ire-irensa a tsawon zamanin da Hausawa suka ratso, abu ne mai fa'ida da muhimmanci.

### 3.2 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce ka fahimci abubuwa muhimmai game da ire-iren zuben Hausa da suka haɗa da:

- Ire-iren zuben Hausa
- Mene ne gargajiya?
- Yaya zuben gargajiya yake?

- Mene ne zamani?
- Ya ake gane zube na zamani?
- Wace irin dangantaka ke tsakanin zuben gargajiya da na zamani?

## 3.1 Abin Da Ke Cikin Darasin

### 3.3.1 Zube Na Gargajiya

Kafin mu bayyana maka me ake nufi da zube na gargajiya ya dace ka san me ake nufi da gargajiya tukunna. Kamar yadda aka faɗa a farkon darasi, shi zuben gargajiya yana daga cikin sashen adabin gargajiya na Hausawa, saboda haka in ana maganar gargajiya ana nuni ne ga dukkan rayuwa da ta wanzu kafin zuwan baƙi a ƙasar Hausa Idan kuma ana maganar baƙi, to ana iya kasa su zuwa gida biyu, baƙi na kusa da kuma na nesa. Baƙi na kusa su ne waɗanda suke zagaye da Hausawa a matysayin maƙwabta, irin su Fulani da Nupawa da Gwarawa da Buzaye da Kanuri da Yarbawa. To amma da yake su waɗannan maƙwabta ba su yi tasiri kai tsaye ta fuskar rubutu ga Hausawa ba, ya sa ake kallon su da tasirinsu a matsayin na gargajiya ba na zamani ba.

Su kuwa baƙi na nesa, su ne waɗanda suka taso daga ƙasashensu masu nisa, ko kuma saboda bulaguro da Hausawa suka yi zuwa sassan da suke, ya sa suka yi tasiri a kan Hausawan ta fuskoki da dama. Ta fuskar adabi da al'adu cuɗanyar ba ta sa gargajiyar Hausawa ta canza ba sai da aka shigo da rubutu, to a nan ne ake cewa an samar da zamananci a ciki.

Saboda haka za ka iya cewa, ba wani abu ba ne gargajiya face yanayin rayuwa da Hausawa suka sami kansu kafin haɗuwa da baƙin nan kala biyu da muka ambata, na nesa da na kusa. Saboda haka, zube na gargajiya shi ne dukkan wani ~angare na adabin gargajiya da ba waƙa ko wasan kwaikwayo ba, wanda kamar yadda ɗangambo (1984) ya nuna yana cikin 'adabin da Hausawa suka gada daga kaka da kakanni', yana ƙunshe cikin rayuwar yau da kullum, amma wanda tushensa yake tasowa daga kakanni. Babbar hanyar da ake bi a gane shi ita ce, ana shirya shi a ƙwaƙwalwa ne, a kuma aiwatar da shi ta fatar baki. Ire-iren waɗannan zube na gargajiya sun haɗa da:

Tatsuniya
Karin Magana
Take da Kirari
Baƙar Magana
Zambo*******
Habaici********

Tarihi Da Tarihihi
Zambo-Zagi
{arangiya/Zaurance

### 3.3.1.2Zube Na Zamani

A nan ma kafin mu bayyana maka zube na zamani sai mun fasalta maka me ake nufi da zamani. Kamar yadda muka ga gargajiya a baya, ana iya cewa zamani akasin gargajiya ne. Ke nan shi ne ayyukkan zube da suka samu ko wanzu bayan zuwan baƙi ƙasar Hausa. A nan muna magana bisa baƙin nan na nesa ban a kusa ba kamar yadda muka nuna a baya, wato Girkawa ko Larabawa ko Turawa.

Me ya sa zuben Hausa da ya gwamutsu da baƙi daga nesa ake ce da shi na zamani? Ba wani abu ya sa haka ba sai don ganin cewa shi wannan zube ya canza fasali daga ka da baki zuwa takarda, wato rubutu. Rubutun nan da ya canza zuben Hausa zuwa na zamani ya zo wa Hausawa ta fuskiki da dama:

1. Zuben Hausa da ya samu lokacin da gwamutsuwa da Girkanci
2. Zuben Hausa wanda ya samu ta hanyar rubutun Larabci
3. Zuben Hausa wanda aka gani cikin rubutun ajami
4. Zuben Hausa wanda ya zo cikin siffar Ingilishi
5. Sai Zube na ƙarshe wanda aka samu cikin Hausar boko

Dukkan waɗannan hanyoyin rubutun sun taimaka wajen zamanantar da zuben Hausa, in ban da rubutun Girkawa da ba a samu ganin sa a Zahiri ba. Saboda haka, dukkan zuben da aka samu gani a cikin Larabci da Ajami da kuma cikin Ingilishi da Hausar Boko, shi ne wanda ake kira da zuben zamani, musamman in ya ƙunshi zube na gargajiya da aka tsara da shiryawa a ƙwaƙwalwa, kamar tatsuniya da karin magana da kirari da ******zambo**** da habaici****** da makamantan su. Ke nan zuben zamani ya ƙunshi abubuwa guda biyu, wanda yake ƙunshe da zamanin da baƙi suka shigo ƙasar Hausa da kuma wanda rubutun da baƙi suka shigo da shi ya yi masa riga da kwalliya, ko dai ta hanyar Larabci da Ajami ko kuma ta Ingilishi da Boko.

### 3.3.2 Dangantakar Zuben Gargajiya Da Na Zamani

Abin ƙara lura game da zuben Hausawa shi ne irin dangantakar da ke tsakanin zuben na gargajiya da na zamani, musamman da yake sun zo a mabambantan lokuta ko zamunni. Ba wani abu ya kawo wannan dangantaka ba face yadda aka samar da zuben tun daga farkon assasa shi. Shi zube na gargajiya ka fahimce shi ne bisa ma'anarsa ta cewa ana shirya shi a ka ne a kuma furta ko a ayyana shi ta baki, shi ya ake kiran wannan zube wata rana da zuben ka ko zuben baka, shi kuma ɗin ne ke

canza kama ya koma zuben zamani ko rubutacce. Bisa wannan tunani ne za a gane yadda dangantakar take a fili. Alal misali, idan ka ɗauki tatsuniya ko karin magana waɗanda cikinsu ko ƙunshiyarsu babu ruhin baƙi a ciki kuma ba a rubuta su ba, su ne za a danganta da gargajiya tsantsa, misali, karin irin wannan magana su ne:

"Duk Dodo ɗaya ake yi wa tsafi"
Wannan tana daga cikin karin maganar da za a kira da ta gargajiya, amma daga lokacin da ta koma Hausawa na cewa:

"Duk Allah ɗaya ake bauta wa"
A nan kuma ruhin Musulunci ya shigo a rayuwar Hausawa, saboda haka sai mu ce, karin maganar ta zama ta gargajiya, mai ruhin zamanin Musulunci. A lokacin da kuma karin maganar ta koma kamar haka:

"Duk Naira yanzu ake bauta wa"

Za mu iya cewa wannan ta koma ta gargajiya, amma mai ruhin zuwan zamanin Turawa, har ma fiye, domin Naira sai a 1975 aka samar da ita.

Yanzu kuma za a ji ana cewa:

"Duk waya ake bauta wa"

Ma'ana, zamanin ya tarar da yau, inda wayar take tashe, wanda ya ƙara tabbatar mana cewa zuben ne dai ke canza launi, amma yana nan yadda yake tun asali na ka da ƙwaƙwalwa ana furtawa ta fatar baki, sai dai zamanin kurum da ya canza.

A kuma lokacin da aka rubuce irin wannan karin magana ko cikin Larabci ko Ajami ko Ingilishi ko Boko to wannan zube ya tashi daga na gargajiya ya koma na zamani, kuma a rubutacce. Wannan ne ya sa ake cewa ana samun shigar giza-gizai tsakanin zuben gargajiya da na zamani, kamar yadda za mu gani a cikin sauran kashe-kashen wannan darasi.

**Auna Fahimta**

Me aka fahimta game da waɗannan abubuwa da ke biye?

1. Gargajiyar Hausawa
2. Yaya zuben Hausawa yake kafin zuwan baƙi?
3. Mene ne zamani a tunanin Hausawa?
4. Ya zuben zamanin Hausawa yake a zahiri?
5. Kawo misalign yadda zuben gargajiya ke komawa na zamani.

## 3.4 Kammalawa

Wannan darasi kamar yadda ƙunshiyarsa ta nuna, an aza tubalinsa ne domin ka fahimci ire-iren zuben Hausawa. Wato zuben gargajiya da na zamani, da kuma yadda za ka iya fasalta su. Ma'ana, yadda za ka iya gane na ka da wanda ake furtawa ta baki da kuma wanda ake shiryawa a ka a fitar da shi ta hanyar rubutu. An kuma ƙoƙarta nuna inda suke haɗuwa da rabuwa da juna, ta hanyar kawo misalai.

## 3.5 Taƙaitawa

Darasin da ya gabata ana so ne ya gabatar maka da abubuwa da suka haɗa da:

- Ire-iren zuben Hausawa?
- Yadda Hausawa suka rarraba zube zuwa gida biyu, na gargajiya da zamani.
- Da kuma yadda na gargajiya ya koma na zamani ta hanyar rubuta shi.
- Daga ƙarshe kuma shigar giza-gizai da gargajiya da zamani ke yi wa juna.

**Jingar Aiki**

1. Gargajiyar Hausawa ita ce wadda ba ta da haɗi da baƙuwar al'umma. Tattauna.
2. Zamani a wajen Hausawa na nufin lokacin da aka haɗu da baƙi. An yarda? Tattauna.
3. Ta yaya zuben gargajiya ke canza riga ya koma cikin ta zamani? Tattauna

## 3.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language, London: Hodder & Stoughton

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory, Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari), Zaria: Amana Publishers

Gusau, S. M. (1995). Dabarun Nazarin Hausa. Kaduna: Fisbas Media Services.

Magaji, A. (1982); “Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa”. Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2002). “Adabi da Bidiyon Kasuwar Kano a Bisa Faifai: Taƙaitaccen Tsokaci”. Maƙalar da aka gabatar a Cibiyar Hausa, Jami’ar Usmanu ɗanfodiyo, Sokoto.

Malumfashi, I. (2009); Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service

Umar, M.B. (1985). Dangantakar Adabin Baka Da Al’adun Hausawa. Kano: Shaguna Commercial Press.

Umar, M. B. (1987). Dangantakar Adabin Baka Da Al’adun Gargajiya. Kano: Triumph Publishers.

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa. Zariya: NNPC

bambadiya.blogspot.com

www.rumbunilimi.com.ng

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Gargajiyar Hausawa

Gargajiyar Hausawa na nuni ne ga dukkan rayuwa da ta wanzu kafin zuwan baƙi na kusa da nesa ƙasar Hausa. Wannan na nufin dukkan wani abu da Hausawa suka gada daga kaka da kakanni', wato tushensa yake tasowa daga kakanni.

2. Yaya zuben Hausawa yake kafin zuwan baƙi?

Kafin zuwan baqi, zuben Hausawa shi ne na gargajiya kuma ana shirya shi a ƙwaƙwalwa ne, a kuma aiwatar da shi ta fatar baki. Ire-iren waɗannan zube na gargajiya sun haɗa da: Tatsuniya, Karin Magana, Take da Kirari, Baƙar Magana, Zambo, Habaici, Tarihi Da Tarihihi, Zambo-Zagi da {arangiya/Zaurance

3. Mene ne zamani a tunanin Hausawa?

Zamani a wajen Hausawa na nufin lokacin da aka haɗu da baƙi.

4. Ya zuben zamanin Hausawa yake a zahiri?

Zamani akasin gargajiya ne. Ke nan shi ne ayyukkan zube da suka samu ko wanzu bayan zuwan baƙi ƙasar Hausa. A nan muna magana bisa baƙin nan na nesa ban a kusa ba kamar yadda muka nuna a baya, wato Girkawa ko Larabawa ko Turawa. Kuma shi wannan zube ya canza fasali daga ka da baki zuwa takarda, wato rubutu.

5. Kawo misalin yadda zuben gargajiya ke canza riga ya koma cikin ta zamani? Tattauna

Misali Karin maganar "Duk Dodo ɗaya ake yi wa tsafi"
Wannan tana daga cikin karin maganar da za a kira da ta gargajiya, amma daga lokacin da ta koma Hausawa na cewa:

"Duk Allah ɗaya ake bauta wa"
A nan kuma ruhin Musulunci ya shigo a rayuwar Hausawa, saboda haka sai mu ce, karin maganar ta zama ta gargajiya, mai ruhin zamanin Musulunci. A lokacin da kuma karin maganar ta koma kamar haka:

"Duk Naira yanzu ake bauta wa"

Za mu iya cewa wannan ta koma ta gargajiya, amma mai ruhin zuwan zamanin Turawa, har ma fiye, domin Naira sai a 1975 aka samar da ita.

Yanzu kuma za a ji ana cewa:

"Duk waya ake bauta wa"

# RUKUNI NA 2

Kashi Na 1 Fasalin Zuben Gargajiya
Kashi Na Biyu Ci Gaban Ire-Iren Zuben Gargajiya

## Kashi Na 1 Fasalin Zuben Gargajiya

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Fasalin Zuben Gargajiya
1.3.1 Na Hausawa Zalla
1.3.1.1Tatsuniya
1.3.1.2Karin Magana
1.3.1.3Baƙar Magana
1.3.1.4Take Da Kirari
1.3.1.5{arangiya
1.3.1.6Habaici*********
1.4 Kammalawa
1.5 Taƙaitawa
Jingar Aiki
1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

Wannan darasi ci gaba ne daga inda na baya ya tsaya. Idan ka so kana iya cewa ƙoƙarin fayyace wannan fage na zuben gargajiya ne da kyau. Abin da aka saba bai wuce yin cikakken bayani kan zuben gargajiya ba, domin a fiddo shi yadda yake, musamman wanda muka kira da na Hausawa tsantsa, wato wanda bai gauraye da baƙi, na kusa ko na nesa.
An yi haka ne domin ka iya bambantawa tsakanin zube, na gargajiya tsantsa da kuma wanda za a gani can gaba wanda aka kira da zube mai surki. A nan ne kuma za a ~arje gumi game da wannan irin zube ta hanyar fasalta shi da kyau. Da yake abin da yawa, an za~i wasu daga ciki ne domin misaltawa.



### 1.2 Manufar Darasi

Manufar wannan kashi daga cikin fasalin wannan darasi shi ne a yi wa zuben Hausa na gargajiya fiɗar da za a iya gane shi idan an gan shi, ta hanyar ɗaukar sa ɗaya bayan ɗaya a farfasa su ta hanyar ma'anarsu da zubi da tsarinsu tare da kawo misalansu

## 1.3 Fasalin Zuben Gargajiya

Domin daidaita tunani, a wannan hauji na kashin darasin, za a bi mataki na yin filla-filla game da wasu za~a~~un zuben Hausawa na gargajiya da ake iya kira da na Hausawa tsantsa. Za a fayyace su ne domin ka iya bambanta su daban da waɗanda suke gwamatse da shigowar zamani.

### 1.3.1 Na Hausawa Zalla

Idan muka ce zuben Hausawa zalla a nan, muna magana ne a kan irin adabin bakan nan na Hausawa da ake ayyanawa ba tare da bin wasu ƙa'idoji na a-zo-a-gani-ba, cikin su kuwa akwai tatsuniya da kirari da baƙar magana *******da zambo da habaici******* da wasu irin su da dama. Bari mu ɗauki wasu daga cikin waɗannan domin mu ga yadda fasalinsu ya kasance.

#### 1.3.1.1Tatsuniya

Tatsuniya tana ɗaya daga cikin zuben Hausa na gargajiya da za mu kira zuben Hausa tsantsa, musamman ganin cewa tana tare da al'ummar Hausawa tun tale-tale. Ba inda aka samu Labarin cewa an ga tatsuniya a matsayin baƙuwar kalma ko dai daga Larabawa ko Turawa, don haka 'yar ƙasa ce. Ida nana son fayyace ma'anar tatsuniya to sai an yi la'akari da cewa Hausawa da dama sun amince ita ce makarantar farko ta 'ya'yan Hausawa. Ke nan daɗaɗɗiyar al'ada ce tsakanin Hausawa, wadda kuma mata, musamman tsofaffi da amare ne suka fi yin ta. Wannan ya nuna mana cewa an fara wannan tada tun da al'ummar Hausawa suka fara aure da haihuwa da kafuwar iyali. Ba kuma wani abu Hausawa ke kira da tatsuniya ba face wasu ƙananan zantuka masu sa nishaɗi da ake gabatarwa don ɗebe kewa da faɗakarwa da ilmantarwa.

Idan kuwa muka dubi ma'anar tatsuniya a luggance, za mu ga ta zo da ma'anoni mabambanta, alal misali, Bargery (1934) ya zo da kalmomi biyu masu kama da juna da ya kira 'Tatsuniya da Gatana', duk da bai fayyace yadda ma'anar take ba, tun da kwatance ne ya yi da Ingilishi, inda ya kira Tatsuniya da 'a fable' ko kuma 'riddle, ita kuma 'Gatana' ya ce 'a fable', wadda aka samo daga buɗewar bayar da labarin da ake wa yara, wato 'ga ta nan, ga ta nanku'. Shi kuwa Muhammad (1990) a littafin Hausa Metalanguage ya kira Tatsuniya da Folktale ne, wato abin da ya shafi labarai na gargajiya da sukaƙ unshi gizo da ƙoƙi da dabbobi da tsirrai da makamantansu. Shi kuwa {amusun Jami'ar Bayero ya yi nuni ne da cewa labari ne da ake ba wa yara na hikima don hira.

Idan muka koma ga masana adabi kuwa, za mu ga kowane da irin yadda ya kalli ma'anar Tatsuniya, alal misali Umar (1978) ya ce, tatsuniya ita

ce labaran nan da aka “shirya game da gizo ko waninsa da ya ƙunshi wani darasi ko ya cimma wata manufa ta musamman cikin hikima.”

Saboda haka za mu iya cewa, tatsuniya ta daɗe tsakanin Hausawa, sa’annan mata ne, musamman amare da tsofaffi ke yin ta, wata sa’a kuma yara na yi tsakaninsu domin nishaɗi da annashuwa. An fara tatsuniya ne tun lokacin da Hausawa suka fara aure da hayayyafa, kuma babban burinta bai wuce ta ilimantar, ta karantar, ta kuma nishaɗantar ba.

Idan aka koma kan saƙon da ke tattare a cikin tatsuniya kuwa, za a ga cewa suna tafiya ne bisa irin tafarkin da aka gina tatsuniyar. Ma’ana, abin da masu yin tatsuniyar suka tanada ga masu sauraro. Alal misali, tatsuniyar Ruwan Bagaja ko ta ‘Yar Mowa da ‘yar Bora, waɗanda ke ɗauke da nuni ga ƙin nuna wariya da son kai a tsakanin iyali. Ita kuwa tatsuniyar Takitse, tana nuni ne ga rashin alfanun danniya da cin zalin talakawa. Idan kuma aka dubi tatsuniyar ɗanmusa tana koya wa masu sauraro muhimmancin kunya da kawaici da dai misalan irin waɗannan.

Daga ƙarshe akwai abubuwa masu muhimmanci da ya kamata a sani game da tatsuniya waɗanda Gusau (2000) ya bayyana, da suka haɗa da masu yin tatsuniyar waɗanda ya kasa gida biyu; amare don ɗebe masu kewa da kuma tsofaffi, domin taya su hira da rage musu aikin ~arar gyaɗa ko gyaran zare da ire-iren sana’o’insu na gargajiya. Lokacin yin tatsuniya kuwa bai wuce dare ba ko kuma wajen da yara ke wasa. Haka nan akwai buɗewa da rufe tatsuniya da sauran matakai irin waɗannan da dama.

### 1.3.1.2Karin Magana

Kafin mu shiga cikin fagen sanin karin maganar Hausa, ya dace mu fahimci kalmomin nan biyu da suka gina zancen, wato kari da kuma magana. Shi dai kari na nufi wani ~angare ko rabi ko karyayye ko kuma rababbe. Ita kuwa magana na nufin zance ko furuci ko kalami da mutum kan yi domin a fahimci abin da ke cikin zuciyarsa. Ke nan idan muka dubi batun a yadda yake a zube, za mu ce ba wani abu ba ne karin magana ba face zancen da aka yi wa gi~i ko aka karya shi ko raba shi ko kuma aka kawo wani ~angare aka yi watsi da wani ~angaren.

Sai dai bisa tunanin masana, suna ganin cewa za a iya bayyana karin magana da wata gajerar magana wadda ke ɗauke da dogayen ko kuma ~oyayyen bayani ko zance a cikinta. Wasu masanan kuwa suna ganin karin magana da cewa Hausa ce aka dunƙule a waje ɗaya wato zance ne dogo a dunƙule wuri ɗaya, wato taƙaitacce.

Saboda haka muna iya cewa, za a iya rarraba karin maganar Hausa zuwa sassa biyu wato sashen farko da kuma sashe na biyu mai bayani game da sashen farkon. Alal misali ‘Zuciya da ƙuna da kaza ta kwana kan dami’. Sashe na farko shi ne “Zuciya na ƙuna…., sashe na biyu shi ne mai bayyana abin da zuciyar ta ji, wato da kaza ta tashi da safe ta gan ta kan dami. Ke nan muna iya cewa siffar farko ta karin magana ita ce ta zo da ~angare biyu, domin kuwa yawancin karin maganganun Hausa ~angare biyu gare su.

Bayan wannan siffar kuma ana iya sake rarraba karin maganar Hausa zuwa irin ‘yan kalmomin da ke maƙale a jikinsu, alal misali akwai masu ɗauke da:

- Inji: Allah suturi buƙui inji kishiyar mai doro.
- An Ce: In gani a ƙasa, an ce da kare ana biki a gidansu.
- Sai: Sai bango ya tsage ƙadangare ke samun wurin shiga.
- Daga: Daga ƙin gaskiya, sai ~ata.
- Ko: Ko a Kwara, mai arziki yana sayar da ruwa.******
- Dole: Dole zama da ɗuwawu.
- Har: Cin danƙo har da su kaza.
- Ta: Ta malam, ba ta wuce amin ba.

Baya ga wannan kuma, ana iya sake rarraba karin magana zuwa ga karin magana ta kai tsaye da kuma mai labari. Wato duk wadda take haka nan ba wani labari a cikin ta ita ce ta kai tsaye, ita kuma wadda sai an fasa ta a samu cikakken bayani, ita ce mai labari. Misali:

- Cin ƙanzon kurege
- Kamun gafiyar |aidu
- Gobarar Titi
- Buɗin bakin Baba
- Cin ƙwallon Ndah

Ko ba komai, karin magana ta kasance wani babban rukuni na adabin baka, wadda galibi da ka ake shirya ta a kuma aiwatar da ita da ka a kuma adana da ka. Haka kuma irin gudunmawar da take bayarwa a cikin harshe ba ƙarama ba ce, musamman wajen nuna armashinta da watsuwarta.

Dangane da abubuwan da ke faruwa na yau da kullum kuwa, an fi yawan samun karin magana a bakin mata da kuma rukunin waɗansu jama’a dangane da yanayin sana’arsu da kuma hulɗarsu. Wannan shi ya sa gwargwadon kasancewar al’umma, gwargwadon kasancewar harshenta da kuma amfani da karin maganganu.

Zamantowar karin magana a rubuce bai samu ba sai bayan da ilmi da wayewar kai suka ƙara samuwa a ƙasar Hausa. Misali, kafin zuwan Turawa a ƙasar Hausa, akwai shaidar wanzuwar rubutaccen adabi cikin ajami wanda ya haɗa da karin Magana. Da. Turawa suka zo ci gaba kawai aka yi ta hanyar mayar da su cikin rubutun boko.

Daga ƙarshe muna iya karkasa yawancin karin maganganun da muke da su bisa irin fannin da suke bayani kai. Alal misali, akwai na:

- Fanin siyasa da sha'anin mulki:

Da dama sarki bisa jaki
Sarkin yawa ya fi sarkin ƙarfi
Babba juji ne
Tambari sai sarki

- Fannin addinin gargajiya

Duk bori/dodo ɗaya ake wa tsafi.
An huta, bori ya kashe boka
Maye bai fidda maitarsa a fili
Tsafi gaskiyar mai shi

- Fannin kasuwanci

Kasuwa ta mutum biyu ce, idan ka ga na uku ~arawo
Da rashin tayi akan bar arha
Daga ganin sarkin fawa, sai miya tai zaƙi

- Fannin rayuwar aure

Arha, aure bashi
{irmisisi, tusa gaban miji
Mai kar~a, surukin mai kyauta

- Fannin zamantakewa

Kowa da kiwon da ya kar~e shi, maƙwabcin mai akuya ya sayi kura
Sauna ke gane ɗan banza
ɗan uwa rabin rayuwa/jiki

- Fannin sana'a

Na-duƙe tsohon ciniki
Sana'a goma maganin takaici
Kakarsa ta yanke saƙa
Ko ɗan riƙo ya san kifinsa

- Fannin nishaɗi

Baki ya fi son ana motsa shi
Gemu ba ya hana wasa

### 1.3.1.3Baƙar Magana

Daga kalmomin biyu da suka gina wannan batu, 'Baƙa" da 'Magana' za mu fahimci cewa baƙa na magana ne bisa abin da yake mai duhu ko mai ~ata rai ko makamancin haka. Ita kuwa magana tana nufin zance ko furuci. Ke nan idan Bahaushe ya ce magana baƙa ce yana nufin zance ne da ke tayar da rai ko muzguna masa.

A adabin bakan Bahaushe idan ana batun baƙar magana ana danganta ta da kutare ko kuma mahauta. Ana ganin kutare suna jefa baƙar magana ne saboda irin yanayin da suka samu kansu na rashin yatsun hannaye da na ƙafafuwa. Wannan yanayin ne ya sa sai abu kaɗan ya ~ata masu rai har su kai ga jefa baƙar magana. Wannan kuma shi ya sa yawancin baƙar maganar tasu kan faɗa ne ga Maiduka, wato Allah, wanda a nasu tunanin kamar bai yi musu adalci ba da ya yi su kutare.

Haka ya sa yawancin labaran da suke da alaƙa da kutare za ka ga ba kawai baƙin zance ba ne kawai, zancen ne mai kama da sa~o, saboda yadda ake jefa zancen ga Maiduka, domin fito da halin ni'ya'su da suke ciki.

Shi kuwa mahauci ana cewa yana yin baƙar magana ne saboda yanayin da ya sami kan sa na fitar da rai kowace safiya. Wasu masana na ganin cewa yadda yake ta'allaƙe da cire rai na dabbobin da yake hulɗa da su dole ne mahauci ya kasance cikin baƙin ciki da ~acin rai. Shi ya sa idan mutane suka gaya masa zancen da bai yi masa daɗi ba shi ma yake jefa musu mara daɗi, domin kuwa wanda ya kasance tamkar Azara'ilu ga dabbobi ba abin da ba zai iya faɗa wa wanda bai yi masa mai daɗi ba. Misalan baƙar maganar kutare tana da yawa, wasu daga ciki sun shafi batutuwa da dama da suka haɗa da:

"Wai wani kuturu ne ya iske ana wa'azin turmi, mai wa'azi na cewa ai shi Allah shi ke yin yadda ya so, kuma yana iya gyara kowane irin lamari. Kuturun na jin haka, sai ya kira mai wa'azin ya ce da shi, 'malam har da wannan, Allah na iya gyarawa?' yana magana yana ɗaga dungulmin yatsansa sama domin mutane da mai wa'azi su gani."

Haka kuma, "wai wani kuturu ne ya tafi bara ya yini bai samo komi ba, ga shi kuma an yi ruwan sama ya yi masa dukan tsiya. yana zuwa ƙofar gidansa sai ya ga yara suna wasan ƙasa, sun gina gidan ƙasa, suna cewa, 'ɗakin Allah kar ka rushe,' sai kuturun ya sauko daga kan jaki ya sa

dungulminsa cikin ɗakin da yara suka yi da yashi, yana cewa, 'rushe shi, rushe shi, shi ma ya kwana waje.'

Su kuwa mahauta baƙar maganar tasu ta fi fitowa fili ne dangane da sana'arsu. Alal misali, "wani mahauci ne yake sayar da nama, sai wani ya zo ya dubi tsiren da ke gaban wuta ya ce da shi, ashe ma dai namanka naka ɗanye ne. Wannan ya ~ata wa mahaucin rai, sai ya kada baki ya ce da shi, 'ɗɗɗɗ, kauce kada ta buge ka', wato wai da ran saniyar yake gasa ta."

Saboda haka za mu iya cewa, baƙar magana tana da nata mazauni a cikin rayuwar zuben Hausawa, musamman ganin cewa ta bi tafarkin zuben gargajiya na Hausawa da bai da alamun gaskiya a ciki, domin abin da aka tsara ba wai ana nufin haka ba ne, shi ya sa Hausawa ke cewa, "baƙar magana ba zagi ce ba, amma ta ɗara zagi zafi."

**1.3.1.4Take Da Kirari**

Take da kirari tamkar 'yan uwan juna ne, domin kuwa tare suke tafiya. Sai dai take shi ne tamkar Hassan, shi kuwa kirari ya kasance Hussaini, ko kuma mu ce abokan wasan juna ne. Shi take ya samu ne daga kalmar takawa, wato a yaba ka ko ƙwarzanta ko zuga ka, da zai sa ka jirga ko ka taka saboda ka ji daɗin abin nan da ka ji ko saurara, Malumfashi (2013).

Shi ma kamar sauran sassan adabin bakan Hausawa muna iya cewa take abu ne da ya shafi kiɗa da waƙa. Galibi waƙar baka da ta zo da kiɗa to buɗinta shi ne take. Shi ya sa masana ke cewa 'take wani guntun amo ko zance ne na share fage wataƙila kafin kirari ya iso'. Yana zuwa ne a salon kiɗa ko busa ko wanin waɗannan wanda akan fassara cikin magana. Haka kuma take na iya zama wani ~angare na ƙoƙarin yabo ko kushewa ga abubuwan da jama'a suka sa gaba na ra'in kansu wanda shi yake haifar da take da kirari.

Akan yi wa maza tuni da wani kakansu jarumi ko wanda ya yi fice kan wata sana'a ta wannan fasali. Muna iya cewa, ke nan take wata shimfiɗa ce ta amfani da harshe wajen tayar da tsikar jikin mutum, kuma abin da zai biyo a kan wannan shimfiɗar shi ne kirari, kuma take bai cika tsawo ba.

Alal misali, farauta na ɗaya daga cikin sana'o'in farko na Bahaushe, don haka ga al'ada kafin fara farauta kiɗa ake yi domin sanar da jama'a cewa za a fita. Galibi wannan kiɗan yakan zo a matsayin taken wani ɗan farauta. Jin kiɗan yakan sanya wanda aka kaɗa masa takensa ya tsimu kuma abokan adawarsa na gida da waje su ma su ɗimauta da niyyar idan aka tafi daji za a yi yadda za a yi. {addarta a yi nasarar kama wani nama, abin da zai biyo baya shi ne kuwwa da kirari kafin a ~arke da faɗa.

Saboda haka za a samu cewa, take na zuwa ne da fasalin kiɗa ko busa ko gogawa ko makamantan haka. Da yake take ba zance ko furuci ne ba yana zuwa da amo ne. Da zarar aka yi wa mutum take tana yiwuwa ya ~uge da yin kirari.

Shi kuma kirari yana ɗaya daga cikin rukunin adabin bakan Bahaushe da ya gada tun kaka da kakanni, don haka ba wata al'umma da za ta yi iƙirarin cewa ita ta koya wa Bahaushe hikimar aiwatar da kirari. Masana adabin Hausa sun ba da ma'anar kirari gwargwadon fahimtarsu, dangane da yadda ya shafi al'amurran Hausawa da kuma yadda su suka cuɗanya da shi. Bargery (1934) ya bayar da ma'anar kirari a ƙamus ɗinsa da cewa waɗansu maganganu ne da ake yi wa sarakuna ko muhimman mutane da suke bayyana halayensu da kuma kamanninsu ta hanyar kambamawa.

Wasu masanan na ganin kirari da cewa, wani abu ne wanda ya yi kama da yabo, haka kuma a duk lokacin da ɗanma'abba yake rera shi za ka ji kamar waƙa, ko kuma wani irin jawabi ne aunanne da ake faɗa da baka. Haka ma masu wasanni, kamar mafarauta ko 'yan dambe ko 'yan kokawa suna yi kirari. Ana iya cewa, kirari irin wasa da kalmomin hikima ne ko kalmomin cicci~awa da aka yi wa wani mutum don a kambama shi ko wani abu don a fito da kyawonsa da armashinsa ga idon jama'a.

Saboda haka, muna iya cewa ba inda Bahaushe bai ajiye kirari a rayuwarsa ba. Miji na yi wa matarsa uwargida ko amarya. Mata na iya yi wa ɗanta, ɗan fari ko ɗan auta. Ana iya yi wa basarake ko talaka da dai makamantansu. Alal misali:

'Amarsu ta ango, ba kya laifi ko da kin kashe ɗan masu gida.'

Haka ma Hausawa na yi wa kishi kirari da cewa, 'kishi asalin kissa, mafarin mutuwa, mai kai mutum ga ramin halaka.'

Su kuma 'yan farauta na yin kirari mai kamar haka :

Ayye hoho! Ihu…,
Sai ni kahiri na Amadu danja,
Dije na gida tana aza sanwa,
In ratsa daji in kuma ratsa,
In tai da gyauge da geza,
Yaro na gani kwaɗai na ci nai,
Yaro ba mutum ba sai an girma.

Ana kuma iya yi wa mutum kirari kamar haka:

Gamji ɗan ƙwarai,
Naira yayinki a kai ko'ina…,
Gamzaki mai fita da subahi,
Zaki mai ƙashi guda…,
Giwa kin wuce kaho…,
|auna sanuwar sake ….

Babbar hikimar da ke tattare a nan ita ce, amfani da harshe wajen yabo da ƙoƙarin cire wa kai ƙaiƙayin damuwa da kasalar zuci. Har ila yau, ga nuna gwaninta ta harshe wajen ƙoƙarin jera kalmomi da zantuttuka makusanta da nisantar juna a wuri ɗaya. Wannan ba ƙaramin al'amari ba ne, kuma har kwanan gobe abin tinƙaho ne a cikin sha'anin rayuwa. Dubi a cikin tawai ko renon yara yadda mata kan yi kirari ga ɗansu da cewa:

ɗan fari gilashi,
Sai na goya na kuma tarye,
Nuhuna Nuhu,
Nuhu ɗan Buhari.

**1.3.1.5{arangiya**********

{arangiya wani na'uin rayuwa ne da ke wanzuwa wanda mutum kan yi domin ya burge. A nan ya shafi kalami ne ko furuci da wani kan yi domin nuna gwaninta. (Malumfashi,2013). Ke nan muna iya cewa, salon magana kalamai ne na hikima da kakkarya harshe ko kuma yin magana mai sarƙiya. Irin wannan shi ne masu nazari ke kira ƙarangiya, kuma ana yin ta ne ta hanyar wasa da harshe don nuna gwaninta. Ba kasafai kalmomin da aka yi amfani da su a cikin salon magana ke ba da cikakken bayani idan aka ware su a matsayin ɗaiɗaiku ba, sai dai cike suke da ba da nishaɗi da kuma raha.

Akan yi salon magana ko ƙarangiya a lokacin da yara suka ƙare kalaci, sukan taru a wurin wasa suna faɗi-banza-faɗi-wofi, yayin da wasu a ƙofar ɗakin wata tsohuwa (wataƙila kaka) ko amarya ana hira ana taɗi har a kai ga salon magana, Malumfashi (2013). Misali kamar a ce:

JAGORA: Wa zai faɗa da sauri?

ɗan tsuntsu tsurullu,
Ka bar tsurta zawo inda baba
Ka tsurta sallah (sau da yawa)

Ko

Tulin tutun burgu
Tulin kuyya baba (sau da yawa)

Ko

Shamuwa masha ruwa wuya miƙe (sau da yawa)
Wani salon maganar ko ƙarangiya kuma sai a cikin kiɗa da waƙa yake fitowa wajen da mawaƙa ke amfani da wannan dabarar domin ƙara wa waƙarsu armashi. Sa'idu Faru ya kawo salon magana cikin waƙarsa da yake yi wa sarkin yaƙin Banga, inda yake cewa:

Yaro in taƙamar salon magana kaka yi ce tsare tsara, tsari tsattsarin tsattsara ka tsantsame tsari tsaf ga tsamiya.

Tunkuɗa tunku cikin tukar ruku ~u
Tukuɗin Tumba yai tu~us!
Tumba taho yau da ke da ta~o da ta~us da 'yat tu~us.

Wasu masanan na kiran salon magana da gagari-gwari, wato zance da ke wahalar da Gwarawa ko waɗanda ba su ji Hausa sosai ba faɗa. Alal misali:

{ato ya yo ƙoto, kwaɗo ya yo ƙoto, {ato ne zai ƙwace ƙoton kwaɗo, ko kuwa kwaɗo ne zai ƙwace wa ƙato ƙoto? {ato ƙwace ƙoton kwaɗo.

A irin wannan hali, ba Gwari ba, ko Bahaushen da ƙyar zai sha babu kuskure. Idan ana wannan za ka tarar kowa ya himmatu, kuma ana ƙoƙari a ga dai an kai labari, abin gwanin sha'awa.

Wasu masanan na ganin cewa, salon magana hanya ce ta amfani da za~a~~un kalmomi masu kama da juna a cakuɗa su, su ba da wani sabon kari da tsari a cikin harshe, Malumfashi (2013). Don haka, salon magana ya kasance wata dabara ta samar da kariya ga wannan harshen da al'ummar da ke amfani da shi.

**1.3.1.6Habaici******************

Ginuwar adabin baka a cikin habaici ta faru ne tun lokacin da abu biyu ko fiye suka nuna ƙaunarsu a kan abu ɗaya. Wato bisa al'ada da kuma halayya irin ta ɗan Adam ba koyaushe ne yake son ya yi tarayya da wani kan abin da shi yake ƙauna ba. Saboda haka, idan ana maganar habaici koyaushe yana faɗawa ne ga abubuwa biyu makusanta.

Na farko, masana da dama sun bayyana cewa an fi samun habaici a tsakanin mata waɗanda suke kishiyoyi ne, ke nan a tsakanin mata aka fi samun yawan habaici da karin Magana. Habaici tsoro ne kuma yakan zo da siffar takala da kuma ramuwa a fakaice, Malumfashi, (2013). Ko ba kome, habaici tare yake da arashi da ke nuna shakku ko razana ta mai magana zuwa ga wanda yake yi wa maganar. Misali a tsakanin mata kishiyoyi na cikin gida akan ji kalamai kamar:

As kaza mai yawan tsince-tsince.
Tir! Da mujiyar ga mai fitar dare.

Sanin kowa ne aikin kaza tsince-tsince ne, amma saboda wata manufa za a sawo sabuwar kaza idan can da babu ita don kawai a rinƙa fashe takaici. Alal misali, a can da zamanin da ake harajin mai unguwa da aka matsa wa wani mutum, tilas ya biya haraji. Da zufan goshi, mutumin nan ya je ya samo kuɗin haraji ya kawo wa sarki. Bayan ya miƙa, sai ya kada baki ya ce "to ranka shi daɗe babu kare bin damo… Malumfashi, (2013) Abin nufi a nan shi ne, mutum na amfani da salon habaici domin fashe haushinsa a gurin da ƙarfi ba ya tsamo shi. Akwai irin wannan dabara da yawa a cikin zuben gargajiya ta hanyar amfani da harshe a yi yabo ko suka ko nuna fushi ko yarda ko kuma ƙi da har abin yakan sanya a yi zagi ko da kuwa a fakaice ne. Misali:

Wanda ya gani shi ka faɗa.
{etar gwaiwa ta ci mai ita.
Mai maɗi ke tallar zaƙi, mai zuma gida aka isko shi.
Su wane dai /su wance dai.
Ba ruwan arziki da mugun gashi….
Yabanya Allah fisshe ki fari.
Na gaba yai gaba, na baya sai labari.
Gani nan, bari nan.
Hassada ga mai rabo taki.
Giwa a garin wasu ~era.
Mai son ɗan ƙwarai, ya auri isassa.

Kowane daga cikin waɗannan zantuttuka da sauran makamantansu na da dalili da muhalli da kuma yanayi da ke sa a aiwatar da shi. Sai dai kamar yadda muka sani yawancin habaici na ƙoƙarin fitar da kamannu ko siffofin wanda ake yi wa shi ta yadda za a iya ganewa kai tsaye. ********

Auna Fahimta

Me aka fahimta game da waɗannan abubuwa da ke ƙasa?

1. Zuben a gargajiyar Hausawa.

2. Yaya za a iya rarraba Karin Magana a Hausa?
3. Yi taƙaitaccen bayani game da tatsuniya da take da kirari a zuben Hausawa?
4. Su wa aka fi alanqantawa da baqar magana a aládar Hausawa?
5. Me ake nufi da qarangiya?

## 1.4 Kammalawa

Wannan darasi kamar yadda ƙunshiyarsa ta nuna, an aza tubalinsa ne domin ka fahimci ire-iren zuben Hausawa, wato zuben gargajiya da na zamani. Sai dai ya fi mayar da hankali ne kan fahimtar fasalin zuben gargajiya na Hausawa zalla kacokam da suka haɗa da irin su tatsuniya da take da kirari da karin mgana da habaici **********da sauran su.

## 1.5 Taƙaitawa

Darasin da ya gabata an so ne ya gabatar mana da abubuwa da suka haɗa da:

- Ma'anar zuben gargajiya.
- Fasalce-fasalcen zuben gargajiya.
- Sai tattauna batutuwan da suka shafi tatsuniya da kirari da karin magana da take da sauran irin su.

## 1.6 Jingar Aiki

1. Yaya zuben gargajiya yake a Hausa? Tattauna.
2. Su wa ke gabatar da tatsuniya a ƙasar Hausa? Tattauna.
3. Kawo taƙaitaccen bayani game da biyu daga cikin zuben gargajiya da aka yi nazari.

## 1.7 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language. London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory, Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari). Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce, Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982). "Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa". Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009). Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa**.** Zariya: NNPC

bambadiya.blogspot.com
www.rumbunilimi.com.ng

## 1.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Zube a gargajiyar Hausawa.

Wannan na nufin zuben Hausawa zalla, wato irin adabin bakan nan na Hausawa da ake ayyanawa ba tare da bin wasu ƙa'idoji na a-zo-a-gani-ba, cikin su kuwa akwai tatsuniya da kirari da baƙar Magana da zambo da habaici da wasu irin su da dama.

2. Yaya za a iya rarraba Karin Magana a Hausa?

Za a iya rarraba karin maganar Hausa zuwa sassa biyu wato sashen farko da kuma sashe na biyu mai bayani game da sashen farkon. Alal misali 'Zuciya da ƙuna da kaza ta kwana kan dami'. Sashe na farko shi ne "Zuciya na ƙuna…., sashe na biyu shi ne mai bayyana abin da zuciyar ta ji, wato da kaza ta tashi da safe ta gan ta kan dami.
Bayan wannan siffar kuma ana iya sake rarraba karin maganar Hausa zuwa irin 'yan kalmomin da ke maƙale a jikinsu, alal misali akwai masu ɗauke da: inji. An ce, Sai, Daga, KO, Dole, Har da sauransu. Ana iya sake rarraba karin magana zuwa ga ta kai tsaye da kuma mai labari. Wato duk wadda take haka nan ba wani labari a cikin ta ita ce ta kai tsaye, ita kuma wadda sai an fasa ta a samu cikakken bayani, ita ce mai labari.

3. Yi taƙaitaccen bayani game da tatsuniya da take da kirari a zuben Hausawa?

Tatsuniya: Tatsuniya tana ɗaya daga cikin zuben Hausa na gargajiya da za mu kira zuben Hausa tsantsa don haka daɗaɗɗiyar al'ada ce tsakanin Hausawa, wadda kuma mata, musamman tsofaffi da amare ne suka fi yin ta. Ba kuma wani abu Hausawa ke kira da tatsuniya ba face wasu ƙananan zantuka masu sa nishaɗi da ake gabatarwa don ɗebe kewa da faɗakarwa da ilmantarwa.

Take da Kirari: Take da kirari tamkar 'yan uwan juna ne, domin kuwa tare suke tafiya. Shi take ya samu ne daga kalmar takawa, wato a yaba ka ko ƙwarzanta ko zuga ka, da zai sa ka jirga ko ka taka saboda ka ji daɗin abin nan da ka ji ko saurara, Malumfashi (2013).

Shi ma kamar sauran sassan adabin bakan Hausawa muna iya cewa take abu ne da ya shafi kiɗa da waƙa. Galibi waƙar baka da ta zo da kiɗa to buɗinta shi ne take. Shi ya sa masana ke cewa 'take wani guntun amo ko zance ne na share fage wataƙila kafin kirari ya iso'. Yana zuwa ne a salon kiɗa ko busa ko wanin waɗannan wanda akan fassara cikin magana. Haka kuma take na iya zama wani ~angare na ƙoƙarin yabo ko

kushewa ga abubuwan da jama’a suka sa gaba na ra’in kansu wanda shi yake haifar da take da kirari.

Da zarar aka yi wa mutum take tana yiwuwa ya ~uge da yin kirari. Shi kuma kirari kamar yadda Bargery (1934) ya bayar da ma’anarsa a ƙamus ɗinsa da cewa waɗansu maganganu ne da ake yi wa sarakuna ko muhimman mutane da suke bayyana halayensu da kuma kamanninsu ta hanyar kambamawa.

4 Su wa aka fi alaqantawa da baqar magana a aládar Hausawa?
Waxanda aka fi alaqantawa da baqar magana su ne, kutare da mahauta. Kutare suna jefa baƙar magana ne saboda irin yanayin da suka samu kansu na rashin yatsun hannaye da na ƙafafuwa. Wannan yanayin ne ya sa sai abu kaɗan ya ~ata masu rai har su kai ga jefa baƙar magana. Wannan kuma shi ya sa yawancin baƙar maganar tasu kan faɗa ne ga Maiduka, wato Allah, wanda a nasu tunanin kamar bai yi musu adalci ba da ya yi su kutare.

Shi kuwa mahauci ana cewa yana yin baƙar magana ne saboda yanayin da ya sami kan sa na fitar da rai kowace safiya. Wasu masana na ganin cewa yadda yake ta’allaƙe da cire rai na dabbobin da yake hulɗa da su dole ne mahauci ya kasance cikin baƙin ciki da ~acin rai. Shi ya sa idan mutane suka gaya masa zancen da bai yi masa daɗi ba shi ma yake jefa musu mara daɗi, domin kuwa wanda ya kasance tamkar Azara’ilu ga dabbobi ba abin da ba zai iya faɗa wa wanda bai yi masa mai daɗi ba.

4. Me ake nufi da qarangiya?

{arangiya wani na’uin rayuwa ne da ke wanzuwa wanda mutum kan yi domin ya burge. A nan ya shafi kalami ne ko furuci da wani kan yi domin nuna gwaninta. (Malumfashi,2013). Ke nan muna iya cewa, salon magana kalamai ne na hikima da kakkarya harshe ko kuma yin magana mai sarƙiya. Ana yin qarangiya ne ta hanyar wasa da harshe don nuna gwaninta. Ba kasafai kalmomin da aka yi amfani da su a cikin salon magana ke ba da cikakken bayani idan aka ware su a matsayin ɗaiɗaiku ba, sai dai cike suke da ba da nishaɗi da kuma.

## Kashi Na Biyu Ci Gaban Ire-Iren Zuben Gargajiya

### Tabbatuwar Rubutun Zube

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Ci Gaban Ire-Iren Zuben Gargajiya
2.3.1 Na Hausawa Bayan Zuwan Larabawa
2.3.1.1 Labari
2.3.1.2 {issa
2.3.1.3 Tarihi
2.3.1.4 Tarihihi
2.4 Kammalawa
2.5 Taƙaitawa
2.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan {arin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 2.1 Gabatarwa

Wannan darasi shi ma ci gaba ne daga inda Kashi Na ɗaya ya tsaya. A nan an yi ƙoƙari ne wajen fayyace ~angaren zuben Hausa na gargajiya kuma an fi bayar da ƙarfi wajen yin cikakken bayani kan zuben gargajiya wanda ya samu gauraya da na zamani wato bayan zuwan Larabawa da Turawa. Ba kamar wancan ba da aka kalli na Hausawa tsantsa, wato wanda bai da gauraye da baƙi, na kusa ko na nesa.

An yi haka ne domin ka iya bambantawa tsakanin tsantsar zube na gargajiya da kuma wanda za a gani a nan mai gauraye ko mai surki. A nan ne kuma aka ~arje gumi game da wannan irin zube ta hanyar fasalta shi da kyau. Da yake abin da yawa an za~i wasu daga ciki ne domin misaltawa.



### 2.2 Manufar Darasi

Manufar wannan kashi kamar na bayansa shi ne a yi wa zuben Hausa na gargajiya fiɗar da za a iya gane shi idan aka gan shi, ta hanyar ɗaukar sa ɗaya bayan ɗaya domin farfasa su ta hanyar ma’anarsu da zubi da tsarinsu da kuma kawo misalansu.

## 2.3 Ci Gaban Ire-Iren Zuben Gargajiya

Kamar yadda aka gani a kashi na farko na wannan darasi a cikin wannan rukuni an baje bayani ne kan zuben Hausa na gargajiya, mai surki da zamani. An yi filla-filla game da wasu za~a~~un zuben Hausawa na gargajiya da ake iya kira da na Hausawa, amma masu surki da zamani. Za a fayyace su ne domin ka iya bambanta su daban da waɗanda suke na Hausawa tsantsa.

### 2.3.1 Na Hausawa Bayan Zuwan Larabawa

Idan muka ce zuben Hausawa bayan zuwan Larabawa ko zamani a nan muna magana ne a kan irin adabin bakan nan na Hausawa da ake ayyanawa ba tare da bin wasu ƙa'idoji na a-zo-a-gani-ba, kuma sun samu ne bayan haɗuwa da baƙi, musamman Larabawa. Cikin irin wannan zuben kuwa akwai irin su Labari da {issa da Tarihi da Tarihihi da wasu irin su da dama. Bari mu ɗauki wasu daga cikin waɗannan domin mu ga yadda fasalinsu ya kasance.

#### 2.3.1.1Labari

Labari abu ne da Hausawa suka daɗe da shi a cikin rayuwa, sai dai bisa ga dukkan alamu ya samu sunansa ne daga lokacin da Larabawa suka shigo ƙasar Hausa, domin kafin zuwansu an fi tu'ammali da tatsuniya a matsayin wani abu makamancin hsaka. Saboda haka za mu iya cewa, an ari kalmar ne daga Larabawa, wato daga 'habar', kamar yadda argery (1934) ya nuna. Hakan shi ya sa ma ake kiran sa da habarce a wani ƙaulin.

Labari na nufin duk wani abu da aka zauna aka kitsa shi ba don ya faru ba, sa'annan aka ayyana shi domin nishaɗantarwa a tsakanin al'umma, ya kuma shafi bayanai kan yaƙi ko fatauci ko soyayya ko tafiye-tafiye ko wani abu makamancin haka. Ida ana son a gane ya labari yake, to sai an koma ga yadda ake tsara da gabatar da shi. Kamar yadda Malumfashi, (2019) ya nuna, dole ne labari ya kasance labartaccen habartacce ne, wato ba wani abu da ya shafi gaskiya ko tarihi ko wata aukuwa a zahiri da mai sauraro ko karatu zai iya gane lagon labarin tun kafin a yi nisa. Duk da cewa wasu masana na ganin ba yadda za a yi labari ya kasance qirqirarre ko qagagge ko fitsararre, wato tunanin da babu irin sa ko kwatankwacinsa ko samfurinsa. Sai dai idan aka tsananta bincike ana cin karo da rayuwa ta zahiri a cikin ginin labari, saboda abubuwan nan guda uku da muka kasafta a baya, wato ji da gani da jini ko gado ko kuma zamantakewa da ke tattare a cikin qwaqwalwar kowane xan Adam.

A tuna, a duk lokacin da labari ya kasance bay a da ruhin labartawa to abubuwa biyu ke faruwa. Na farko zai ginsar da mai sauraro ko karatu, domin da ji ko gani zai gane cewa ya san labarin don haka ba zai ci gaba da saurare ko karatu ba. Idan kuma mai saurare ko karatu ya watsar da labari, to an yi asarar tsarawa da riqewa. Na biyu, duk mai tsara ko karanta labari da ya yi amfani da wani matakin da ba na labartawa ba, zai nuna cewa ba labari yake bayarwa ko rubutawa ba, sai dai qila ko waqa ko wasan kwaikwayo ko makamantan haka, waxanda a ilmance ba kara zube suke zuwa ba, suna da nasu qa'idoji da dokoki, wanda ba a samu a ruhin labari.

Labartawa a nan mataki ne na ganin yadda za a sa mai sauraro ko karatu ya kasance ya aminta da abin da ake faxa ko rubutawa. Wato ya gaskata mai bayar da labarin ko rubuta shi. Duk labarin da bai kasance turke ga mai ba da shi ko rubuta shi ba, ma'ana, mai ba da labarin ko rubutawa ya kasance a wuri xaya yake rawarsa da tsallensa, daga baya ya lula zuwa wasu sassa na ginin, ya kuma sake dawowa inda yake, wato tamkar mai kai gwauro da mari ko yin waxari, yana iya samun naqasu wajen bi da nazari.

Kamar yadda muka sani, a gargajiyance akwai tsarin da Hausawa suka samar wanda da an gani an san labartawa ce ake yi, saboda haka labari ne ake bayarwa ba akasin haka ba. Ke nan siffar abin da ake ji ko sauraro ta labari ce ba tarihi ko tarihihi ko tsagoron gaskiya ba. Ke nan za mu iya cewa, kowane labarin Hausawa akwai alamu da ake bi a gane shi. Alal misali, labari kan zo da buxewa da uwar jikin labarin da kuma rufewa. Ita buxewar labari tana zuwa da siffofin daban-daban, wato ko dai a soma da 'Wata rana'**….** ko 'A wani gari'**….** ko 'Wani Shuxaxxen lokaci'**….** ko wani abu makamancin haka. Daga nan za a biyo da uwar labari, wadda ke qunshe da zallar bayanin qunsiyar labarin. Daga baya sai a qare da marufin da ya dace, ko dai irin su 'Tamat.'ko 'Qurungus' ko 'Qarshe' ko makamancin haka.

**2.3.1.2{issa**

{issa kalma ce da aka samo daga harshen Larabci wadda ta shige tsundum a cikin adabin Hausa. Ita dai wannan kalma tana ɗauke da ma'anoni biyu a cikin harshen Larabci; ma'ana ta lugga da kuma ma'ana ta zahiri. A luggance, ƙissa na nufin bibiya ko ƙididdigewa, wato mutum ya bi diddigin wani abu har ya zuwa ƙarshensa. A ma'ana ta zahiri kuwa, kalmar ƙissa na nufin ba da labarai dangane da mutanen da suka shuɗe, ko kuma ba da labarai a kan waɗansu abubuwa da suka auku a da. Ko kuma wani labari da ke kara zube da ya ƙunshi shiryarwa zuwa ga addini ko gaskiya ko neman tsira kan wani abu. A ra'ayin masana da dama sun yi nuni da cewa, an fi danganta ma'ana da manufar ƙissa a kan labarun da suka danganci addini kawai. Watau bayanai a kan rayuwar

annabawa da sahabbai da waliyyai da sauran su. Duk da haka, akwai wasu labarai na ƙayatarwa da jawo hankali da za a iya kiran su da ƙissa, kamar irin ƙissoshin da suka shafi soyayya. Bisa ga haka akan ce, ƙissa wata hanya ce ta cusa wata manufa cikin zukatan masu saurare.

Duk da irin wannan hasashe game da ƙissa, ana da fahimtar cewa ta shafi abin da ya bibiyo labarin annabawa kamar yadda ya zo cikin Alƙur'ani mai girma, inda ake da surori da suka bayyana labaran annabawa da aka zayyana a cikin Al'ƙur'ani. Sai dai ita ƙissar da Bahaushe ke bayani ta shafi wadda aka gina ne bisa tunanin Bahaushe, wato ga yadda labarin yake a zahiri amma a ƙara masa wani abu ko dai don daɗin labarin ko kuma domin a ƙara ƙayatar da mai sauraro. Alal misali ƙissar Annabi Yusuf ko ta Annabi Sulaiman ko kuma ta Annabi Nuhu, duk za a same su da ɗan bambanci da waɗanda {ur'ani ya zo da su. Wannan ya sa masana suka raba ƙissar zuwa gida biyu;

i) {issar Cinye Dare: Wadda ta ƙunshi labarai da zantuttukan da mutane suke yi don cinye dare.

ii) {issar Addini: Wannan ta ƙunshi labarai ne da ake tsarawa a kan wani abu da ya auku na addini a lokacin annabawa da sahabbai da waliyyai da shaihunnai da sauran su.

A Hausance ke nan, ƙissa labari ne na gaskiya da aka bayar ko ake bayarwa a kan rayuwar annabawa da sahabbai ko waliyyai ko shaihunnan malamai, ko wasu bayin Allah da sauran su da suka danganci addinin Musulunci, musamman waɗanda Alƙur'ani da Hadisai suka kawo bayaninsu. Hausawa sun sami damar sanin wani labari da ake kira da suna 'ƙissa' bayan cuɗanyarsu da Larabawa, suka kuma samu damar rabauta da addinin Musulunci. Don haka a iya cewa, tasirin addinin Musulunci da karance-karancen da suka danganci tafsirai da hadisai da wa'azi wajen yaɗa addinin Musulunci, su ne suka taimaka wajen samuwar ƙissa ga al'ummar Hausawa.

Masana da dama sun rarraba ƙissa zuwa sassa daban-daban. Daga cikin su akwai Sa'idu Muhammad Gusau wanda ya kasa ƙissa zuwa nau'i huɗu kamar haka:

- {issar Annabawa, wadda ta bayyana rayuwarsu ta haƙiƙa da irin gwagwarmayar da suka sha wajen isar da saƙon Ubangiji (Allah).
- {issar sahabbai da waliyyai da shaihunnai, wadda ke ƙunshe da bayanin rayuwarsu.
- {issar sauran bayin Allah (muminai), wadda take bayyana rayuwar wasu bayin Allah, nagartattu da suka miƙa wuyansu ga addinin Allah.
- {issa kangararru, waɗanda suka bijire wa addinin Allah.

## 2.31.3 Tarihi

Kamar yadda aka sani ita wannan kalma ta tarihi baƙuwar kalma ce da aka aro daga Larabci, wato 'Tarikh', mai nuni ga sanin abin da ya wuce na labarin nahiyoyi ko ƙasashe ko mutane ko abubuwa daban-daban. Duk da cewa tarihi labari ne amma yana da ƙanshin gaskiya a cikin sa. Akwai labaran tarihi da dama da aka sani da suka haɗa da tarihin anabawa ko sarakua ko attajirai ko kuma jarumai, irin su Annabi Muhammadu ko Annabi Isa ko Annabi Irahim ko kuma irin su Sarkin Kano ko Sarkin Goir ko ƙasashen Hausa **********akwai ko aza akwai da jarumai iei su ɗawaire da iri su da dama.

Shi tarihi a lokutta da dama gaskiya ne duk da ba a rasa inda ake saƙala son rai, amma kashi 9 cikin 10 yana tafe da gaskiya ne. Ana samun tarihi ko dai daga bakunan tsofaffi ko kuma dattawa ko wasu ma'aikatan fada da ke tu'ammali da shi ko kuma malaman addii da mayaƙa da masu fatauci da karantarwa.

## 2.3.1.4 Tarihihi

Asalin wannan kalma ta tarihihi an samo ta ne daga kalmar tarihi ta hanyar liƙa wa kalmar ɗafa-ƙeya na 'hi', sai ta koma 'tarihihi'. Sai dai abin kula a nan shi ne, tarihi dai yana nufin wani labari na haƙiƙa da ya ta~a faruwa a cikin al'umma. To, amma shi tarihihi za a iya cewa, wani labari ne na wasu abubuwa da suka ta~a wakana na haƙiƙa a cikin al'umma, sai dai irin wannan labarin yana cakuɗe da wasu abubuwan da ba a tabbatar da faruwarsu ba. Don haka idan aka ce tarihihi, a taƙaice ana nufin gur~ataccen tarihi, wanda aka cakuɗa shi a tsakanin gaskiya da ƙarya.

Tarihihi, labari ne da ake riƙe shi da ka, kuma kasancewar kai ba mariƙi ba ne ballantana har ya yi ajiya, sai wajen ruwaito waɗannan abubuwa da suka faru a rayuwa ake gwama su da waɗanda ba su faru ba. Wato dai, yawancin tarihihi ya ƙunshi labarai na kunne ya girmi kaka, waɗanda ba a iya tabbatar da haƙiƙanin aukuwarsu. Tarihihi labarai ne da suka ƙunshi abubuwan da suka danganci rayuwar Hausawa, musamman a jiya.

Akwai tarihihi kala-kala a ƙasar Hausa, sai dai waɗanda suka yi tashe sun haɗa da na taririhin Bayajidda da tarihihin Sarkin Katsina Korau da tarihihin Wali ɗanmarina da Wali ɗan Masani ko wani ~angare na tarihin Shehu Usman ɗanfodiyo ko Bawa Jangwarzo ko ɗanwaire da makamantan su.

**Auna Fahimta**

1. Me ake nufi da {issa?
2. Qissa kasha nawa ta kasu?
3. Me ya bambantaTarihi da Tarihihi?

## 2.4 Kammalawa

Shi kuma wannan darasi ci gaba ne daga inda wancan na bayansa ya tsaya. Wato an dubi yadda zuben gargajiya ya kasance bayan zuwan Larabawa ƙasar Hausa, kamar irin su Labari da {issa da Tarihi da Almara da Tarihihi.

## 2.5 Taƙaitawa

Darasin da ya gabata ne ya gabatar mana da abubuwa da suka haɗa da:

- Bayani game da zuben gargajiya bayan zuwan Larabawa.
- An kuma tattauna yadda wasu daga cikin zuben suka kasance a zahiri, wato irin su labari da ƙissa da tarihi da tarihihi da sauran su.

**Jingar Aiki**

1. Me ya faru da zuben gargajiya bayan zuwan Laraawa? Tattauna.
2. Me ake nufi da tarihi?
3. Me ya bambanta labari da almara?*********

## 2.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language, London: Hodder & Stoughton Ltd.

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory, Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari), Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce, Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982). "Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa." Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009). Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service

Malumfashi, I. (2019); Labarin Hausa A Rubuce: 1927-2018. Zaria: ABU Press

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa. Zariya: NNPC

bambadiya.blogspot.com

www.rumbunilimi.com.ng

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Me ake nufi da {issa?
2. {issa kalma ce da aka samo daga harshen Larabci kuma tana da ma'anoni biyu a cikin harshen Larabci; ma'ana ta lugga da kuma ma'ana ta zahiri. A luggance, ƙissa na nufin bibiya ko ƙididdigewa, wato mutum ya bi diddigin wani abu har ya zuwa ƙarshensa. A ma'ana ta zahiri kuwa, kalmar ƙissa na nufin ba da labarai dangane da mutanen da suka shuɗe, ko kuma waɗansu abubuwa da suka auku a da. Ko kuma wani labari da ke kara zube da ya ƙunshi shiryarwa zuwa ga addini ko gaskiya ko neman tsira kan wani abu. A ra'ayin masana da dama sun yi nuni da cewa, an fi danganta ma'ana da manufar ƙissa a kan labarun da suka danganci addini kawai. Watau bayanai a kan rayuwar annabawa da sahabbai da waliyyai da sauran suQissa kashi nawa ta kasu?

Qissa ta kasu kasha huxu, akwai:

i {issar Annabawa, wadda ta bayyana rayuwarsu ta haƙiƙa da irin gwagwarmayar da suka sha wajen isar da saƙon Ubangiji (Allah).
Ii {issar sahabbai da waliyyai da shaihunnai, wadda ke ƙunshe da bayanin rayuwarsu.
Iii {issar sauran bayin Allah (muminai), wadda take bayyana rayuwar wasu bayin Allah, nagartattu da suka miƙa wuyansu ga addinin Allah.
Iv {issa kangararru, waɗanda suka bijire wa addinin Allah.

3. Mene ne bambanci tsakanin tarihi da tarihihi?

Shi tarihi labara ne da a lokutta da dama gaskiya ne duk da ba a rasa inda ake saƙala son rai, amma kashi 9 cikin 10 yana tafe da gaskiya ne. Shi ma tarihihi labari ne na wasu abubuwa da suka ta~a wakana na haƙiƙa a cikin al'umma, sai dai irin wannan labarin yana cakuɗe da wasu abubuwan da ba a tabbatar da faruwarsu ba. Don haka tarihihi gur~ataccen tarihi ne wanda aka cakuɗa shi a tsakanin gaskiya da ƙarya.

## RUKUNI NA 3

Kashi Na 1 Bayani Game Da Samuwar Rubutun Zube
Kashi Na 2 Hukumomin Inganta Adabi Da Samuwar Rubutaccen Zube
Kashi Na 3 Rawar Hukumomin Inganta Adabi Wajen
Kashi Na 4 Shekarun 1980 Da Samuwar Sabon Fasalin Rubutu

### Kashi Na 1 Bayani Game Da Samuwar Rubutun Zube

**Tabbatuwar Rubutun Zube**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Bayani Game Da Samuwar Rubutun Zube
  1.3.1 Me Larabawa Suka Yi?
  1.3.2 Me Ya Faru Bayan Zuwan Turawa?
  1.3.3 Rubutattun Labaran Hausa Na Farko
1.4 Kammalawa
1.5 Taƙaitawa
1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 1.1 Gabatarwa

Wannan kasha ya qunshi bayani ne game da yadda rubutu ya wanzu a ƙasar Hausa da kuma yadda zuben malam Bahaushe ya canza kama daga kai ya koma takarda ya dace mu san wani abu game da ƙasar Hausa da ma yadda suka samu cuɗanya da baƙin da suka taimaka wajen samar da zuben a takarda.

### 1.2 Manufar Darasi

Manuafar wannan darasi ita ce qoqarin gano yadda rubutun zube ya samu a Hausa.

### 1.3 Bayani Game Da Samuwar Zube A {asar Hausa

Su dai mutanen da ke zaune a ƙasar Hausa sun sami kansu a wannan yanki da daɗewa, suna kuma gudanar da rayuwarsu mani'imciya ta hanyar inganta da kyautata al'adunsu da kuma ɗabi'unsu na yau da kullum. Ana iya ganin gudanuwar rayuwar al'ummar ta hanyar lura da

abubuwa da dama. Da akwai al'amurran da suka shafi zaman tare da yanayin ciyar da kai da hanyoyin gudanar da addini da kuma tattalin arziki. Tattare da su ne da wasu makamantan haka aka gina yanayin rubutun Hausawa, musamman ganin cewa hanyar rubutu ita ce ke ƙara tabbatar da shigar al’umma cikin tsarin waɗanda suka ci gaba.

A kowace irin al'umma ana soma rayuwa ne ba da hanyar rubutu ba haka nan kurum, ana soma gudanar da al’amurra ne da adabin gargajiya ko abin da wasu ke kira adabin baka ko zuben al’umma, wanda ke gudana tattare da yadda al'amurran al'ummar ke wakana. Saboda haka, ana iya cewa tun farkon samuwar al'ummar ƙasar Hausa su ma ba da rubutu suka fara ba da adabinsu na gargajiya ne suka wanzu. Ba a da wata tabbatacciyar shaidar da ta nuna cewa ga lokacin da wannan al'umma ta kafu, ballatana a fahimci yadda adabin al'ummar ya kasasnce a lokacin kafuwa. Ko a tsakanin masana tarihi, an kasa samun matsaya dangane da lokacin da wannan al'umma ta ƙasar Hausa ta kafu. Wasu masana tarihi na ganin cewa kafuwar al'ummar Hausawa ya faru ne saboda ƙafewar da hamadar Sahara ta yi shekaru aru-aru da suka gabata.

Sai dai abin da aka fi dogara da shi dangane da kafuwar al'ummar Hausawa shi ne haɗuwa da jama'a suka yi a wani zamani da ake kira na tsintar 'ya'yan itace da farauta. Daga baya kuma jama'ar suka koma manoma, wasu na zaune a garuruwa, wasu a dokar daji. Lokacin nan ba wata ƙasa ko daula, sai dai zaman rayuwa a tungaye da 'yan'uwantaka da ke gudana a tsakanin wannan gida da wancan, tare da amfani da maigida a matsayin shugaban gida ko kan-gida, kamar yadda Smith (1987:67) ya yi nuni. Wannan shi ya haifar da unguwanni waɗanda suka haɗu suka samar da ƙauyuka, sai dangantakar ta zama ba ta jini kaɗai ba, ta haɗa da sana'a. Su waɗannan ƙauyuka su suka gina garuruwa na ka-zo-na-zo, da bunƙasar gari mai tattare da wasu garuruwan zagaye da shi zuwa birni, har aka sami manyan biranen ƙasar Hausa da masu mulkar su. Wannan zaman tare shi ya haifar da jama'a masu mabambantan sana'o'i, suka sami damar zama waje ɗaya, birane suka ci gaba da kafuwa.

A bisa wannan tsari ne adabin bakan Hausa ya soma ginuwa, aka sami ha~akar zube da waƙoƙi kala-kala; wasu don yabo ko kyautata sana'o'in Hausa kamar  noma, wasu kuma don jin daɗin zaman yau da kullum, kamar da dare a yi tatsuniyoyi ko kuma yara da samari da 'yan mata su yi waƙe-waƙe da raye-raye a dandali da sauran abubuwa masu alaƙa da ayyukan adabi waɗanda ba a rubuce suke ba, domin a wancan lokaci ba wata hanyar rubutu da ta isa ga Hausawa.

Bayan wannan zama irin na ciyar da kai, akwai kuma zama irin na danganta rayuwa da abin bauta, wadda ita ma daɗaɗɗiyar al'ada ce. Masana da dama sun yi nuni da cewa mazauna wannan yanki na ƙasar Hausa a rayuwarsu ta farko ba su da wani addini da ya wuce na

gargajiya, wato bautar gumaka da dodanni. A kowane gida da akwai abin da ake ce wa Kangida. Wasu suna da macizai ko ƙadangaru ko zakaru ko duwatsu ko wata bishiya ko saniya ko kuma uwar-gona. Haka abin yake a unguwanni, inda ake bauta a gindin duwatsu. A Kano akwai wuraren bauta na dutsen Magwan da na Gwauron dutse. A wasu birane kuma akwai bauta irin ta Tsumburbura a dutsen Dala na Kano da ta ɗantalle a Dutsen Wai a Katsina, da kuma bautar Magiro a dutsen Kwatarkwashi, da ke Zamfara.

Dangane da haka za a iya fahimtar cewa, gudanuwar al'ummar Hausa a rayuwarsu ta farko ta danganta ne bisa tsarin neman hanyoyin ciyar da kai da tsarin bauta irin ta maguzanci, waɗanda suka taimaka musu wajen gina adabin bakansu na gargajiya duk kuwa da yake cewa ba wata hanyar rubutu da suke amfani da ita domin adana irin wannan rayuwa.

Yaushe ke nan Hausawa suka sadu da hanyar rubutu irin na zamani? Kafin mu amsa wannan tambaya ya dace mu fahimci cewa, hanyar sadarwa da Hausawa suka saba da ita tun azal hanya ce ta gargajiya da ta ƙunshi alamtarwa da nuni da sassaƙa da ajiye alamu da kaɗe-kaɗe da amfani da muryoyi daban-daban. Saboda haka, muna iya cewa hanyoyin sadarwa na gargajiya su ne suka wadatar ko kafin a mayar da harkoki ga takarda ko makamantantan haka.

Hasashen da aka fi yi shi ne, Hausawa sun fara yin rubutu irin na zamani tun da daɗewa, wasu sun yi nuni da cewa ko kafin rubutun Larabci da Ajami da Boko Hausawa sun yi rubutu irin na Girkanci ko Romanci, domin tunanin wata rijiya da ake da ita a Kano ta Akwa mai nuni da ruwa ko wurin samar da ruwa a wasu harsuna na Romanci ko Girkanci. Wannan bai tabbata ba domin kuwa ba wani rubutu a cikin Romanci da muka gada da zai iya nuna cewa an yi wannan rubutu. Saboda haka, ba wata hanyar rubutun zamani da Hausawa suka sani da ta wuce ta Larabci da Ajami ko kuma Boko. Domin tabbatar da haka muka ga ya dace a bibiyi tarihi domin ganin yadda wannan batu ya wanzu.

### 1.3.1 Me Larabawa Suka Yi?

Kasancewar bautar gargajiya ta sami gindin zama a wasu sassa na ƙasar Hausa har zuwa ƙarni na 14, bai hana addinin Musulunci ya sami kutsa kansa a cikin wannan yanki tun da jimawa ba. Domin haka, ba kamar yadda wasu ke hasashen cewa Musulunci ya shigo ƙasar Hausa a daidai ƙarni na 13 ko na 14 ba, ko da Wangarawa suka zo ƙasar Hausa, har suka iso Kano a zamanin Sarkin Kano Yaji ɗan Tsamiya (1349-1385), sun iske akwai ~ir~ishin addinin Musulunci a wannan nahiya.

Kafin addinin Musulunci ya shigo ƙasar Hausa sai da aka ƙaddamar da shi a nahiyar Hijaz a tsakanin ƙarni na 7 da na 8, sa'annan ya watsu

zuwa sassa daban-daban na duniya, gami da ƙasar Hausa. Daga Gabas ta Tsakiya addinin Musulunci ya ratso zuwa nahiyar Afirka da Turai, musamman sassan Magrib da Andalusiya. Addinin Musulunci ya barbazu a ko'ina, inda sannu a hankali ya zama addinin duniya. Daga Afirka ta Arewa ne Musulunci ya cuso kai zuwa Yammacin Afirka, ta amfani da aƙalla hanyoyi guda biyu muhimmai. Waɗannan hanyoyi sun amfanar ne ta hanyar hada-hadar ciniki da saye da sayarwa. A irin waɗannan tafiye-tafiye ne Musulunci ya biyo 'yan kasuwa zuwa wuraren mazauna Yammacin Afirka. Duk da cewa ba musuluntar da jama'a aka zo yi kai tsaye ba, amma sai da Musulunci ya sami wurin zama a Daular Borno wadda maƙwabciya ce ga ƙasar Hausa.

Wata hanyar kuma da Musulunci ya shigo cikin ƙasar Hausa ita ce ta yankin Daulolin Ghana da Mali na dauri. Bayanai sun nuna cewa, a lokacin da dakarun Al-Murabid suka fatattaka Daular Ghana a shekarar 1076, wanda ya jawo faɗuwar daular, sai aka maye ta da daular Mali. A wani zango na mulkin daular Mali, a zamanin Mansa Musa a 1240, ake jin cewa Musulunci ya bazu a kusan duk faɗin yankin Afirka Ta Yamma, ciki har da yankin da ake kira Nijeriya a yau.

Shigowar Wangarawa daga Mali (Melle) a zamanin Sarkin Kano Yaji (1339-1385) ya sa Musulunci ya ƙara samun gindin zama a ƙasar Hausa. Wangarawa sun sa hannu cikin harkokin gudanar da mulki ka'in da na'in da kuma inganta ayyukan Musulunci ta fuskar Limanci da Ladanci da Alƙalanci da rubuce-rubuce dangane da addini. A wannan lokaci ne aka giggina makarantu da masallatai don bunƙasa Musulunci a wannan yanki, musamman a Kano da Katsina.

*****************A zamanin Sarkin Kano Yakubu (1452-1463), wasu gungun Fulani ɗauke da littattafai suka shigo ƙasar Hausa daga Mali (Melle) ƙarƙashin shugabancin Musa Jokolo, wanda yake kaka ne ga Shehu Mujaddadi ɗanfodiyo. Shigowar waɗannan Fulani ya ƙara wa addinin Musulunci martaba da ɗaukaka a idon jama’a. A wannan lokaci ne aka inganta zuwa aikin Hajji, kuma ƙasar Hausa ta sake jadadada dangantakarta da sauran ƙasashe Musulmi da ke a Gabas ta Tsakiya. Haka abin ya dinga gudana har zamanin zuwan mashahuran malamai masu wa'azi kamar Almaghili.***************

Daga wannan zamani ne Musulunci ya bar fada, ya warwatsu cikin garuruwa da ƙauyuka na ƙasar Hausa. Ta haka ne ko da malamai irin su Almaghili suka ziyarci garuruwan Katsina da Kano, sun iske ilmin addinin Musulunci ya ginu. Abin da kawai suka yi shi ne ƙara rubuta littattafan addini, kamar waɗanda suka danganci sha'anin mulki da shari'a. Sannu a hankali, Musulunci ya zaunu sosai a ƙasar Hausa.

Ke nan ana iya cewa, tun daga ƙarni na goma sha ɗaya (11) zuwa ƙarni na sha bakwai (17) tadojin Hausawa suka cuɗanya da aƙidojin Musulunci. Ta haka ne Hausawa suka fara fahimta da lizimtar halin rayuwa da al'adun Larabawa. Hakan ya sanya suka naƙalci harshen Larabci da yadda ake rubuta shi. Wannan yunƙuri na ƙoƙarin iya karatu da rubutun Larabci da Hausawa suka himmatu a kai ya ba su damar ƙirƙiro wata hanyar rubutu ta kansu da sunan Ajami, wato rubutun Hausa ta amfani da haruffan Larabci. Kodayake ba a sami daidaito dangane da lokacin da Hausawa suka fara rubutun Ajami ba, duk da haka an amince cewa rubutun Ajami ya daɗe a ƙasar Hausa, musamman tun a ƙarni na 14 da na15.

Samar da hanyar rubutun Ajami a ƙasar Hausa ya jawo rubuta adabin Hausa cikin yanayin zube. A ƙarni na goma sha bakwai (17), an sami rubuce-rubuce cikin ajami, kamar littattin Riwayar Annabi Musa, wanda Abdullahi Suka ya wallafa. Bugu da ƙari kuma an samar da waƙoƙi cikin Ajami gwargwadon hali, waɗanda suka haɗa da Shi'irar Hausa da Jumuyyah ta Sheikh Ahmed Tila. Har wa yau, a cikin ƙarni na goma sha bakwai (17) ne aka sami mashahuran waliyan nan guda biyu a Katsina, wato Wali ɗanmarina da Wali ɗanmasani. Duk da cewa waɗannan waliyai sun fi mayar da hankali ne wajen koyar da Musulunci, sun yi rubuce-rubucen waƙoƙin Hausa da dama. An nuna cewa Wali ɗanmarina yana da waƙoƙin Hausa gwargwado.

Haka aka ci gaba da samar tare da wanzar da rubutun Hausa, musamman na waƙoƙi, har zuwa ƙarni na goma sha takwas (18). A daidai wannan lokaci ne malamai, kamar Malam Muhamamdu Al-Katsinawi da Malam Muhammadu Na Birnin Gwari da Malam Shi'ittu ɗan Abdurrra'uf, suka inganta rubuce-rubucen Hausa. Shi Malam Muhammadu Na Birnin Gwari ya wallafa waƙoƙin Hausa cikin Ajami. Shi kuma Malam Shi'ittu, waƙoƙinsa na Larabci da Hausa sun kai ɗari biyu (200), waɗanda suka shahara su ne waƙar Tuba da waƙar Wawiya da Jiddul Azizi da wasu da dama.

Daga wannan lokaci har zuwa ƙarni na goma sha tara (19), lokacin da Shehu Usmanu ya jaddada addinin Musulunci a ƙasar Hausa rubutun Larabci da Ajami ya sami ci gaba da inganta ta hanyoyi mabambanta, musamman ta fannin waƙoƙi da zube. Shugabannin jihadi irin su Shehu Usmanu ɗanfodiyo da ɗansa Muhammadu Bello da ƙanensa Abdullahin Gwandu da 'yarsa Nana Asma'u da autansa Isan Kware da kuma wasu malamai da dama, sun agaza wajen rubuta waƙoƙin Hausa da kuma ayyukan zube. A wancan lokaci na su Shehu Usmanu, ba wai ana rubuta waƙoƙi ne cikin Ajamin Hausa kawai ba, a'a, har da a cikin harshen Fulfulde. Haka kuma an mayar da wasu ayyukan zube na gargajiya cikin Ajami da kuma Larabci.

### 1.3.2 Me Ya Faru Bayan Zuwan Turawa?

Ko da Turawa suka shigo sassan ƙasar Hausa ba su shigo ƙasar a jahilce ba, domin suna da wata masaniya a kan mutanen wurin da kuma yanayin ƙasar. Labaran farko sun je gare su ne daga ayyukan matafiya da suka ratsa ƙasar Hausa, suka wallafa littattafai game da ƙasar da mutanenta. Daga cikin irin waɗannan marubuta da masana akwai Ibn Batuta da kuma Leo Africanus. Shi Leo Africanus a cikin littafinsa na 7 ya bayyana labarin abubuwan da ya gani ko ya ji a lokacin ziyarar da ya kai Afirka. Saboda haka tun a ƙarni na goma sha tara (19) ƙungiyoyi daga jinsin Turawa, sun aiko da masana don su binciki yadda ƙasashen Afirka suke da yadda al'adunsu ke gudana da yanayin harsunansu da kuma addinansu. Sa'annan kuma su bincikio hanyoyin sadarwarsu ta ruwa da ta ƙasa da kuma matakan da suke amfani da su ta fuskar ciniki da saye da sayarwa. Wannan ƙoƙarin sanin yanayi da al’ummar nahiyar Afirka da Turawa suka yi ya kawo kakkafa ƙungiyoyin Turawa masu manufofi daban - daban. A Ingila an samar da Kungiyar Afirka a 1788. Wannan ƙungiya ita ta turo su Mungo Park da Clapperton da Denham da 'yan uwan nan guda biyu wato Landers Brothers, waɗanda suka ziyarci yankunan ƙasar Hausa.

Baya ga waɗannan ƙungiyoyi na neman sanin halayen da ƙasashen Afirka suke ciki, akwai kuma ƙungiyoyin Mishau da Turawa suka turo don bincike, musamman kan al'adu da harsuna da addinan ƙasashen Afirka a tsakanin ƙarni na 18 da na 19. Shahararru daga cikin waɗannan 'yan mishau su ne Barth da Schon. Ta fuskar ayyukan Barth da Schon ne labaran ƙasar Hausa da jama'arta suka isa Turai, kai tsaye. Barth ya wallafa littafi mai ɗauke da bayanan abubuwa da ya ji, ko ya gani a arewaci da tsakiyar Afirka a tsakanin shekarar 1857 zuwa 1859. Ya kuma wallafa wani littafi mai ɗauke da bayanan harsunan Hausa da Fulani da Barebari da Wangala da Bagurma a shekarar 1862. Wanda ya wanzar da rubutun adabin Hausa sosai ta fuskar amfani da haruffan Romanci shi ne J.F. Schon. Ya zo Yammacin Afirka ne a ƙarƙashin ƙungiyar Mishau ta C.M.S, inda a 1832 ya ziyarci Senegal. A tsakanin 1841 har zuwa 1847 ne ya ziyarci ƙasar Hausa da wasu yankunan ƙasar Neja.

Waɗannan yawace-yawace da Schon ya yi sun sa ya iya wasu harsuna da yawa har ya sami ƙwarewa a cikinsu, musamman harsunan wuraren da ya ziyarta. Ta haka ne kuma ya sami damar yin nazari da rubuce-rubuce a kan wasu harsunan, musamman harshen Hausa. Ya wallafa littattafai kan kalmomin Hausa a 1843 da {amus na harshen Hausa a 1876 da littafin karin maganganu da labarai da tatsuniyoyin Hausa a 1886 da kuma littafin Magana Hausa (1885) da wasu da dama da suka shafi addinin Kirista.

Ayyukan da su Schon suka gabatar sun ba da haske wajen samar da wata kafa ta mayar da adabin bakan Hausa a rubuce. Tun kafin a kafa mulkin mallaka a ƙasar Hausa aka mayar da wasu sassan adabin bakan Hausa a rubuce cikin haruffan Romanci. Misalan waɗannan rubuce-rubuce sun ƙunshi tattara labarai da tatsuniyoyi da karin maganganu da sauran maganganun azanci da al'adun Hausawa wuri guda a takarda. Daga shekarar 1891 aka sami littattafai da yawa da suka ƙunshi irin wannan fasali. Daga cikin littattafan da suka yi fice akwai Specimens of Hausa Literature na C.H. Robinson (1896) da kuma Hausa Stories and Riddles na H.C. Harris (1908) da Hausa Sayings and Folklore na Fletcher, R.S (1912) da Littafi na Tatsuniyoyi na Frank Edgar (1924) da sauran su.

Wannan tafarki da Turawa suka bi shi ne ya wanzar da abubuwan amfani dangane da rubutun bokon Hausa. Ta haka aka sami damar zama don kyautata nazari da kuma rarraba sigogin rubuce-rubucen zuwa azuzuwa mabambanta. Shi ya sa ko da Turawa suka mallaki ƙasar Hausa, ayyukan adabi ta fannin tatsuniyoyi da labarai da maganganun azanci sun sami kar~uwa ta amfani da haruffan Romanci. Dangane da haka, ke nan zuwan Turawa ƙara taimakawa ya yi wajen kafa makarantun koyar da nazarin ilmi, inda ta haka ne aka daɗa faɗaɗa hanyoyin wanzar da rubutun Hausa.

A wannan lokaci ba a yi wani tanadi dangane da tsarin da za a bi na kyautata ilmin boko ko kuma yadda za a yi da na Musulunci da aka iske ba. Abin da Turawa suka mayar da hankali a kan sa shi ne, tattaunawa kan batutuwan da suka shafi gudanar da ilmi, ba ƙoƙarin wanzarwa ba sai kuma ɗan abin da ba rasa ba wanda masu aikin Mishan suka yi a Lakwaja da Wusasa ta Zaria kafin tabbatuwar mulkin mallaka.

### 1.3.4 Rubutattun Labaran Hausa Na Farko

Hukumomin inganta adabin Afirka ba su da wata fuska takamaimiya sai wadda gwamnatin mulkin mallaka ta samar a kowace ƙasa da take mulki. Sai dai domin abubuwa su daidaita, an samar da hukumar {asa da {asa Ta Nazarin Harsuna da Al'adun Afirka da {ungiyar Afrika da kuma Mujallar da take bugawa ta Afrika tun daga 1908. Waɗannan hukumomi sun taimaka wajen ɗora harsashin samar da adabin Afirka a cikin boko, musamman na Hausa da aka fara jin ɗuriyarsa tun daga 1929. A wannan shekara ce hukumar {asa da {asa Ta Nazarin Harsuna da Al'adun Afirka ta shirya gasar rubutun Hausa (ƙagagge ko zube).

Tun da farko an tsara gasar ne daga London ƙarƙashin kulawar shugabannin Hukumar Nazarin Harsuna da Al'adun Afrika. Wannan hukuma da haɗin kan hukumomin kula da ilmi na ƙasashen Afirka tun farkon shekarun 1920 suka shirya gasar rubutu tsakanin ɗalibai da malaman makarantun ƙasashen a cikin harsuna 'yan gida kan zube da

ƙagaggun labarai. A ƙasar Hausa yawancin waɗanda suka shiga gasar malaman makarantun boko ne. Alal misali, gasar da aka yi a 1929 an samar da littattafai har guda 37, 10 a cikin harshen Hausa, 15 a cikin harshen Suto, 9 a cikin harshen Ganda, 2 a cikin harshen Madingo da kuma 1 a cikin harshen Mende. Littafin Komane mai taken Esela e isang phethehong a cikin harshen Suto da kuma na Lwanga mai taken Ebyafayo bya Baganda a cikin harshen Ganda, su ne suka zo na biyu. Babu wanda ya yi nasarar zama na ɗaya, saura kuwa duk sun sami yabo ne kurum.

Idan aka yi nazari littattafan da suka sha yabo daga harshen Hausa su ne na H.B.G. Nuhu mai taken Hausa Stories da na Malam Dodo, shi ma Hausa Stories, sai na Malam Ahemet Metteden, mai suna Zaman Dara da na Malam Bello Kagara mai taken Littafin Karatu Na Hausa, sai kuma na Malam Nagwamatse, mai suna Takobin Gaskiya. Daga wannan gasa mun fahimci cewa tuni waɗanda za su yi wani abin a-zo-a-gani game da ƙagaggen adabin Hausa sun fara bayyana. Malam Bello Kagara yana daga cikin waɗanda suka cinye gasar da hukumar fassara ta shirya a tsakanin 1932 zuwa 1933 da littafinsa Ganɗoki. Shi kuma Malam Nagwamatse duk da cewa bai ci wani abu a gasar 1932/1933 ba, amma ya sha yabo da littafinsa na Boka Buwaye.

Daga abin da muka gani a sama, ko da shekarar 1929 ta ƙarasa cika akwai hukumar Fassara a ƙasar Hausa, wadda ita ce ta kasance unguwarzoma a lokacin waccan gasa ta farko. Sai ƙaruwar makarantu da ɗalibai na gwamnati ya ƙara ɗora sabon nauyi a kan hukumar ta Fassara. Saboda a sami hanyar samar da littattafan karantawa da sauran kayan aiki a waɗannan makarantu ya sa aka yi shawarar kafa wannan hukuma wadda za ta kula da wannan al'amari a tsarin hukuma ta dindindin. Tun daga 1924 wannan batu na kafa wata mai kula da wannan lamari ya kunno kai. Jami'an kula da sababbin makarantu na ƙasar Hausa sun sha aike wa da rahotanni zuwa Kaduna dangane da amfanin da ke tattare ga manufar kafa wata hukuma da za ta samar da kayan aiki na ma'aikatar ilmi da kuma raya adabi, amma hakan ba ta faru ba sai a 1929, lokacin da aka kafa Hukumar Fassara. Wannan hukuma ta fassara ta fara zama ne a cikin ofisoshin makarantar ɗan Hausa da ke Kano. Hukumar ba ta sami mazauninta na musamman ba sai a 1930, lokacin da aka gina shi a {ofar Tukur-Tukur, Zariya.

Babban aikin wannan Hukuma shi ne shirya littattafan Hausa don karatu da koyarwa a makarantu. Hukumar ta soma gudanar da ayyukanta a ƙarƙashin jagorancin Mista C.E.J. Whitting, wanda daga baya ya hannunta aikin gudanar da hukumar ga Mista R.F.S.Parry (Jami'i mai kula da ilmi da ke Zariya). A ran 2/4/1931, Kyaftin F.W. Taylor ya amshi ragamar shugabancin hukumar tare da ma'aikata 'yan ƙasa da suka

haɗa da Malam Sule Isa da Malam Tafida da Malam Umaru, da kuma Malam Shekarau.

A shekarar 1931 Hukumar Fasssara ta fuskanci aikin fassara gadan-gadan tare da shirya littattafai don samar da abin karantawa da koyarwa a makarantun gwamnati. Littattafan da wannan hukuma ta fara fito da su sun ta'allaƙa ne kan tarihin ƙasar Hausa, inda aka shirya aka kuma samar da littafin Hausawa Da MaƙWabtansu da kuma fassara littafin Koyar Da Kiwon Lafiya (I). Daga nan kuma aka tsara littafin Jimlolin Hausa Zuwa Ingilishi. Akwai kuma littafin Koyarwa na Lissafi da Littafin Karantawa Na Fari. Har wa yau, a shekara ta 1931 aka tsara littafin Labaru Na Da Da Na Yanzu (NAK/KAD/EDU/746).

A ranar 18 ga Fabrairu 1932, Kyaftin Taylor ya ajiye aikin shugabancin hukumar fassara. Wannan ya sa aka rufe hukumar na wani lokaci. Sai a ranar 17 ga watan Mayu aka sake buɗe hukumar a Katsina, a ƙarƙashin shugabancin Mista R.M. East. Daga watan Disamba na 1931 zuwa watan Fabrairu na 1932, hukumar fassara ta samar da littattafai da suka haɗa da Darussan Koyarwa Don Makarantun Elementare da littafin Bayani Kan Cututtuka da kuma Magaurayi. A wannan shekara kuma aka kammala fassara littafin Koyar Da Kiwon Lafiya (II), aka kuma sake wa Aljaman Yara fasali, aka sake buga shi. Hukumar ta yi gyare-gyare ga littafin Labaru Na Da Da Na Yanzu, inda aka fassaro sassan tarihin ƙasar Hausa da suke rubuce cikin harshen Larabci aka zuba su a cikin wannan littafi.

Tun daga shekarar 1932 R. M. East ya soma nuna damuwarsa dangane da yadda hukumar fassara ke gudanar da ayyukanta. A nasa tunanin, ya ga cewa ayyukan da ya kamata hukumar ta yi sun wuce fassara kawai. Wanna ya sa yana kama ragamar shugabancin hukumar sia ya shiga fito da sababbin abubuwa da za su inganta aikin hukumar. Baya ga fassarar ayyukan gwamnati da littattafan Elementare, hukumar ta tsara tare da buga littattafai da dama, ga kuma buga Jaridar Nijeriya Ta Arewa da aka soma a 1932. Haka kuma, a sakamakon wannan tunani na R.M. East na ƙoƙarin inganta adabin Hausa ya sa aka soma tunanin yadda za a samar da ƙagaggun labarai daga 'yan ƙasa domin nishaɗantar da al'umma. Haka kuma, aka haɗa har da yin talifi da kuma sayar da littattafai da aka rubuta a cikin harsuna daban-daban na ƙasar Hausa domin samun riba. Hukumar ta tsara yarjejeniya da mawallafa da masu buga littattafai da kuma tsangayoyi na ilmi na Larduna kan tafarkin da ya dace su bi a ga an sayar da littattafan da hukumar ta tsara ta kuma buga.

Har zuwa farkon shekarar 1933, hukumar fassara ta ga ba a sami littattafan adabin da take buƙata ba waɗanda suka shafi ƙagaggun labaran Hausa. Sai dai wani abin la'akari shi ne, ko da hukumar ke ta wannan fafutika, su 'yan Mishau sun yi nisa a wannan fage na samar da

ƙagaggun labarai, domin kuwa W.R.S Miller da ƙungiyar Mishau ta C.M.S tuni suka fahimci amfanin wannan fasali na ƙaga labari domin isar da saƙo, saboda haka suka fitar da littafin ƙagaggen labari na farko na Miller da aka buga cikin harshen Hausa mai suna Fatima, a 1933. Ga alama littafin bai gamsar ba, kuma shi ya sa ba a ji amonsa ba a cikin karikitan ƙagaggun labaran Hausa na tun wancan lokaci. {ila ba wani abu ya sa haka ba sai domin ba ya ɗauke da komi sai wa'azin kirista da yaɗa manufofin addinin Kiristanci. Wataƙila ganin irin rawar da C.M.S da Miller suke neman takawa ya sa aka shirya gasa ta biyu da ta taimaka wajen samar da littattafan adabin Hausa na farko ta fuskar zube daga 'yan gida. An dai shirya wannan gasa ne da manufofi biyu; ta farko a samar da ingantattun littattafan adabi, na biyu a sayar da littattafan ba a raba kyauta kamar yadda aka saba yi ba a da.[25] Wannan gasa ta samar da littattafai da suka inganta tare da kyautata adabin Hausa, kuma an gudanar da ita ne a shekarar 1933.

Auna Fahimta
Domin gane ko an fahimci wannan darasi da kyau, sai a bayyana abubuwa kamar haka:

- Me ya faru kafin samar da rubutaccen Labarin Hausa?
- Wace rawa Larabawa suka taka?
- Wace gudunmuwa Turawa suka bayar?
- Wacce gudunmawa Hukumar Fassara ta bayar??

## 1.4 Kammalawa

Wannan darasi shi ne ya fayyace yadda aka samar da rubutattun labaran farko da aka gani da yadda aka samar da littattafan da irin gwagwamayar da aka sha domin samar da labaran Hausa a rubuce tun daga shekarar 1927 zuwa 1933.

## 1.5 Taƙaitawa

Darasin ya gabatar mana da abubuwan da suka haɗa da:

- Bayani game da samuwa da wanzuwar rubutun zube na Hausa a zami zuwan Laraawa da Turawa.
- Yadda aka samar da littattafan farko a Hausa Jingar Aiki

1. Me ya faru da zuben Hausa bayan zuwan Larabawa?
2. Wace gudunmuwaTurawa suka bayar wajen samar da rubutaccen zuben Hausa?
3. Wace gudunmuwa 'yan Mishan suka bayar wajen samuwar littattafan zuben Hausa na farko?

## 1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language, London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory, Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari), Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce, Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982); “Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa.” Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009); Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd.

Malumfashi, I. (2019); Labarin Hausa A Rubuce: 1927-2018. Zaria: ABU Press and Publishers

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa. **Zariya:** NNPC

bambadiya.blogspot.com

www.rumbunilimi.com.ng

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1 Me ya faru kafin samar da rubutaccen Labarin Hausa?

Kafin samarda rubutattun labaran Hausa, Hausawa suna da hanyoyin sadarwa na gargajiya da suka wadatar da su kafin a mayar da harkoki ga takarda ko makamantantan haka.

2 Wacce rawa Larabawa suka taka?

Larabawa sun taimaka wajen zuwan Musulinci qasar Hausa wanda sai da aka ƙaddamar da shi a nahiyar Hijaz a tsakanin ƙarni na 7 da na 8, sa'annan ya watsu zuwa sassa daban-daban na duniya, gami da ƙasar Hausa. Daga Gabas ta Tsakiya addinin Musulunci ya ratso zuwa nahiyar Afirka da Turai, musamman sassan Magrib da Andalusiya. Addinin Musulunci ya barbazu a ko'ina, inda sannu a hankali ya zama addinin duniya. Daga Afirka ta Arewa ne Musulunci ya cuso kai zuwa Yammacin Afirka, ta amfani da aƙalla hanyoyi guda biyu muhimmai. Waɗannan hanyoyi sun amfanar ne ta hanyar hada-hadar ciniki da saye da sayarwa wanda ta haka ne aka samu rubutun ajami.

3 Wace gudunmuwa Turawa suka bayar?

ƙungiyoyi daga jinsin Turawa, sun aiko da masana don su binciki yadda ƙasashen Afirka suke da yadda al'adunsu ke gudana da yanayin harsunansu da kuma addinansu. A kwai kuma ƙungiyoyin Mishau da Turawa suka turo don bincike, musamman kan al'adu da harsuna da addinan ƙasashen Afirka a tsakanin ƙarni na 18 da na 19. Shahararru daga cikin waɗannan 'yan mishau su ne Barth da Schon. Ta fuskar ayyukan Barth da Schon ne labaran ƙasar Hausa da jama'arta suka isa Turai, kai tsaye. Ya wallafa littattafai kan kalmomin Hausa a 1843 da {amus na harshen Hausa a 1876 da littafin karin maganganu da labarai da tatsuniyoyin Hausa a 1886 da kuma littafin Magana Hausa (1885) da wasu da dama da suka shafi addinin Kirista. Ayyukan da su Schon suka gabatar sun ba da haske wajen samar da wata kafa ta mayar da adabin bakan Hausa a rubuce. Tun kafin a kafa mulkin mallaka a ƙasar Hausa aka mayar da wasu sassan adabin bakan Hausa a rubuce cikin haruffan Romanci.

3 Wace gudunmawa hukumar fassara ta bayar?

Hukumar fassara ta bayar da gudunmawa wajen bunqasa rubutun zube. A shekarar 1931 Hukumar Fasssara ta fuskanci aikin fassara gadan-gadan tare da shirya littattafai don samar da abin karantawa da koyarwa

a makarantun gwamnati. Littattafan da wannan hukuma ta fara fito da su sun ta'allaƙa ne kan tarihin ƙasar Hausa, inda aka shirya aka kuma samar da littafin Hausawa Da MaƙWabtansu da kuma fassara littafin Koyar Da Kiwon Lafiya (I). Daga nan kuma aka tsara littafin Jimlolin Hausa Zuwa Ingilishi. Akwai kuma littafin Koyarwa na Lissafi da Littafin Karantawa Na Fari. Baya ga fassarar ayyukan gwamnati da littattafan Elementare, hukumar ta tsara tare da buga littattafai da dama, ga kuma buga Jaridar Nijeriya Ta Arewa da aka soma a 1932. Haka kuma, a sakamakon wannan tunani na R.M. East na ƙoƙarin inganta adabin Hausa ya sa aka soma tunanin yadda za a samar da ƙagaggun labarai daga 'yan ƙasa domin nishaɗantar da al'umma. Haka kuma, aka haɗa har da yin talifi da kuma sayar da littattafai da aka rubuta a cikin harsuna daban-daban na ƙasar Hausa domin samun riba.

## Kashi Na 2 Hukumomin Inganta Adabi Da Samuwar Rubutaccen Zube

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Gasa Da Samuwar Rubutaccen Zube
 2.3.1 Gasar 1927 Da Samuwar Rubutun Zube
 2.3.2 Gasar 1929 Da Ginuwar Rubutun Zube
 2.3.3 Gasar 1932 Da Wanzuwar Rubutun Zube
 2.3.4 Samuwar Littafin Fatima
2.4 Kammalawa
2.5 Taƙaitawa
 Jingar Aiki
2.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa

A wannan kashi za a duba tarihin yadda aka samar da rubutattun labaran farko da cikakken bayanni kan gasar 1927 da 1929 da 1932 da kuma tattauna littafi farko da ya fito, wato littafin Fatima da dalilin samar da shi.

### 2.2 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi za ka fahimci tasirin:

- Gasar 1927 ga Rubutun zube
- Gasar 1929 ga rubutun zube
- Gasar 1932 ga rubutun zube

### 2.3 Gasa Da Rubutaccen Zube

Kamar yadda ɗanamarya (2012) ya bayyana, hukumomin ilimi sun yi ta ƙoƙarin bin hanyoyi da matakai da ma dubarun da za su dasa tare da samar da ingantaccen adabi ga mutanen da suke yi wa aiki. Bisa wannan tunani ne, Hukumar kula da Kwalejin Ilimi ta Katsina, ta shirya gasar rubuta ƙagaggen labari cikin Hausa a tsakanin ɗaliban kwalejin a shekarar 1927.

### 2.3.1 Gasar 1927 Da Samuwar Rubutun Zube

Manufar shirya wannan gasa ita ce koya wa ɗalibai fasahar ƙirƙira labarai a cikin harshensu. Haka kuma, yin hakan zai sa a sami labaran karantawa masu sanya nishaɗi ga al'ummar Hausawa. A wannan lokaci Dr. East yana ɗaya daga cikin jami'an makarantar da suka shirya wannan gasa, kuma yana aikin malanta. Abubakar Imam na ɗaya daga cikin ɗaliban da suka rubuta labarai domin shiga gasar. Labaran da suka rubuta a matsayinsu na ɗalibai ba su ƙunshi abin a zo a gani ba, sai dai duk da haka an aiko masu da ladan £3 (pounds), amma ba a buga labaran waɗanda suka ci gasar a matsayin littafi ba. Hukumar makaranta ta miƙa wa Abubakar Imam ladan sule goma a matsayin shi ne wanda ya lashe gasar kuma ya fi kowa nuna bajinta, Mora (1989:28).

Abubakar Imam ya nuna cewa ya rubuta ƙagaggen labarin amma bai iya tuna batun labarin da ya yi rubutu a kai, kuma ba a buga shi a matsayin littafi ba. Haka nan babu wani kwafi na labarin a hannunsa, don haka labarin yana da wuyar samu ga masu yin nazari, Abdullahi (1998:23).

Wannan gasa ita ce ta zama zakaran gwajin dafi a share fage da nuna hanya tsakanin 'yan bokon ƙasar Hausa, na yadda za a yi amfani da basirar ƙiƙirar ko ƙagawa a maimakon fassara kamar yadda ake yi da, domin samar da littatafan labarai cikin harshen Hausa a makarantu ko domin nishaɗi a yayin da ake karanta su.

### 2.3.2 Gasar 1929 Da Ginuwar Rubutun Zube

A cikin shekarar 1903 aka sake shirya wata gasa. Wannan gasar kamar waccan ce ta farko, in da aka nemi marubuta da su yi rubutu a kan ƙagaggen labari cikin harshensu su aika. Hukumar Nazarin Al'adu da Harsunan mutanen Afirka ta ɗauki alhakin shiryawa da gudanar da wannan gasa. Duk da cewa wannan hukuma ta fara shirya wannan gasa a shekarar 1903, ba a sami Hausawa 'yan ƙasa sun shiga ba sai a cikin shekarar 1931, inda wasu Hausawa 'yan arewacin Nijeriya suka shiga gasar kamar yadda aka nema. Dr. East shi ne jami'in da ya jagorancta tare da wakiltar malaman da suka rubuta labaran shiga gasar a gaban hukumar da ke da mazauninta a Ingila.

An ƙiyasta ladar £20 da za a baiwa waɗanda suka shiga gasar kuma suka yi nasara a matsayin goro ga wanda ya zama na ɗaya, £10 ga wanda ya zo na biyu da kuma £5 ga wanda ya zama na uku. Sai kuma duk wanda ya rubuta abin a zo a gani gwargwado za a ba shi wani hasafi. Kimanin marubuta 39 suka shiga gasar daga harsunan Afirka. Daga harshen Hausa kuwa babu wanda ya samu zuwa na farko, sai dai akwai waɗanda suka sami kyaututtuka na biyu zuwa ƙasa.

Kamar yadda aka ambata a baya, jami'an da suka wakilci waɗanda suka shiga gasar na daga cikin kwamitin da ke nazarin labaran da aka aika da su domin bayar da matsayi da kyaututtuka ga waɗanda suka sami nasara. Bayan an gama nazarin dukkanin labaran da aka aika a wajen gasar daga harsuna daban-daban na Afirka, sai aka aika da kyautar kuɗi har sule talatin ga duk wanda ya shiga gasar. A harshen Hausa mutum tara (9) suka rubut amma mutum shidda (6) ne kawai suka sami kyautar inda aka aiko masu da kuɗi £3 kowannensu kamar haka: -

**Sunan Marubuci** **Sunan Littafi** Mal.
H.B.G Nuhu Hausa Stories Mal. Dodo
Hausa Stories Mal. Ahmed Metteden
Zaman Dara Mal. Nagwamatse Takobin
Gaskiya
Mal. Bello Kagara Littafin Karatu na Hausa
ɗan Mal. Alkali Sokoto Labaran Hausa
Westermann (1933).

Waɗannan su ne kaɗan daga cikin malaman da suka shiga gasar daga ƙasar Hausa. Akwai harsunan Suto da Ganda da Mende da Madingo waɗanda su ma sun aika da nasu labaran a cikin harsunansu. Cikinsu an sami zakaru da waɗanda suka nuna bajinta kuma aka ba su lada gwargwadon rawar da suka taka a gasar. Amma abin takaici, daga ƙarshe hukumar da ta shirya tare da gudanar da gasar ta yi shelar cewa, ba za ta ɗauki nauyin buga waɗannan labarai a matsayin littatafai ba, sai dai jami'an da suka je a matsayin wakilai su taimaka wa masu sha'awar buga labaransu a matsayin littatafai wajen yin hakan.

Waɗannan labarai da aka samar a lokacin wannan gasa, ba a buga su ba, kuma ba a dawo da su ga marubutansu ba. Haka ma ba a yi masu wani tanadi da za su kawo yanzu ba, ballantana a sanya su cikin jerin littatafan da ake nazarinsu kamar yadda ake yin nazarin sauran littatafan da aka samar ta hanyar yin gasa. Shiryawa da gudanar da wannan gasa ya yi tasiri matuƙa ga samar da littatafai musamman ta fuskar samun kyaututtuka da sika biyo bayan gasar, Westermann (1933: 102-103).

### 2.3.3 Gasar 1932 Da Wanzuwar Rubutun Zube

Bayan kyaututtukan da aka aiko ga waɗanda suka shiga gasar da ta gabata, sai gwamnati a can Ingila ta bai wa Turawan mulkin mallaka damar shirya wata sabuwar gasa da kansu a garuruwan da suke shugabanta tun da sun rigaya sun sami haske game da yadda ake gudanar da ita. Maƙasudin shirya wannan gasa kuwa a daidai wannan lokaci shi ne, domin dasa tsiron harsashin adabin Hausa a cikin boko. Haka kuma, akwai nufin koya wa 'yan ƙasa yadda za su iya samar da labaran ƙirƙira cikin harshensu. Har ila yau, ana son a sami littattafan

sayarwa don samun kuɗin shiga ga hukumar, kuma a sami littattafan nishaɗi ga jama'a musamman masu sha'awar karatu.

A shekarar 1932/1933 Hukumar fassara ta shirya wannan gasa, kuma ta danƙa alhakin karaɗe ƙasar Hausar ga Dr. East, inda nan take ya zagaya garuruwan Katsina da Kano da Sakkwato da Bauchi da Kebbi da wasu garuruwa da ya haɗu da ɗalibai da malamai tare da bayyana masu abinda ya shafi tsari da fasalin yadda littattafan za su kasance. Dr. R.M East ya jaddada ma waɗanda suka shiga gasar cewa hukumar ba za ta amince da duk wani nau'i na ajin fassarar fasahar wani ba Malumfashi (2009).

Hukumar fassarar ta sami littatafai da dama daga waɗanda suka amsa kira na shiga wannan gasa. Mafi yawan littatafan da aka aiko wa hukumar domin shiga gasar sun dace tare da yin biyayya ga tsarin da ta shimfiɗa. Lokacin da hukumar ta zo buga littatafan sai da ta yi masu taciya sosai musamman farkonsu da ƙarshensu, da kuma sake tsarin babobinsu, sannan ta buga su. Sakamakon wannan gasa ya fito ne bayan ta gama tsarawa da sake fasalin waɗannan littatafai, sannan aka fitar da sakamakon gasar kamar haka:

| **Sunan Marubuci** | **Sunan Littafi** |
|---|---|
| Malam Abubakar Kagara | Ruwan Bagaja |
| Mal. Bello Kagara | Ganɗoki |
| Abubakar Bauchi | Shehu Umar |
| Muhammad Gwarzo | Idon Matambayi |
| East da Tafida | Jiki Magayi |

Akwai wasu littattafan da suka shiga wannan gasa baya ga waɗannan. Duk da cewa waɗannan ne aka za~a, su ma waɗancan sun taka rawar gani domin sun gamsar da hukumar. An yi nufin buga su bayan an sake masu tsari, amma hakan ba ta samu ba. Littattafan su ne:

| **Sunan Marubuci** | **Sunan Littafi** |
|---|---|
| Mal. Nagwamatse | Boka Buwaye |
| Mal. Jumare Zariya | Yarima Abba |

Daga ƙarshe wannan hukuma ta cimma gurinta na samar da littattafai da abin karantawa don nishaɗi, duk da cewa waɗannan littatafai ba nan take aka buga su ba sai daga baya har ma littafan suka yi ta shiga kasuwa, Malumfashi (2009).

### 2.3.4 Samuwar Littafin Fatima

Littafin Fatima ƙagaggen labari ne da Likita Walter Miller ya rubuta a shekarar 1933. Likita Miller ɗan Mishan ne na ƙungiyar Church Missionary Society (CMS) da suka shigo ƙasar Hausa suka zauna a garin Zariya a shekarar 1905 a ƙarƙashin Ayarin Mishan Ga Hausawa. Marubucin ya rubuta littafin a daidai da shekarar da Hukumar Talifi ta ƙaddamar da gasar rubuta ƙagaggun labaran Hausa a dukkan faɗin Arewacin Nijeriya. Ya rubuta littafin ne da kila nufin shiga wannan gasar, amma kasancewar littafin na ƙunshe da batutuwan yaɗa addinin Kirista ya sa bai sami kar~uwa ga Hukumar Talifi ba. An buga littafin a ɗakin ajiye littattafai na ƙungiyar CMS da ke Legas a shekarar 1933.

Littafin Fatima ya ƙunshi jigon yaɗa addinin Kirista ne a cikinsa. Likita Miller ya tsara jigon ne ta hanyar nuna irin yadda addinin Kirista ke gyara halayen mutane da mayar da su mutanen kirki. Ya yi haka ta kawo irin karimci da mabiya addinin Kirista ke nuna wa jama'a ko sun san su ko ba su san su ba. Bai tsaya nan ba kawai, ya bi addinin Musulunci ya ~ata ta hanyar nuna Musulmi ba su da halaye na gari. Tun a farko-farkon littafin ya fara fito da halayen kirki na Kiristoci bayan da ya kawo haɗarin jirgin ƙasa a Zariya inda wani Musulmi mai suna Audu ya sami rauni kuma yaran Mishan suka kawo shi a gidansu na Mishan. Ga yadda ya kawo wani Likita mai suna Harris ya kar~i Audu.

'Sannunku! amma dai na fi so in ɗauki wannan yau gama ina so in lura da yaron nan da kyau a chikin daren nan, kada wani abu ya hau kan chiwon nan....' (Shafi na 9).

Ire-iren waɗannan halaye na gari na Harris wai su suka sa wani matashi Musulmi mai suna Auta ya zama Kirista kamar yadda marubucin ya kawo a shafi na 10 kamar haka:

'Sa'anda suka fito daki suka rufe kofa, Auta ya che ma Sule da Iro, mataimakansa, ''Ina za a sami Bature kamar wannan? Wanene ba za ya ji dadin aiki tare da shi ba?.......Loto loto ya kan kira ni in zo dakinsa, mu yi addu'a tare, amma ba ya taba nuna mani wani halin alfarma ba. Ta wajen irin wannan fa na ga dukan abinmu na da ba su da wani anfani ba, gama a raina na che, 'Idan addinin Isa Almasihu ya iya maida mutum kamar wannan Bature, Dr. Harris, wannan addini shi ne zan bi har abada. Abin da ya sa na zama Christian ke na; ba domin wani abin da ya koya mani na wajen karatu ba..........'

A shafi na 13-14 marubucin ya kawo wasu halayen kirki na wata yarinya Kirista mai suna Hassana abin da ya ba Audu wanda aka yi jinya a gidan Mishan mamaki har ya nemi Auta ya gaya masa dalilin halayenta na gari haka. Auta ya amsa masa;

Hasana Christian che, Audu, shi ya sa: wannan ga abin da ni kaina na gani. A chikin addinin Muhammadiya ba shi yiyuwa a sami wannan irin hali; ko kai da kanka ka taba gani ba?

**Auna Fahimta**

Domin fahimtar ko darasin ya zauna sai ɗalibai sun fayyace abubuwa kamar haka:

- Mece ce manufar gasar shekarar 1927?
- Wace rawa gasar 1932 ta bayar ga adabin Hausa?
- Me ya faru a tsakanin 1932 da 1933?
- Bayani kan littafin Fatima a matsayin littafin farko a ƙasar Hausa
- A Wace shekarar aka buga littafin Fatima?

## 2.4 Kammalawa

{oƙarin wannan darasi shi ne ya bayyana tarihin yadda aka samar da rubutattun labaran farko da cikakken bayanni kan gasar 1927 da 1929 da 1932 da kuma tattauna littafi farko da ya fito, wato littafin Fatima da dalilin samar da shi.

## 2.5 Taƙaitawa

Darasin ya gabatar mana da abubuwa ne da suka haɗa da:

- Bayani kan Hukumomin Inganta Adabi Da Samuwar Rubutaccen Zube
- Yadda aka assasa da gudanar da gasar 1927 da 1929 da kuma ta 1932 da samuwar rubutun ginuwar rubutun zuben Hausa.
- An kuma dubi samuwar littafin farko na Hausa na Fatima

**Jingar Aiki**

1. Wace gudunmwa ce Hukumomin adabi suka bayar wajen samuwar rubutaccen labarin Hausa?
2. Tattauna gasar 1927 da irin rawar da ta taka wajen samuwar rubutun zuben Hausa.
3. Waɗanne littattafai gasar 1929 ta samar a ƙasar Hausa? Tattauna.

## 2.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language, London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory, Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984). Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari), Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce, Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982). 'Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa.' Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009). Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd

Malumfashi, I. (2019). Labarin Hausa A Rubuce: 1927-2018. Zaria: ABU Press and Publishers

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa**.** Zariya: NNPC

bambadiya.blogspot.com
www.rumbunilimi.com.ng

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1 Manufar shirya gasar 1927
Koyawa ɗalibai fasahar ƙirƙira labarai a cikin harshensu da kuma samar da labaran karantawa masu sanya nishaɗi ga al'ummar Hausawa.

2 Wace rawa gasar 1932 ta bayar ga adabin Hausa?
Samar da littattafai da abin karantawa don nishaɗi,

3 Me ya faru a tsakanin 1932 da 1933?
Gwamnatin Ingila ta bai wa Turawan mulkin mallaka damar shirya wata sabuwar gasa da kansu a garuruwan da suke shugabanta don dasa tsiron harsashin adabin Hausa a cikin boko da koyawa 'yan ƙasa yadda za su iya samar da labaran ƙirƙira don samun kuɗin shiga ga hukumar, kuma a sami littattafan nishaɗi ga jama'a.

A shekarar 1932/1933 Hukumar fassara ta shirya wannan gasa, kuma ta danƙa alhakin karaɗe ƙasar Hausar ga Dr. East, inda nan take ya zagaya garuruwan Katsina da Kano da Sakkwato da Bauchi da Kebbi da wasu garuruwa da ya haɗu da ɗalibai da malamai tare da bayyana masu abinda ya shafi tsari da fasalin yadda littattafan za su kasance.
Hukumar fassarar ta sami littatafai da dama daga na shiga wannan gasa. Mafi yawan littatafan da aka aiko wa hukumar domin shiga gasar sun dace tare da yin biyayya ga tsarin da ta shimfiɗa. Hukumar ta tace littattafan da kuma sake tsarin babobinsu, sannan ta buga su.

4 Bayani kan littafin Fatima a matsayin littafin farko a ƙasar Hausa?

Littafin Fatima ƙagaggen labari ne wanda ya ƙunshi jigon yaɗa addinin Kirista. Likita Miller ya tsara jigon ne ta hanyar nuna irin yadda addinin Kirista ke gyara halayen mutane da mayar da su mutanen kirki da ɗan Mishan na ƙungiyar Church Missionary Society (CMS) Likita Walter Miller ya rubuta a shekarar 1933 kuma ya rubuta littafin a daidai da shekarar da Hukumar Talifi ta ƙaddamar da gasar rubuta ƙagaggun labaran Hausa a dukkan faɗin Arewacin Nijeriya. Ya rubuta littafin ne da kila nufin shiga wannan gasar, amma kasancewar littafin na ƙunshe da batutuwan yaɗa addinin Kirista ya sa bai sami kar~uwa ga Hukumar Talifi ba. An buga littafin a ɗakin ajiye littattafai na ƙungiyar CMS da ke Legas a shekarar 1933.

5 A wace shekarar aka buga littafin Fatima?1933

## Kashi Na 3 Rawar Hukumomin Inganta Adabi Wajen

## Tabbatuwar Rubutun Zube

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Daras
3.3 Rawar Hukumomin Inganta Adabi Wajen Tabbatuwar Rubutun Zube
3.3.1 Hukumar Fassara
3.3.2 Hukumar Talifi
3.3.3 Hukumomin Gaskiya Da NORLA Da NNPC
3.4 Kammalawa
3.5 Taqaitawa
3.6 Manazarta
3.7 msoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa

A babin da ya wuce an bayyana tarihin yadda aka samar da rubutattun labaran farko da cikakken bayanni kan gasar 1927 da 1929 da 1932 da kuma bayanai a kan littafin farko littafin Fatima da dalilin samar da shi. A wannan kashi za a yi nazarin irin rawar da hukumomin inganta adabi suka bayar don samar da kuma inganta rubutun zube na Hausa.

### 3.2 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi za ka fahimci:

Hukumar Fassara da irin rawar da ta taka don Inganta Adabi Wajen Tabbatuwar
Rubutun Zube

### 3.3 Rawar Hukumomin Inganta Adabi Wajen Tabbatuwar

Rubutun Zube

Kamar yadda Usman (2011) ta bayyana, bayan yawaitar makarantun boko a Arewacin Nijeriya, musamman daga shekarar 1916, sai ɗalibai suka yawaita, kuma iyaye da sarakuna da sauran al’ummomi suka ƙara fahimtar fa’idar wannan sabon tsarin ilmi, nan take sai matsaloli suka kunno kai. Daga cikin waɗannan matsaloli akwai; ƙarancin littatafan karatu da na horarwa. Wannan ya sa aka fara tunanin samar da wata hukuma da za ta yi maganin wannan matsala.

Tun a shekarar 1924 aka soma tunanin kafa wannan hukuma a tsakanin jami'an gwamnati, amma hakan bai yiwu ba sai a shekarar 1929, lokacin da aka kafa ta a birnin Kano. An dai kafa ta ne domin samar da kayayyakin aiki a makarantu. Da yake ba ta da wani matsuguni na musamman sai ta fara zama a harabar makarantar ɗan Hausa da ke Kano, amma daga baya a shekarar 1930 ta samu mazauninta na dindindin a ƙofar Tukur-Tukur da ke Zariya ta koma can da zama.

### 3.3.1 Hukumar Fassara

Hukumar ta soma gudanar da aikinta a ƙarƙashin jagorancin wani Bature mai suna C.E.J.Whitting. Bayan shi kuma sai, aikin gudanar da hukumar ya koma hannun R.F.S.Parry, wanda yake jami'i ne mai kula da ilmi da ke Zariya.

Wani abin la'akari a nan shi ne, ko da hukumar fassara ke ƙoƙarin tabbatar da zamanta, tana hulɗa da hukumomi irin ta da tsangayoyi masu sha'awar fassara da talifi. Tsangayar da ta yi tasiri sosai kan wannan hukuma ita ce wadda ke kula da harsuna da al'adun Afirka da aka kafa tun a 1905. Wannan Tsangaya ita ce wadda ta fara shirya gasa tsakanin 'yan Afirka domin samar da littattafai na karantawa a maimakon fassaro su kawai. A nan Arewacin Nijeriya hukumar fassarar ce ta taimaka wa 'yan ƙasar da suka shiga cikin waccan gasar ta Afirka, domin ta hanyarta ne aka miƙa littattafan da suka shiga waccan gasar. Daga cikin littattafai 37 da suka shiga gasar wallafa ta Afirka da aka yi a shekarar 1930, na harshen Hausa guda goma ne, Westerman,(1933). Sai dai ba wani daga cikin goman da ya ci gasar, amma wasu sun samu yabo, kuma su ne:

| | |
|---|---|
| H.B.G.Nuhu | Hausa Stories |
| Malam Dodo | Hausa Stories |
| Malam Ahemet Metteden | Zaman Dara |
| Malam Bello Kagara | Littafin Karatu na Hausa |
| Malam Nagwamatse | Takobin Gaskiya |

Saboda haka ko da a shekarar 1931 Kyaftin F.W.Taylor ya amshi shugabancin hukumar ya iske cewa an soma gauraya aikin fassara da talifi. Wannan shi ya sa su kan su 'yan ƙasa da ke aiki tare da shi suka ci gaba da yin irin wannan gauraye lokaci zuwa lokaci. Ma'aikatan da suka kama masa a wannan zamani sun haɗa da Malam Sule da Malam Tafida da Malam Umaru da Malam Shekarau, (NAK. Zaria Prof/14830/Vol/1/1930), waɗanda suka kasance 'yan ƙasa na farko da suka soma aiki a hukumar. A lokacin mulkin F.W.Taylor da muƙarrabansa an gudanar da aikin fassara ba ji-ba gani, domin samar da abin karantawa a makarantun Gwamnati da kuma wasu ayyuka na musamman domin amfanin gwamnati da hukumominta.

A shekarar 1932 F.W.Taylor ya koma gida Ingila, wannan ya sa aka rufe hukumar na wani lokaci, sai a ranar 17 ga Mayu na shekarar 1932, Rupert Moultrie East ya amshi shugabancin hukumar, sai dai a wannan karo a garin Katsina, inda yake aikin koyarwa, Malumfashi (2009 da Ahmad, 2009).

Idan aka yi nazarin ayyukan hukumar daga samuwarta zuwa shekarar 1932 da East ya amshi jagorancinta, za a fahimci cewa ayyuka ne mabambata. Alal misali kamar yadda Malumfashi, (2009) ya bayyana, hukumar ta yi aikin talifi da kuma fassara a haɗe. Hukumar Fassarar ce ta shirya littafin Hausawa da maƙwabtansu da kuma fassara littafin Koyar Da Kiwon Lafiya (I da II) da littafin Jimlolin Hausa Zuwa Ingilishi da littafin Koyarwa na Lissafi da Littafin karantawa na fari da Labaru Na Da Da Na Yanzu.

A cikin shekara ta 1932 ne Hukumar Fassaara ta samar da littattafai da suka haɗa da Darussan Koyarwa Don Makarantun Elementare da littafin Bayani Kan Cututtuka da kuma Magaurayi.

A wannan shekara ne kuma aka kammala fassara littafin Kiwon Lafiya (II), aka kuma sake wa Aljaman Yara fasali, aka sake buga shi, Malumfashi (2009).

Ke nan za a iya cewa, ba wani wanda ya taimaka sosai wajen tabbatuwar wannan hukumar kamar R.M.East. Tun daga wannan lokaci na zaman R.M.East a hukumar Fassara aikin hukumar ya cigaba da canzawa daga fassara kurum zuwa wasu ayyuka na talifi, musamman ganin cewa tun a 1930 an koya wa 'yan ƙasa irin wannan harka tun da farko. Shi kuma East ya yi haka ne ganin cewa irin wannan hukuma da ake da ita a wasu sassa na duniya da ya yi nazari, su ma gaurayawa suke yi da wasu ayyuka na daban.

Daga wannan lokaci sai hukumar ta shiga harkar buga abubuwa da dama da suka haɗa da littattafan labarai da Jaridar Najeriya ta Arewa da aka fara a shekarar 1932. Ba wannan kaɗai ba, hatta ƙagaggun labarai da tatsuniyoyi wannan hukuma ta samar da su. Hakan ya faru ne ta hanyar shirya gasa da ita ma hukumar ta tsara tsakanin 'yan ƙasa daga shekarar 1932 zuwa 1933. Bari mu dubi yadda wannan gasa ta kasance domin gane waɗansu batutuwa game da gauraye da Hukuma Fassara ta yi, wanda ya jawo dole a sake dubar fasalinta da yi mata kwaskwarima daga baya.

Kafin a shirya wannan gasar sai da shugaban hukumar R.M.East, ya kai ziyara wasu sassan ƙasar Hausa, kamar Katsina da Kano da Sakkwato da Bauci da Birnin Kebbi. A wannan ziyara ya tattauna da malamai da ɗalibai da ake da su a waɗannan wurare. A maimnakon ya sanar da su

yadda ake fassara ko ya ce su fassaro labarai, ya bayyana masu abubuwan da yake so su rubuta na littattafan labaran da ake so a samar. (NAK/ADN/1029/1934). Wani abin sha’awa ma shi ne, East ɗin da kan sa ya bayyana cewa Hukumar Fassara ba za ta amshi littafin da ba ƙagawar marubucinsa ba ne, kuma ba za a kar~i fassara ko makamancin haka ba, Malumfashi (2009). Idan da aikin hukumar shi ne fassara to da ƙila abin da za ta mayar da hankali kai ke nan. Saboda haka ko da aka gama gasar, Hukumar Fassara ta sami damar kar~ar littattafai da dama da suka shiga gasar waɗanda aka aiko wa hukumar da suka dace da tsarin da aka shimfiɗa. A lokacin da hukumar ta zo bugawa sai da ta tace wasu da dama, sa’annan aka buga su, (NAK/ADN/1029/1934). Ga yadda littatafan gasar suka kasance:

| | |
|---|---|
| Ruwan Bagaja | Malam Abubakar Kagara |
| Gandoki | Malam Bello Kagara |
| Shaihu Umar | Malam Abubakar Bauchi |
| Idon Matambayi | MalamMuhammadu Gwarzo |
| Jiki Magayi | East da Tafida |

Bayan waɗannan da suka lashe gasar akwai kuma wasu da suka samu yabo amma ba a buga su ba. Ga yadda suka kasance kamar yadda Malumfashi (2009) ya kawo su:

| | | |
|---|---|---|
| 1 | Malam Nagwamatse | Boka Buwaye |
| 2 | Malam Jumare Zariya | Yarima Abba |

Abin la’akari a nan shi ne, waɗannan littattafai guda bakwai sun kasance ƙagaggun labarai ne, amma da alama fassara ta taka rawa wajen samar da su. Wataƙilka shi ya sa hukumar fassara ta kasance ungozomansu. Dubi misalin littafin Abubakar Kagara na Ruwan Bagaja, yawancin kayan cikinsa fassara ce. Alal misali an fassaro wani ~angare na littafin Alfu Laylah Wa Laylah da littafin The Brother’s Fairy Tales, Malumfashi (2009). Saboda haka idan an ga wasu daga cikin waɗannan littattafai sun kasance ƙagaggu, to kuma fassara ta taimaka wajen samar da su, duk da cewa ba fassarar ce aka yi kai tsaye ba.

Ke nan abin da za mu iya cewa hawan East bisa kujerar shugabancin hukumar ya ɗora ta bisa wancan tsari ne da ya gada; da sani ko ba da sani ba. Domin kuwa a ƙarshen gasar da aka yi a 1933, sai ga gaurayen fassara da ƙagawa da sauran abubuwa sun ci gaba da wanzuwa. Wannan tsari da hukumar ta ci gaba da gudanarwa da kuma wasu dalilai masu dama da za a kawo nan gaba, su ne suka taimaka wajen samuwar hukumar talifi da ma duk waɗansu ayyuka da ta yi da ba na fassara ba. A nan za mu mayar da hankali ne wajen gano dalilai ko musabbaban da suka wanzar da haka.

### 3.3.2 Hukumar Talifi

Wani abin ƙarin la'akari kafin mu shiga kawo dalilan da suka haifar da Hukumar Talifi shi ne, duk abin da ya faru a guri ɗaya ne ya faru, wato canjin suna ne kurum aka fi mayar da hankali kai ba wai canza ma'aikata ko ofis ko kuma ayyuka ba. A wannan ~angare na wannan bincike an tattauna wasu daga cikin dalilan da suka haifar da canza sunan Hukumar Fassara zuwa ta Talifi, domin a gane yadda tarihin ya yamutse da kuma yadda tsttsefe shi yake da muhimmanci ga wannan bincike.

Daga ranar 14 ga watan Yuli na shekarar 1936, wasiƙu suka shiga gilmewa tsakanin hukumomin gwamnati dangane da yadda Hukumar Fassara take shirya jarrabawa domin baƙin Turawa da suka zo aiki a Arewacin Nijeriya. An dai fahimci cewa jarrabawar ta yi tsauri, ga shi kuma ana samun matsalar fahimtar haruffan da ake amfani da su, NAK/ADN/767/Vol.3/303,(1936). Haka kuma, ana cikin wannan cece-ku-ce sai wasu hukumomin gwamnati suka shiga aiko wa hukumar ayyukan fassara kai tsaye. Alal misali, jami'i mai kula da ~angaren kiwon lafiya ya turo da tallar allo da ke magana kan yadda masu dabbobi za su isa zuwa Zango da Sabon Gari daga Kaduna, NAK/ADN/767/Vol.3/306,(1936). Nan take hukuma ta yi kamar yadda aka umurce ta. Ba a daɗe ba kuma sai ga wata wasiƙar daga Sakataren Lardunan Arewacin Nijeriya zuwa ga babban Jami'i mai kula da ilmi, yana kira da a ce ma Hukumar Fassara ta fassara dokar gwamnati ta kotuna 'yan ƙasa cikin Hausa. Wannan ya jawo taƙaddama tsakanin Hukumar Fassara da ofishin jami'i mai kula da ilmi, domin kuwa kamar yadda East ya faɗa a cikin amsar wasiƙar da aka aiko masa, ya ce:

A halin da ake ciki dukkan ma'aikatan hukumar na fama da aikin rubuta littattafan labarai (Magana Jari Ce). Ba zan so na matsa musu da wani aiki ba ganin cewa ba mu da isasshen lokaci, domin kuwa aron malam Abubakar aka ba mu na watanni. Za mu fassara waɗannan dokoki nan gaba idan ba aikin gaggawa ba ne. In so samu ne a bari har mu kammala aikin rubutun Magana Jari Ce. Ko kuma in mun sami wani sabon ma'aikaci. Idan ba ka manta ba, tuni ka ba mu dama mu dinga yin irin wannan aiki, tun a shekarar 1935. NAK/ADN/767/Vol.3/311,(1936).

Duk da irin wannan bayani da ya yi, sai da aka sake tuntu~ar East ko yaushe zai yi aikin fassarar idan ana buƙata nan gaba. Ya dai mayar da amsar cewa, aikin zai iya samuwa idan ya kammala ayyukan da ke gabansa. Na farko ga dai aikin rubutun littafin Magana Jari Ce, wanda zai kai har ƙarshen watan Disambar 1936. Sa'annan East ɗin zai wuce zuwa Binuwai domin aikin littafin Tibi da ake yi, shi ma kuma zai ɗauki shi watannin Janairu da Fabrairu. Domin kada gwamnati ta ɗauka cewa Hukumar Fassara ba ta son yin aikin ne, sai ya ba da shawara ta ya tura

Malam Tafida na ofishin hukumar da ke can Kaduna ya yi aikin fassarar tare da jami'in mulki. NAK/ADN/767/Vol.3/314,(1936).

Wannan cece-ku-ce tsakanin hukumomin gwamnati game da yanayin aikin Hukumar Fassara shi ne ya jawo aka fara tunanin cewa lallai a nemi mafita game da irin aikin da hukumar ke yi. Ga dai aikin fassara ya taru ba mai yi, ga kuma ayyukan da ba na fassarar ba sun maƙure hukumar, waɗanda kuma da alama su ne suka hana hukumar yin aikin fassarar da aka kafa ta domin shi.

A ranar 24 ga watan Oktoba na 1936, dole ta sa East ya rubuta doguwar wasiƙa zuwa ga shugabanninsa da ke Kaduna domin ya bayyana yadda za a magance matsalar. Da farko dai ya fara da kawo shawarwarin da wasu suka kawo game irin aikin da hukumar take yi. Daga cikin irin waɗannan mutane akwai Abubakar Imam wanda hukumar ta aro daga Lardin Katsina domin ya taimaka wajen rubuta littafin Magana Jari Ce a shekarar 1936. An dai ba da aron Abubakar Imam daga ranar 21/5/36 zuwa 19/11/36, Malumfashi (2009). Ko da Imam ya iso ofishin ya fahimci cewa sunan hukumar bai dace ba, an dai rubuta Ofishin Fassare-Fassare ne, alhali kuwa shi aikin talifi ya zo yi. A dai wannan zama na Abubakar Imam ne ya ƙara lura cewa ayyukan hukumar kacokam ba na fassara ba ne kurum, kai da alama ma ba fassarar take yi ba, sai wasu ayyuka na talifi da tarihe-tarihe. Wannan da wasu dalilai suka sa ya nemi East da ya dubi sunan nan da kyau, a sama wa hukumar sunan da zai dace da ita. Za mu ga yadda wannan batu ya kaya a ƙarshen wannan babi, amma kafin nan bari mu dubi wasu dalilan da suka ƙara taimakawa wajen canza wa hukumar Fassarar suna.

Idan aka ce lallai wuce-gona da iri shi ne musabbabin canza wa Hukumar Fassara suna ta koma ta Talifi to da alama ba a yi adalci ba. Wannan ya faru ne ganin cewa ita kanta Hukumar Fassara da farko ba ta da wani matsayi na musamman, da yake ba a kafa ta bisa tsari ba. Hatta kuɗaɗen gudanar da ita da farko suna zuwa ne daga cikin kuɗaɗen da aka ware wa makarantar ɗan Hausa, inda ta fara zama. Ma'aikatan hukumar kuma suna daga cikin malamai ko jami'an kula da ilmi na Arewacin Nijeriya. Abin da kila za a iya cewa shi ne, har zuwa shekarar 1932 lokacin da R.M.East ya haye karagar shugabancin hukumar ba wani tallafi daga gwamnati.

Hakan na iya zama gaskiya ganin cewa "ko da aka kafa mulkin mallaka na ƙasar Birtaniya a sassan Afirka da dama gwamnati ba ta bayar da wani tallafi domin gudanar da ilmi ga 'yan ƙasa ba." Kamar yadda Ellerman (1994) ya nuna a cikin binciken Malumfashi da Ahmad, (2007). An sha kai-kawo game da yadda za a ba da kuɗi domin tallafa wa ilmin 'yan ƙasa, amma ba a cimma nasara ba sai a 1929, a lokacin da gwamnatin Birtaniya ta fara aiko da kuɗin tafiyar da harkar ilmi. Sai dai

shi ma wannan taimako kamar rance ne, domin gwamnati ba ta amince ta sa kuɗi kan harkar ilmin ‘yan ƙasa ba, wanda take ganin tamkar hasara ne.

Saboda haka ana iya cewa, Hukumar Fassara da ma ita kanta makarantar ɗan Hausa ba su samu goyon bayan gwamnati ba sai daga baya. An riga an ga bayanin da ke nuni da cewa ko da ɗan Hausa ya buɗe makarantarsa a Kano a 1909 zuwa 1910, kuɗaɗen gudanar da makarantar daga baitulmali suke zuwa. Ke nan ba abin mamaki ba ne idan ita kanta Hukumar Fassara ta kasance tana amfana daga wannan kaso.

Daga wannan ne aka fahimci cewa, aikin fassara shi ya ba da damar a koya wa ‘yan ƙasar harkar talifi domin a samar da ayyukan talifi daga ‘yan ƙasa. Hukumomin da ‘yan Mishan suka kakkafa irin na fassara da kwamitocin talifi da rarraba ayyukan adabi, su ne ake ganin sun zama ginshiƙin wadatuwar da aka samu na ayyukan talifi.

Dangane da haka za a iya cewa, hukumomin talifi da aka samar a sassan Afirka sun taimaka wajen gina ‘yan ƙasa domin su iya talifi irin wanda Turawa ke buƙata. Da zarar aka ce an koya wa mutane hanyar samar da littattafai aka kuma samu masu saye da karantawa, ba abin da ake buƙata, domin tsarin zai ci gaba da gudanar da kansa. ‘Yan mulkin mallaka sun naƙalci wannan fasali, sa’annan suka ci gaba da gudanar da shi, tare da bayar da agajin kuɗi da kayan aiki daga shekarar 1938, Ellerman (1994). Wannan shi ne musabbabin shigowar gwamnatin mulkin mallaka kai tsaye wajen kafa hukumar talifi a Arewacin Nijeriya. Abin la’akari shi ne, tun asali an shirya kafa hukumomin talifin ne a inda ba a da tsarin ilmin zamani ko na Turawa a wurin. To amma a Arewacin Nijeriya ba haka abin ya kasance ba, domin an riga an fara kafa Hukumar Fassara da ayyukan talifi na ‘yan Mishan da tuni suka yi kaka-gida, saboda haka ita Hukumar Talifin daga baya ne ta samu, ba wai wata sabuwa ba ce kamar yadda yake a wasu ƙasashe.

### 3.3.3 Hukumar Gaskiya Da NORLA Da NNPC

Rushe Hukumar NORLA a 1960 ya sa aka danƙa wa Kamfanin Gaskiya dukkan abubuwan da ta mallaka, aka kuma ɗora masa ayyukan da take gudanarwa. A wannan lokaci aka buɗe wani sashi a ƙarƙashin kamfanin don gudanar da ayyukan wallafa da kuma tallar littattafai. Kamfanin ya ci gaba da gudanar da ayyukansa har zuwa wani lokaci.

To amma da tafiya ta fara nisa, sakamakon wancan nauyi da aka ƙara wa kamfanin, sai wasu matsaloli suka fara dabaibaye shi. Waɗannan matsaloli sun haɗa da ƙarancin ƙwararrun ma’aikata da rikice-rikice tsakanin ma’aikatan da shugabannin kamfanin da rashin ingantattun

kayan aiki, ga rashin ciniki, ga kuma uwa-uba ƙarancin kuɗi. Sannan a 1965, aka sake toshe wa kamfanin wata hanyar samunsa, wato aka ɗauke buga jaridun Gaskiya Ta Fi Kwabo da ta 'New Nigerian' zuwa sabon kamfanin da aka kafa mai suna 'New Nigerian Newspapers Limited', a Kaduna. Waɗannan abubuwa da suka taru, su suka sa Kamfanin Gaskiya ya kasa sauke nauyin da ke kansa.

Ana cikin wannan hali ne kuma sai firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato, ya kawo wa kamfanin ziyara. A lokacin ziyarar aka sanar da shi halin da ake ciki, aka kuma ba shi shawarar cewa lallai ya kamata a nemi gudummuwar waɗanda suka ƙware kan harkar wallafa da tallar littattafai don farfaɗo da kamfanin.

Daga nan sai Sir Ahmadu Bello ya  tura wakilansa ƙarƙashin jagorancin ministan harkokin cikin gida na Jihar Arewa, Alhaji Kabir Umar, Chiroman Katagum, da su tafi Ingila domin nema wa Kamfanin Gaskiya wani kamfanin da za su haɗa gwiwa da shi don gudanar da harkar wallafa littattafai. Waɗannan wakilai sun sadu kuma sun tattauna da manyan kamfanoni guda biyu da ake ji da su kan lamarin. Waɗannan kamfanonin kuwa su ne kamfanin wallafa littattafai na Macmillan da kuma kamfanin Edward Arnold and Sons.

Abin da waɗannan masu ziyara suka ji kuma suka gani dangane da kamfanin Macmillan na irin shahararsa a duniya da irin kayan aikinsa ya ba su sha'awa matuƙa. Don haka sai suka ba da shawarar da a gayyace shi ya zo domin haɗa gwiwa da Kamfanin Gaskiya don samun biyan buƙatar abin da ake nema. Wannan ita ta buɗe kafar tattaunawar da ta gudana tsakanin Kamfanin Gaskiya, a madadin gwamnatin Jihar Arewa, a gefe guda, da kuma kamfanin Macmillan a ɗaya gefen. Nan take kuma wannan shahararren kamfani ya ba da shawarar cewa a ware ~angaren wallafe-wallafe daga cikin ayyukan da Kamfanin Gaskiya ke gudnarwa.

A ranar 21 ga watan Okotoba na shekarar 1966 aka ƙulla yarjejeniya[2] tsakanin wannan baƙon kamfani na Ingila da kuma Kamfanin Gaskiya. Sakamakon hakan shi ya haifar da Hukumar Wallafa Littattafai ta Arewacin Nijeriya, wadda da Turanci ake kira 'Northern Nigerian Publishing Company limited', wato NNPC.

A cikin wannan yarjejeniyar an nuna cewa Kamfanin Gaskiya shi ke da jari mafi tsoka, inda ya mallaki kashi 51 cikin ɗari, yayin da shi kuma kamfanin Macmillan ya tashi da kashi 49 cikin ɗari na jimillar abin da aka zuba cikin wannan sabuwar hukuma. Daga nan sai aka ware wa hukumar NNPC ofisoshinta don gudanar da ayyukanta a gefe guda daga cikin makeken ginin Kamfanin Gaskiya, da ke kan titin da ake kira 'Gaskiya Road' a Tudun Jukun da ke Zariya. Hukumar ta naɗa marigayi Alhaji Salihu Kwantagora editanta na farko, a ranar 1 ga watan Afrilu na

shekarar 1967. Manajanta na farko kuwa shi ne Mr. John Hare, wanda ya riƙe hukumar daga 1967 zuwa 1969.

Kamar kuma yadda yarjejeniyar da aka ƙulla ta tanadar, hukumar za ta ci gaba da wallafa littattafai da kuma tallarsu. Sannan waɗannan kamfanoni biyu da suka mallake ta za su ci gaba da tallafa mata don ganin cewa ta zauna da gindinta. Misali, ta ~angaren Kamfanin Gaskiya, ko baya ga ofisoshin da ya bai wa hukumar, ya kuma ba ta wasu kayan aiki da kuma ma'aikata, haɗe da biyan albashinsu. Sannan kuma kamfanin ya bai wa hukumar haƙƙin mallakar littattafansa na adabin Hausa waɗanda aka ƙiyasta sun kai sama da ɗari biyu da sittin. Yayin da shi kuma kamfanin Macmillan ya ɗauki nauyin tura ma'aikatan hukumar zuwa ofishinsa da ke Ingila don ƙaro sanin makamar aiki. Sannan kuma kamfanin ne zai ɗauki ɗawainiyar rarraba da kuma tallar littattafan hukumar a ko'ina cikin duniya.

A tsawon shekaru arba'in ɗin da Hukumar NNPC ta yi da kafuwa, ta wallafa sababbin littattafai da dama a bisa kan waɗanda ta gada daga Kamfanin Gaskiya. Hukumar ta rinƙa samun sababbin marubutanta ne daga malaman jami'o'i kamar ta Ahmadu Bello da ke Zariya da ta Bayero da ke Kano da sauran su, waɗanda kan kawo aikinsu, a ƙulla yarjejeniya, a wallafa, a sayar. Wasu ayyukan kuma kan zo wa hukumar ne daga ma'aikatun ilmi da makarantu manya da ƙanana daga sassa daban-daban na jihohin Arewa. Sannan hukumar har-ila-yau, kan ba da ƙwarin gwiwa ga sauran marubuta kan adabin, kamar kan ƙagaggun labarai da waƙoƙi da wasan kwaikwayo da ma marubuta kan harkokin tattalin arzikin ƙasa da siyasa da sauran fannoni don su ma su ba da tasu gudummuwar wajen wadata jama'ar Arewa da ma ƙasa baki ɗaya da abin karantawa.

**Auna Fahimta**

Domin fahimtar ko darasin ya zauna sai ɗalibai sun fayyace abubuwa kamar haka:

1. Wacce irin rawar Hukumomin Inganta Adabi suka taka wajen tabbatuwar rubutun zube?
2. A wacce rana aka ƙulla yarjejeniya tsakanin baƙon kamfanin Ingila da kuma Kamfanin Gaskiya wanda ya haifar da Hukumar Wallafa Littattafai ta Arewacin Nijeriya, wadda da Turanci ake kira **'**Northern Nigerian Publishing Company limited' NNPC?

## 3.4 Kammalawa

{oƙarin wannan darasi shi ne ya bayyana cikin tarihi yadda aka samar da rubutattun labaran farko da cikakken bayanni kan gasar 1927 da 1929 da

1933 da kuma tattauna littafin farko da ya fito, wato Fatima da dalilin samar da shi.

## 3.5 Taƙaitawa

Darasin ya gabatar mana da abubuwa ne da suka haɗa da:

- Bayani game da samuwa da wanzuwar rubutun zube na Hausa a ƙarƙashin kulawar wasu hukumomi a farkon rayuwa.
- Gudummawar da Hukumar Fassara da ta Talifi suka bayar a farkon rayuwa
- Rawar da Hukumar Gaskiya Da NORLA Da NNPC suka taka wajen samar da rubutun zuben Hausa

**Jingar Aiki**

1. Yi taƙaitaccen bayani game da Hukumar Fassara.
2. Me ya faru a tsakanin Hukumar Fassara da ta Talifi a 1932 zuwa 1937?
3. Da Gaskiya da NORLA da NNPC duk abu ɗaya ne! Tattauna.

## 3.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari


Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language. London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory. Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari). Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce, Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982); “Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa.’ Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009). Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd

Malumfashi, I. (2019); Labarin Hausa A Rubuce: 1927-2018. Zaria: ABU Press and Publishers

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce Cikin Hausa**. Zariya:** NNPC bambadiya.blogspot.com

www.rumbunilimi.com.ng

### 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1 Wacce irin rawa Hukumomin Inganta Adabi suka taka wajen tabbatuwar rubutun zube?

Fassara littattafai daga wasu harasan zuwa Hausa, samarda Labarun Da da na Yanzu da wasu domin samar da ƙagaggun labarai don koyarwa da nishaɗantarwa domin amfani a makarantu.

2. A ranar 21 ga watan Okotoba na shekarar 1966

## Kashi Na 4 Shekarun 1980 Da Samuwar Sabon Fasalin Rubutu

### Tabbatuwar Rubutun Zube

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Shekarun 1980 Da Samuwar Sabon Fasalin Rubutu
4.3.1 Gasar Shekarar 1978
4.3.2 Gasar Shekarar 1980
4.3.3 Bayyanar Sabon Yanka Rake Na Rubutun Zube
4.4 Kammalawa
4.5 Taƙaitawa
4.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari
4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 4.1 Gabatarwa

A kashin da ya gabata an yi nazarin irin rawar da hukumomin inganta adabi suka bayar don samar da kuma inganta rubutun zube na Hausa. Wannan kashin zai duba tarihin yadda aka samar da rubutattun labaran Hausa a shekarar 1978 da 1980 da 1933 da kuma tattauna yadda littattafan da aka kira 'yan zamani suka bayyana.

### 4.2 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi za a fahimci tarihin yadda aka samar da rubutattun labaran Hausa a shekarar 1978 da 1980 da 1933 da kuma yadda littattafan da aka kira 'yan zamani suka bayyana.

### 4.3. Shekarun 1980 Da Samuwar Sabon Fasalin Rubutu

Abin kula daga farko shi ne a fahimci cewa shekarun 1960 sun kasance na samun 'yancin kai da juyin mulki da kuma yaƙin basasa. Ma'ana a cikin shekarar 1960 Nijeriya ta samu 'yancin kanta, saboda haka labaran zube da suka famtsamo daga wannan lokaci za a ga suna da sifofin ƙwatar 'yanci da kishin ƙasa da kuma gwagwarmayar rayuwa bayan samun mulkin kai. Saboda haka, ba abin makaki ba ne marubuta su yi amfani da wannan dama su kalli rayuwar al'ummarsu ta wannan lokaci.

Da kuma aka yi juyin mulki a shekarar 1966 aka kashe 'yan siyasar farko na Arewacin Nijeriya, sai abubuwa suka canza a farfajiya da tunanin al'ummar wannan yanki. Da kuma aka yi rikicin A-Ware bayan

juyin mulki a arewacin Nijeriya, wanda ya jawo sake yin juyin mulkin Gowon sai al'amurra suka canza fasali. Wannan shi ya jawo rikicin Nijeriya da ya kai ga yaƙin Basasa daga 1967 zuwa 1970. Wannan taƙaddama da ta faru za ta yi tasiri a rayuwar al'ummar Arewa da kuma musamman marubutanta. Dangane da haka ba abin mamaki ba ne idan labarun zuben da da aka rubuta a wannan tsakani ko kuma waɗanda suka biyo su suka kasance masu ɗauke da wannan ruhi na rikice-rikice da faɗace-faɗace da halbe-halbe da kuma siyasa irin ta kishin kasa. Alal misali labarai irin Kitsen Rogo na Abdulkadir ɗangambo da {arshen Alewa {asa na Bature Gagare da Za~i Naka na Munir Mohammed Katsina, suna ɗauke da irin wannan fasali.

Haka kuma, rayuwar da ta shafi ginuwar tattalin arziki da ilmin boko da zamantakewar yau da kullum ta wannan zamani ta taimaka wajen samuwar wasu rubutattun zube. Ma'ana, yadda aka samu gara~asar man metur daga farkon shekarun 1970 da yadda kuma aka ga ~ullar ɗalibai masu tarin yawa daga shirin UBE na 1976, wanda ɗaliban farko suka antayo cikin al'umma da ƙishirwar son karatu da kuma ~ullar kayan kallo irin na talbijin da bidiyo a daidai wannan lokaci shi ma ya ƙara sa wa marubuta ƙaimi na rubutun zube, musamman daga rayuwar da suka tsinkaya. Labarai irin su So Aljannar Duniya da Tauraruwar Hamada da Tauraruwa Mai Wutsiya da Turmin Danya da wasu da dama bisa wannan tafarki suka wanzu. A ciki ne za a ga rayuwar sumogal da soyayya da ilmin zamani da yanayin zamantakewar al'umma baki ɗaya. Saboda haka, duk yadda aka so ba zai yiwu ba a canza tunanin marubuci daga abin da ya riska ko ya riske shi ko kuma tsinkayar yadda lamurra za su kasance a cikin labaran da yake rubutawa.

### 4.3.1 Gasar Shekarar 1978

A fagen samar da littattafai tsugune ba ta ƙare ba, domin hukumar nan mai kula da harkokin bugawa tare da samar da littafai mallakin jihohin Arewa watau NNPC Zariya, ta sake ~ullo da wata gasa a fagen rubutun ƙagaggun labarai a cikin shekarar 1978. Marubuta da dama suka shiga wannan gasa daga wurare daban-daban. Kimanin marubuta takwas suka yi nasara har aka za~i littattafansu kuma aka yi masu kyaututtuka. Ya zuwa wannan lokaci kamfanin ya buga littatafai uku ne kawai, waɗanda suka zo na ɗaya da na biyu da na uku a shekarar 1980 kamar haka:

| **Sunan Marubuci** | **Sunan Littafi** |
|---|---|
| Suleman Ibrahim Katsina | Mallakin Zuciyata |
| Hafsatu Abdulwaheed | So Aljannar Duniya |
| Magaji ɗanbatta | Amadi na Malam Ama |

Sai dai abin kulawa a nan shi ne, waɗannan littattafan jigoginsu sun bambanta da na farko irin su Ruwan Bagaja. Su waɗannan Littatafan

jigoginsu sun fi ta'allaƙa ne a kan turbar soyayya. Wannan ba ƙaramar bai wa matasa dama ya yi ba, sai suka zaburo zabura daga kowane lungu don ganin cewa sun taka muhimmiyar rawa wajen samar da littatafai da suka shafi soyayya. Wanda hakan ya yi jagora ya zuwa ga samar da littatafan da yanzu aka fi sani da Adabin Kasuwar Kano (Gusau 2009).

### 4.3.2 Gasar Shekarar 1980

A cikin shekarar 1980 ne, hukumar kula da nazarin ala'adu ta tarayya wadda ke da mazaunita a Legas ta yi wani ho~~asa na shirya sabuwar gasa kan ƙagaggun labarai a cikin harsunan Hausa da Igbo da Yoruba. Ita ma kamar sauran hukumomin, babbar manufarta ita ce tallafawa wajen samar da marubutan littattafan ƙirƙira na fasahar kansu, amma fasahar ta zama ~oyayya wadda ba a ta~a samun kamar ta ba. Har ila yau, wata manufar ta samar da waɗannan littattafai daga wannan hukuma sun haɗa da isar da saƙon gwamnatin tarayya na al'adun kowace al'umma a kan kowane fanni.

A kwana a tashi sai marubuta da dama suka ~ullo daga waɗannan harsuna guda uku ciki har da harshen Hausa. A cikin littattafan harshen Hausa guda bakwai da marubutan suka aika da su an za~i waɗanda suka taka rawar gani kuma aka wallafa su. Duk da cewa an gudanar da wannan gasa tun a shekarar 1980, amma ba a sami damar wallafa waɗannan littafai ba sai a shekarar 1982, (NNPC Zariya). Ga jerin littatafan da suka yi abin a zo a gani kuma hukumar ta wallafa kamar haka:

| **Sunan Marubuci** | **Sunan Littafi** |
|---|---|
| Suleman Ibrahim Katsina | Turmin Danya |
| Musa M. Bello | Tsumingiyar kan Hanya |
| Bature Gagare | {arshen Alewa {asa |
| Mannir M. Katsina | Za~i Naka |
| Hadi Abdullahi Alƙalanci | Soyayya Ta Fi Kuɗi |
| Bello Sa'id | Dausayin Soyayya |
| Yahuza Bello | Wasa {waƙwalwa |

(Gusau (2009).

### 4.3.3 Bayyanar Sabon Yanka Rake Na Rubutun Zube

Daga tsakiyar shekaru 1980 an ~ullar sababbin littattafan Hausa da dama, waɗanda suka sa~a da yadda aka saba gani a baya inda hukuma ce ke kula da lamurran. Yazu kuwa matasa ne suka kama saa'ar ruutu da karatu. Shigowar wannan tsari ne al'amurra suka canza, aka shiga samar da littattafai a maza da mata, masu ɗauke da jigogi da salailai

mababbanta. A wasu lokutta nmaza ke amfani da sunayen mata, a wasu lokutta kuma matan ne ke amfani da su waye maza.

**Auna Fahimta**

Domin fahimtar ko darasin ya zauna sai ɗalibai sun fayyace abubuwa kamar haka:

1. Me ya faru a shekarun 1980 da samuwar sabon fasalin rubutu?
2. Yaya aka gudaar da gasar shekarar 1978.
3. Bayani kan bayyanar sabon yankan rake na rubutun zuben Hausa.

## 4.4 Kammalawa

Wannan darasi ya bayyana tarihin yadda aka samar da rubutattun labaran Hausa a shekarar 1978 da 1980 da 1933 da kuma tattauna yadda littattafan da aka kira 'yan zamani suka bayyana.

## 4.5 Taƙaitawa

Darasin ya gabatar mana da abubuwa ne da suka haɗa da:

- Bayani game da shekarun 1980 da samuwar sabon fasalin rubutun Hausa.
- Yaya aka gudunar da gasar shekarar 1978
- Me ya faru a shekarar 1980
- Me ake nufi da sabon yankan rake na rubutun zube?

**Jingar Aiki**

1. Yi bayani game da gasar rubutu ta shekarar 1978.
2. Yaya aka gudanar da gasar shekarar 1980?
3. Me ya faru daga shekarun 1980 game da sababbin rubuce-rubucen Hausa?

## 4.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language. London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory. Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984). Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari). Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce. Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982). "Tasirin Adabin Baka A Kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa". Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009). Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd

Malumfashi, I. (2019). Labarin Hausa A Rubuce: 1927-2018. Zaria: ABU Press and Publishers

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa**.** Zariya: NNPC

bambadiya.blogspot.com

www.rumbunilimi.com.ng

## 4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. A shekarar 1980 hukumar kula da nazarin ala'adu ta tarayya ta shirya gasa kan ƙagaggun labarai a cikin harsunan Hausa da Igbo da Yoruba domin samar da marubutan littattafan ƙirƙira na fasahar kansu, samar littattafai don isar da saƙon gwamnatin tarayya na al'adun kowace al'umma a kan kowane fanni. An sami marubuta da dama daga waɗannan harsuna guda uku ciki har da harshen Hausa. A cikin littattafan harshen Hausa guda bakwai da marubutan suka aika an wallafa wasu daga ciki a shekarar 1982. Daga ciki akwai littafin Suleman Ibrahim Katsina mai taken Turmin Danya da na Musa M. Bello mai takenTsumingiyar kan Hanya.

2. Hukumar kula da harkokin bugawa tare da samar da littafai mallakin jihohin Arewa watau NNPC Zariya, ta sake ~ullo da wata gasar rubutun ƙagaggun labarai a cikin shekarar 1978. Marubuta da dama daga wurare daban-daban sun shiga gasar. Kimanin marubuta takwas suka yi nasara har aka za~i littattafansu kuma aka yi masu kyaututtuka. Kamfanin ya buga littatafai uku waɗanda suka zo na ɗaya da na biyu da na uku a shekarar 1980 kamar haka:

| **Sunan Marubuci** | **Sunan Littafi** |
|---|---|
| Suleman Ibrahim Katsina | Mallakin Zuciyata |
| Hafsatu Abdulwaheed | So Aljannar Duniya |
| Magaji ɗanbatta | Amadi na Malam Ama |

3. Wannan na nufin samin ~ullar sababbin littattafan Hausa da dama a tsakiyar 1980 daga matasa waɗanda suka sa~a da yadda aka saba gani a baya inda hukuma ce ke kula da lamurran amma a yanzu matasa ne suka kama saa'ar rubutu da karatu. A dalilin haka aka samar da littattafai da maza da mata suka wallafa masu ɗauke da jigogi da salailai mabambanta. A wasu lokutanma maza ne ke amfani da sunayen mata ko mata su yi amfani da sunayen maza.

## RUKUNI NA 4

Kashi na 1 mene ne adabin kasuwar kano?
Kashi na 2 ci gaba da wanzuwar rubutaccen zuben hausa
Kashi na 3
Kashi na 4

### Kashi na 1 Mene Ne Adabin Kasuwar Kano?

**Tabbatuwar Rubutun Zube**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Mene Ne Adabin Kasuwar Kano?
 1.3.1 Bayani Game Da Adabin Kasuwa
 1.3.2 Bayani Game Da Adabin Yayi
 1.3.3 Taƙaitaccen Bayani Game Da Adabin Kasuwar Kano
1.4 Taƙaitawa
1.5 Jingar Aiki
1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 1.1 Gabatarwa

Darasin da ya gabata an bayyana tarihin yadda aka samar da rubutattun labaran Hausa a shekarar 1978 da 1980 da 1933 da kuma tattauna yadda littattafan da aka kira 'yan zamani suka bayyana. Wannan darasi sai yi nazarin Adabin Kasuwar ke nufi da Adabin Kasuwa da na Yayi, sa'annan an yi taƙaitaccen bayani game da Adabin Kasuwar Kano

### 1.2 Manufar Darasi

- A wannan darasi za a fahimci abinda ake nufi da Adabin Kasuwa
- da Adabin Yayi da kuma Adabin Kasuwar Kano.

### 1.3 Mene ne Adabin Kasuwar Kano?

Kamar yadda muka sani rayuwar adabin Hausa ta biyo zanguna mabambanta. Wannan ba sai an yi dogon sharhi ba, domin kuwa daga tashin Hausawa na zaman gargajiya har zuwa lokacin da suka cuɗanya da baƙi an sami sauye-sauye da adabin Hausawa ya yi, ko dai ta fuskar

sauyawar riga daga ta gargajiya zuwa ta zamani (Larabci ko Ingilishi ko Faranshi) ko kuma ta sauyawar kayan cikin adabin saboda haɗuwa da sababbin ladubban rayuwa .

Irin sauye-sauyen da aka samu daga gargajiya zuwa zamani abu ne da masana suka sha ambaton sa. {ila abin da ba a fi mayar da hankali kai sosai ba shi ne yadda gwamutsuwa da baƙin al'amurra ke haifar da sababbin batutuwa da ke bukatar ƙara bincike da nazari. Batutuwan da suka yi tashe a cikin 'yan shekarun nan, musamman abin da ya shafi ƙagaggun labaran Hausa, bai wuce batun nan na Adabin Kasuwar Kano ba, wato littattafan da yawancinmu ke kira Labaran Soyayya da suka tuzgo daga sassa daban-daban na ƙasar Hausa da ke hedikwata a birnin Kano.

Samuwa da watsuwa ko kuma kar~uwa da kuma ce-ce-ku-ce da wannan sabon salon adabi ya samu kansa a ciki, tsakanin marubuta da manazarta da masana a ƙasar Hausa da ma sassan duniya daban-daban ya jawo ayyukan nazari da musayar miyau mai tarin yawa.

Abin da za mu yi ƙoƙarin yi a nan shi ne shimfiɗa tabarmar nazari game da wannan fage ta hanyar neman sanin yadda adabin kasuwa yake ta hanyar tambayar ko akwai wani abu wai shi adabin kasuwa? Idan akwai shi to yaya yake? Shin ana iya samun sa a ƙasashe masu tasowa kamar Nijeriya? Ko kuwa dai wanda ake da shi da ake kira Adabin Kasuwar Kano, an sa masa sunan ne domin cin mutunci da ~atunci ko son rai? Abin da za mu sa gaba bai wuce amsa waɗannan tambayoyi da ma wasu da ka iya biyo baya ba. Ta haka ƙila haske ya ƙaru game da wannan fage na tarihin adabi da zai bayyana mana bambancin da ke tsakanin adabi na zahiri da wanda ake kira na kasuwa da kuma yadda irin fasalin ya samu ginuwa a ƙasar Hausa.

### 1.3.1 Bayani Game Da Adabin Kasuwa

A duk lokacin da aka soma batun da ya shafi Adabin Kasuwa abubuwa da dama ke zuwa zuciyar mai nazari, ciki kuwa har da tunanin nan da ke nuni da cewa idan har akwai adabin kasuwa to akwai wani adabin da ba na kasuwa ba. Idan kuma ka ɗauki ma'anar Adabin Kasuwa a luggance da ke nufin adabi na kowa da kowa ko na yayi ko abin da ke jan hankalin jama'a a kodayaushe, to ana iya cewa akwai adabin da ke da akasin haka. Ma'ana, adabin da ba na kowa da kowa ba, adabin manya, masu ilmi ko sarauta ko daraja a tsakanin al'umma. A taƙaice dai adabin da ke shimfide a wani wuri domin manazarta da masana ko kuma wanda fagensa ba na kowane ɗan tagaja-tagaja ba ne wajen saye da karantawa da nazari, wato abin da ake wa lakabi da gangariyar adabi. Saboda haka, ƙoƙarinmu a nan shi ne mu bambanta tsakanin gangariyar adabin da

wanda ake wa laƙabi da na kasuwa, domin ta haka ne za a gane yadda tunanin samuwar Adabin Kasuwar Kano ya tusgo, yake kuma gudana.

Adabi dai kamar yadda masana suka yi nuni, kundi ne ko hoto ko madubi, (dubi Dangambo, 1984, da Gusau, 1995 da Malumfashi, 2002) da ke ɗauke ko nuna hanyar gudanar da rayuwar al`umma. Za a iya fahimtar irin wannan adabi ta yin la`akari da abubuwa guda biyu; na farko shi ne harshen da ake amfani da shi, wanda yake maƙunshin tarihi, kuma linzamin bayyana tunani ko kuma wata manufa. Na biyu kuma ita ce fasaha, wadda ita ke bayyana tunanin da ke cikin zuciya a aikace, kamar yadda Muhammad, (2001) ya bayyana.

Shi kuma Cuddon,(1999) da yake ƙoƙarin fitar da ma'anar adabi a luggance cewa ya yi, adabi na iya kasancewa abubuwa da dama da suka haɗa da wasan kwaikwayo da waƙa da gajerun labarai da rubutattun litattafai da dai sauransu. Ya ci gaba da cewa idan har aka ce wannan aikin adabi ne, to makunshiyar aikin ta bambanta da sauran kwashe-kwashe na yau da kullum, musamman idan abin ya shafi gaskiyar lamari ko kuma faɗar tarihi. Ke nan adabi yana da wasu siffofi da suka bambanta shi da wasu ayyuka da ba su da tasiri irin nasa. Duk da haka, akwai ayyuka ko rubuce-rubuce da dama waɗanda ba a yi su don su kasance na adabi ba, amma kuma za a iya sanya su cikin aikin adabi; saboda ingancin aikin da asalinsa ko kuma irin kyawo da kuma fasahar da aka nuna wurin rubuta shi, kamar yadda Cuddon, (1999) ya nuna.

Daga wannan hasashe za a iya cewa adabin da ke da waɗannan siffofi da aka ambata a sama, shi ne ke kasancewa gangariyar adabi, akasin haka kuma sai ya zama wani abin, ƙila ma na kasuwa ko kuma gwanjo ko makamancin haka.

Kamar yadda kowane sashe na duniya yake da gangariyar adabi, to haka a wasu sassan duniya ake da adabin kasuwa (Market Literature) ko kuma adabin yayi (Popular Literature). To amma idan muka ce adabin kasuwa, nan zai iya kasancewa na yayi, domin kuwa duk abu ɗaya suke tattaunawa. Duk abin da ya kasance na kasuwa to yana da alaƙa da yayi. Kasuwa dai wuri ne da ake saye da sayarwa na dukkan abubuwan rayuwa. Duk wanda ke cikin wannan al`umma yana iya zuwa cikin kasuwa domin yin kasuwancinsa. Saboda haka, adabin kasuwa wani ~angare ne na adabin al'umma da kowa zai iya shiga cikin kogin ya yi iyo ko kurme, masani ko malami ko manazarci ko akasin haka. Ke nan irin wannan adabi wani abu ne ko dai waƙa ko wasan kwaikwayo ko ƙananan labarai, ko rubutattaun litattafai da aka tsara a wani zangon rayuwar jama'a, ake kuma tsintar su a tsakanin jama'ar ba tare da wani kandagarki ba. Ta fuskar sayar da su ba a yi wani tanadi na wurin da ya dace ba, ko dai a same su a kasuwa ko wurin hirar matasa ko tsakanin matan aure ko makarantu ko kuma ma duk inda jama'a ke tururuwa

domin karatu da rubutu. Haka kuma, idan aka ce adabi na yayi ne, ana nufin cewa zai rayu daga wani lokaci zuwa wani, wato akwai lokacin da yake tashe, akwai kuma lokacin da yake sallacewa, sai a bar masana da yin rubdugu kansa, Malumfashi (2002).

Sai dai ya kamata a lura cewa akwai kuma lokutta da ake kallon irin wannan adabin na kasuwa ko yayi a matsayin adabin talakawa ko marasa shi. Wato ya ke~anta ne ga wasu gungun jama'a a cikin wani zamani da ba su damu da adabin da ke gudana ba, ƙila ko don ba su da kuɗin sayen sa ko kuma ya kasance na masu gari ne. Idan aka faɗaɗa tunani a nan, za a ga cewa shi wannan adabi na kasuwar ko yayin, canzawar zamani ce ta sa ake yi masa wani sabon kallo, musamman da yake ba a damu sosai da yi masa gangariyar nazari ba. Kai ba wannan ba ma, ai masana da dama ba su ɗauki aikin adabi irin wannan abin toƙabo ba, shi ya sa ba a damu da sanin inda ya sa gaba ba. Sai dai ko da aka soma nazarin nasa daga baya, an kuma shigo da ayyukan adabi da mutum na iya cewa ba irin na adabin kasuwa ko yayin da aka saba ji da gani ba ne.

A halin yanzu, daga cikin ayyukan adabin kasuwa ko na yayi da ake da su an sanya irin ƙagaggun labaran da a da ba su cikin irin wannan rukuni, wato irin waɗanda suka haɗa da labaran bincike ko tsafi ko na ban tsoro ko soyayya ko na Amurkawan dauri ko na ban dariya ko kimiyya, wato dai ƙagaggun labarai da milyoyin jama'a ke saye da karantawa a sassan duniya daban-daban ko da kuma ba a nazarin su a ajin adabi ko jami'o'i, musamman daga shekarun 1930. Har yau taƙaddama ba ta ƙare ba dangane da ko waɗannan irin ayyukan adabi gangariyar adabi ne ko kuma kwamacala ne. Ga masana, kamar yadda aka bayyana a (eNotes.com), irin wannan aikin adabi na kasuwa bai da nasaba da aikin ƙwarai. Ana nuni da cewa dabara ce kurum ta samun kuɗi da suna, amma ba adabin da za a ta da jijiya wajen karatu ko nazari ba ne.

### 1.3.2 Bayani Game Da Adabin Yayi

Daga nazarin da aka gudanar, an fahimci cewa adabin kasuwa ko na yayi yana tafiya ne kafaɗa da kafaɗa da gangariyar adabin al'umma. Shi gangariyar adabin yana kasancewa tsakanin masu ilmi ko hannu da shuni ko kuma iyayen ƙasa. Duk wani abu da ba na wannan gungun mutane ba, yawanci shi ake wa laƙabi da adabin kasuwa ko yayi. Alal misali, kusan duk yawancin ayyukan adabi da suke da wannan siffa a Turai ko Amurka ko sauran sassan duniya, an samar da su ne tsakanin ƙarni na 16 da 17 da na 18, daidai lokacin da fasahar dab'i ko buga littattafai ta yi tashe a duniya. Kamar yadda bayanai suka yi nuni, yawancin jama'a da masana idan ana maganar adabin ƙarni na 16 da 17 da na 18, ana maganar gangariyar adabi ne ko na masu ilmi ko mulki ko

dukiya, amma ba su kaɗai ne suka kwashi nasu kason ba daga rayuwar adabi, akwai adabin talakawa ko na kasuwa, wato na kowa da kowa. Ma'ana, an samar da adabin da aljihun talaka zai iya biya ya saya don karantawa. Wannan dama ta samu ne domin an samar da injinun buga littattafai na bakin hanya da suka ba talaka damar ya sami gurbin da zai buga nasa adabin. Ire-iren waɗannan ayyukan adabin su ne ake ba sunaye daban-daban da suka haɗa da Grub Street Literature ko Chapbooks. Waɗannan laƙabobi sun wanzu ne saboda la'akari da irin yadda aka samar da adabin ko wuraren da ake samar da littattafan ko kuma yanayin bugawa da sayar da su. Su dai Grub Street Literature su ne ayyukan adabin da aka samar daga wuraren buga littattafai da ke kan Titin Grub a Landon. Da yake a tsakanin ƙarni na 16 da 17 da na 18 an samar da marubuta na ƙwarai, sai dai rubutun nasu ya fi mayar da hankali ne ga masu-fada-a-ji, bai ta'allaƙa ga sauran jama'a ba, ga shi kuma sun fi sauran jama'ar yawa. Wannan ya sa aka shiga neman wasu da za su agaza da nasu rubutun. Sai dai yawancin irin waɗannan marubuta ba su da sanayya ta zamani game da fasahar rubutu da ƙaga labarai, shi ya sa idan sun yi rubutu ake biyan su kuɗaɗe kaɗan, wannan ya sa suke rayuwa a cikin talauci da ƙunci. Shi kansa inda suke zama a bakin titin domin yin aikin nasu na adabi, wuri ne na ƙazanta da yawan lalata da tashin hankali, nan ake samun ~arayi da mabarata da dai ire-irensu, nan ne marubutan da injinan buga ayyukansu suka ɗaura aure.

Su kuwa Chapbooks littattafai ne da ake wa laƙabi da littattafai masu arha, su ne ayyukan adabin da suka kasance na yayi ko na jama'a a karo na farko a wancan zamani na ƙarni na 17 da 18. Ba ruwansu da kamfanonin hukuma ko na gwamnati, ba kuma ruwansu da manyan kamfanonin ɗab'i da ke neman ƙazamar riba. Ana kuma shiryawa da buga irin waɗannan littattafai domin isar da saƙo ga talakawa ko masu sha'awar adabi, amma ba su da kuɗin sayen gangariyar adabin da ke wanzuwa a lokacin. Wannan damar ce marubutan da masu karatu ke amfani da ita domin su isar da saƙo ga sauran jama'a ba tare da kamfanin ɗab'i ya sa baki ba. Yawancin abubuwan da ake samarwa sun haɗa da waƙe-waƙe da labarai da ayyukan addini da saƙonnin siyasa da makamantansu.

Tarihi ya nuna cewa, ko da hada-hadar ɗab'i da rubuce-rubuce ta kankama daga ƙarni na 15 da na 16 akwai ire-iren waɗannan ayyuka masu arha. Yawancinsu sun fita kasuwa ne daga ƙarni na 17 da na 18 a Ingila, kuma an nuna cewa sun kai ƙoƙoluwa ne a shekarar 1775, ta yadda ake samar da littattafai sama da 200,000 a kowace shekara.

Waɗannan littattafai sun taimaka wajen raya ayyukan adabin Ingila a wancan lokaci, sun sanya son karatu ga waɗanda ba su yi nisa a karatun ba, ko suka yi karatun suka watsar daga baya. Yawancin waɗannan littattafai ba su da yawan shafi, ba a yi musu bugun ƙwarai, sa'annan ana

sayar da su da arha daga wannan titi zuwa wancan, a maimakon wuraren da aka tanada domin sayar da gangariyar adabi. Domin ganin yadda wannan fasali ya kasance, bari mu dubi yadda na zamanin Elizabeth yake a Ingila.

### 1.3.3 Taƙaitaccen Bayani Game Da Adabin Kasuwar Kano

Daga abubuwan da aka gani a babin da ya gabata, ba abin mamaki ba ne idan aka ci karo da Adabin Kasuwa a Amurka ko Turai ko Rasha ko cikin ƙasashen Asiya ko Larabawa, kai ko ma ina ne a cikin duniya. Hakan na faruwa ne ganin cewa ai ba ƙasashen Turawa ko waɗanda suka ci gaba ne ke da damar su samar da adabin kasuwa su kaɗai ba. Haka kuma, ba dole sai harshen Ingilishi ko wani harshen da ya sami ci gaba kaɗai ne zai iya samar da shi ba. Kowace kasa, kuma kowane irin harshe zai iya samun adabin kasuwa a cikin wani zangon rayuwar adabin. Domin inganta bincike, ya dace mu bi salsala, mu ga yadda aka samar da abin da yawanci ake kira Adabin Kasuwar Kano tsakanin Hausawa.

Abin da aka daɗe ana kira Adabin Kasuwar Kano ya samo asali ne a farkon shekarun 1980, kuma wannan shekaru a ƙasar Hausa ko Arewacin Nijeriya baki ɗaya, shekaru ne masu tarihi a ~angaren samuwar ilmin boko da rubutu. A daidai wannan zangon rayuwa ne ɗaliban UPE (shirin gwamnatin tarayya da aka soma daga 1976 domin ba kowane yaro damar samun ilimin furamare kyauta), suka fara shiga kasuwar rubutu da karatu da rububin abubuwan karantawa. ɗaliban farko na wannan shiri sun baro firamare a shekarar 1982, daga wannan lokaci har zuwa 1984, an yaye ɗalibai har kashi huɗu. Saboda haka aka samar da sababbin makaranta da suke bukatar abin karantawa.

Haka kuma, wannan zango ya zo daidai da lokacin da babban kamfanin wallafa da ɗab'i a ƙasar Hausa wato NNPC ya soma shiga tasku, ya soma sukurkucewa da neman durƙushewa. A daidai wannan lokaci kamfanin NNPC ya daina buga littattafan hira da nishaɗi, bayan kuma ga dubban matasa da aka yaye daga shirin na UPE sun antayo cike da shauƙin irin waɗannan littattafai da babu su.

Wannan shiri na UPE, duk da cewa bai zaunu da gindinsa ba, amma ya samar da sababbin makaranta a farkon shekarun 1980. Kuma a daidai wannan lokaci sai ga shi tattalin arzikin Nijeriya ya ƙara inganta, saboda gano man fetur da aka yi, ya ƙara wa ƙasar hanyar samun kuɗaɗen shiga masu yawa. Bincike kuma ya nuna cewa duk lokacin da irin wannan harka ta kasance haka, wato ga masu ilmi gwargwado, sa'annan ga 'yan kuɗi a hannun jama'a, kamar yadda muka gani a fasalin Adabin Kasuwar Kitsch na Jamus, sai ka ga hanyoyin samar da adabi, mai kyau ko maras kyau suna wadatuwa. Da yake tun can azal akwai kayayyakin

rubutu da ɗab'i gwargwado a ƙasar Hausa, sai ya ba matasa damar da suka tsunduma cikin wannan harka ta wallafa littattafai ba ji ba gani, kamar yadda Furniss, (2001) ya yi nuni.

Tun kafin shekarar 1984 lokacin da littafin Rabin Raina na Talatu Wada Ahmed ya fito kasuwa, akwai ~ir~ishin rubuce-rubucen soyayya a ƙasar Hausa. Idan ba a manta ba, a shekarar 1978 kamfanin NNPC ya shirya gasa da ta samar da littattafai a shekarar 1980, kamar su Mallakin Zuciyata na Sulaiman Ibrahim Katsina da So Aljannar Duniya na Hafsat Abdulwaheed da kuma Amadi na Malam Amah na Magaji Dambatta, Haruna (2009). Sai dai abin lura shi ne, waɗannan littattafai daga gasa suka fito, wato sai da aka yi shiri da tsari, haka kuma na hukuma ko kamfani ne, don haka sun biyo tsari da ingancin da ya bambanta su da adabin kasuwa. Ke nan za a iya cewa, waɗannan littattafai na gasar 1978 sun nuna hanya ne na irin adabin da zai biyo bayansu, ba su ne farkon adabin na kasuwa a ƙasar Hausa ba.

A ɗaya ~angaren kuma, an danganta littafin Rabin Raina na Talatu Wada Ahmed da zama tushe ko tubalin samuwar adabin kasuwa a ƙasar Hausa, saboda yanayin da ya samu da kuma yadda ya shiga kasuwa. Shi ma ba wai zama aka yi badomin assasa wannan fage na adabin kasuwa tattare da shi ba.

Kamar yadda a karo na farko wadda aka danganta aikinta da Adabin Kasuwar Kano, Talatu ta bayyana wa Mujallar Garkuwa (2000) yadda ta samar da littafin. Ta ce ita ba ta san da wani abu wai shi adabin kasuwa ba lokacin da take rubuta littafinta. Ta ƙara da cewa, ta dai rubuta shi ne a lokacin tana makarantar WTC Katsina, sadda take aji uku, wato wajajen shekarar 1980. Ta kuma rubuta shi ne daga gyauron labaran da take ba 'yan uwanta ɗalibai lokacin da suke makaranta can da dare kafin su yi barci. Bayan ta gama sakandire ne ta fitar da shi ta hanyar aika shi gidan rediyon tarayya Kaduna domin a karanta a shirin 'Shafa Labari Shuni', amma sai aka daɗe ba a karanta shi ba. Daga baya ta miƙa wa wani kamfanin bakin hanya da ake kira Ogwu a Kaduna domin ya buga mata shi.  Kamfanin Ogwu ya buga, ya kuma shiga sayar da littafin da ya ga mutane sun damu suna son su karanta. A lokacin da Kamfanin Ogwu ya shiga sayar da littafin, ita Talatu tana Kwalejin Ilmi ta Kafanchan wajen ƙaro ilmi, a can ne wata ƙawarta ta zo da littafin, tana yi mata bayanin yadda littafin ya yi kasuwa ita ba ta ma sani ba. Wannan daɗin abin da ya faru ya sa ta koma gida ta ji abin da ya auku. Mahaifiyar Talatu ta ba ta kuɗin da aka samu, ta yi murna ƙwarai da ganin arzikin da wannan littafi ya jawo mata. Daga wannan lokaci ne ta shiga sake buga littafin, ana watsawa a cikin ƙasar Hausa, ta yadda abin ya dinga ba ta mamaki na ganin cewa mutane, musamman masu sayar da littatafai daga ko'ina a faɗin ƙasar Hausa ke kira ko yo saƙon don Allah ta aika masu da kwafe 500 ko dubu ko dubu biyu ko ma fiye.

Fitar wannan littafi da yanayin da ya samu kansa lokacin bugu da sayarwa da kuma hanyoyin da aka bi aka samar da shi, ya nuna wa sauran marubuta cewa ashe akwai wata hanyar rubutu da wallafa littattafai da ba dole sai ta bin kamfanonin bugu da wallafa na gwamnati ba. Saboda haka daga samuwar wannan littafi na Rabin Raina a shekarar 1984, za mu iya cewa akalar adabin hira ko ƙagaggen labari ta soma sauyawa, kuma a iya cewa daga wannan lokacin ne Adabin Kasuwar Kano ya fara ginuwa. Sai dai abin da ke da muhimmanci a nan shi ne, ba wai zama aka yi ba domin a tsara a kuma gina wannan fasali na Adabin Kasuwar Kano ba, abu ne da ya kasance caccakuɗe, kuma tattare da abubuwa mabambanta da suka hada da :

- Tun da farko dai akwai matsalar abubuwan karantawa a makarantu da kuma tsakanin sababbin makaranta kamar yadda muka yi bayani.

- Ga halin da kamfanin NNPC ya shiga daga farkon shekarun 1980 na rashin buga littatafan hira.

- Ga kuma ɗaruruwan ‘yan makaranta da waɗanda suka kammala makarantun, sun kuma rubuta littattafai masu yawa, ba wurin buga su, balle a san da su.

- Shirin gidan Rediyon Tarayya Kaduna na ‘Shafa Labari Shuni’ da wasu da dama a gidajen rediyon jihar Kano da Katsina da Sokoto da wasu wurare da dama ya taimaka wajen fito da waɗansu daga cikin marubutan da ke ~oye.

- Bugun littafin Talatu na bakin kasuwa da yadda ya sami kar~uwa ya sanya wasu, ƙila suka ce su ma bari su gwada bugawa da sayarwa.

Saboda haka, littattafan da ake ta yayatawa a halin yanzu a matsayin waɗanda suka biyo bayan littafin Talatu daga 1984, ba wai shawara suka yi da juna ba, kuma ba su san wani na yin irin wannan aiki ba, kamar yadda bincike ya nuna a halin yanzu. Ke nan jawabin da Malumfashi, (1994) ko wanda Adamu, (1996) da Adamu (2000) suka yi na lissafa littatafan da suka biyo na Talatu kamar haka ba daidai ba ne, sai dai daga littafin Talatu na Rabin Raina sai:

Ibrahim Hamza Abdullahi da Soyayya Gamon Jini a 1986.
Idris S. Imam da In Da Rai a 1987.

Balaraba Ramat da Budurwar Zuciya a 1987.

A.M Zaharadden da Kogin Soyayya a 1988**.**

Idan so cuta ne, na Yusuf M. Adamu a 1989.

An yi wannan hasashe bisa hujjar da ta nuna cewa babu wani bincike da ya tabbatar da jeruwa da daidaituwar wannan tsari ko kuma wani bayani da ya ce an tattauna tsakanin waɗannan mutane na biyo sahun Talatu Wada.Bari mu yi nazarin batun da kyau.

Tun da farko dai garuruwan marubutan daban-daban suke, Talatu na Kaduna, Ibrahim Hamza na Kano, Idris S. Imam kuwa tun 1984 aka buga littafin nasa ba wai a 1987, Balaraba kuwa ko kafin ta shigar da littafinta na Budurwar Zuciya a layin adabin kasuwa ta fuskar shiga ƙungiyar 'Raina Kama'**,** an riga an buga littafin a Zaria a kamfanin Gaskiya Corporation a 1984. Haka shi ma Zaharradeen a Kano yake, shi kuwa Yusuf Adamu yana ɗalibta a Sakkwato ne ya shigo da nasa littafin. Haka kuma daga binciken da aka gudanar an fahimci cewa, ko kafin Ibrahim Hamza Abdullahi da littafinsa na Soyayya Gamon Jini a 1986, an samar da Hannunka Mai sanda **1** na Kamarradeeen Imam a 1985. Me ya sa ba a shigar da shi cikin layin na farko ba ? Haka kuma a tsakanin 1984 da aka samar da littafin Talatu, ba wai littattafai huɗu ne suka yi tashe ba kurum guda 13 ne.

Ke nan ba wata ƙungiya ba ce ko kuma ba wani taro aka yi ba aka ce a samar da wannan abu da aka kira Adabin Kasuwar Kano daga baya. Shi kuma Malumfashi (1994) da ya kira shi da wannan suna, ya yi haka ne daga abin da ya gani masu kama da juna tsakanin littattafan da irin waɗanda aka samar a Onisha kamar yadda ya bayyana daga baya, Malumfashi (2004).

Kamar yadda muka gani can baya, rayuwar adabi takan shiga cikin wani sauyi ne na wani lokaci, daga baya kuma ta kasance cikin wani tsari na daban. Irin wannan shi ne ya faru ga abin da aka kira Adabin Kasuwar Kano yanzu. Sai dai wani abu da za a yi la'akari da shi shi ne, yawancin matasan da suka yi tashe a wancan lokaci a wannan fage ba su yi amfani da kamfanonin ɗab`i da ake da su don bayyanar da ayyukansu na adabi ga jama'a ba. Ba don komi ba kuwa sai don ba wani kamfani da ya damu ya buga ire-iren waɗannan littattafai. Ba kuma wai don ba su da kasuwa ko kuma ba su sami kar~uwa ba a tsakanin al`umma ba, a`a, a tsakanin shekarun 1978-1982 ba abin da ya fi tashe da kar~uwa kamar irin labaran da wasu suke rubutawa, suna aikawa gidajen rediyoyi daban-daban ana karantawa. Ba wani abu ya jawo hakan ba sai ganin littattafan da aka samar daga gasar da aka shirya a 1978 da suka samar da litattafan soyayya na farko da za a iya kira `yan zamani, sun yi tasiri ga rayuwar irin waɗannan matasa.

Sai dai ga alama, amfani da aka yi da kafar rediyo, wadda ta sanya ƙagaggun labarai irin waɗannan suka sami martaba, ba wai kawai tsakanin waɗanda suka yi boko ba kurum, har ga waɗanda aikinsu shi ne sauraron rediyo, amma ba su iya karatun ba. Bisa wannan tafarkin aka shiga samar da sababbin marubuta, wasu ta hanyar kwaikwayon abin da aka rubuta, suka aika gidajen rediyoyin, wasu kuma ta sake wa tatsunniyoyi da labaran Hausa fasali, wasu ko ta kwaikwayo ko ɗaukar fasalin wasu labaran Ingilishi ko fassara kai-tsaye ko kuma nade fina-finan Indiya da na Turawa zuwa takarda. Cikin ɗan lokaci ƙanƙani, sai ga kabod-kabod na gidajen rediyoyin nan sun cika maƙil, wasu ma suka shiga ƙonawa, wanda ya sa masu rubutun suka shiga guna-guni idan ba a karanta nasu labaran ba. Su kuma waɗanda Allah ya tarfa wa garinsu nono daga cikin waɗanda aka karanta nasu a gidajen rediyoyin, sai ga shi sun fara samun suna da ɗaukaka. Wannan ya jawo wasiƙu suka shiga gilmawa zuwa gare su, ana yaba masu. Ta haka kuma aka ga cewa ga wata kafa ta samu ta kashe waccan ƙishirwa ta rashin labaran Hausa da ta addabi matasa, ta yadda a tsakanin shekarar 1984 zuwa 1998 marubuta da sababbin littatafai suka baje kasuwarsu a ƙasar Hausa.

Idan aka yi nazari sosai, za a ga ko da Talatu ta bayyana a 1984 a Kaduna, ba a Kadunar ta tsaya ba, domin littattafan sun karwaɗe duk faɗin ƙasar Hausa, musamman birnin Kano da suka dasa rayuwarsu. A Kanon akwai irin littafin Talatu Wada da ya riga ya shiga kasuwa kafin ma bayyanar na Talatu, wato Wasiyar Babakere na Ibrahim Sale Gumel. A kuma wannan shekara ta 1984, an sami ɗan uwan na Talatu, wato In Da Rai Da Rabo na Idris S. Imam. Saboda haka, ko da Kamarradeen ya shigo da nasa littafin a 1985, ba dole ba ne ya san da abin da Talatu ta yi ko kuma sauran da suka riga nata shiga kasuwa, musamman ganin cewa ɗa ne ga marigayi Abubakar Imam, kuma yana aiki da kamfanin Huda-Huda da ke Zaria, wadanda su ne mawallafansa. Yadda Kano ta shigo cikin harkar da littattafan da ‘yan Kanon suka samar bai rasa nasaba da suna da tashen da littafin Talatu da na Idris Ibrahim suka yi a kasuwar Kanon. Littattafai tara ne suka wanzu a wannan lokaci a tsakanin 1986 zuwa 1989. Ga alama kuma su ne suka sanya Kano ta sami kar~uwa da Tagomashi a wannan harka ta yadda daga baya Gusau ta shigo sahu. Kanon ta sake bayyana, daga can kuma sai ga Sakkwato tare da Yusuf Adamu.

## Auna Fahimta

Domin fahimtar ko darasin ya zauna sai ɗalibai sun fayyace abubuwa kamar haka:

1. Mene ne Adabin Kasuwa?
2. Kawo taqaitaccen bayani game da Adabin Yayi

3. Waƙanne dalilai ne suka haifar da samuwar Adabin Kasuwar Kano.

## 1.4 Kammalawa

A wannan darasi an yi ƙoƙarin bayyana mene ne Adabin Kasuwar Kano ta hanyar me ake nufi da adabin kasuwa da na yayi, sa'annan an yi taƙaitaccen bayani game da Adabin Kasuwar Kano

## 1.5 Taƙaitawa

Darasin ya gabatar mana da abubuwa ne da suka haɗa da:

4. Sanin mene ne Adabin Kasuwar Kano.
5. Taƙaitaccen bayani game da adabin kasuwa.
6. Da bayani game da adabin yayi.
7. Sannan aka zo da taƙaitaccen bayani game da Adabin Kasuwar Kano.

**Jingar Aiki**

1. Me ake nufi da Adabin Kasuwar Kano?
2. Me ya bambanta adabin kasuwa da adabin yayi?

## 1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language.London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory. Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari). Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce, Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982). "Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa". Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009). Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd

Malumfashi, I. (2019). Labarin Hausa A Rubuce: 1927-2018. Zaria: ABU Press and Publishers

Malumfashi, I. (2002). Adabi da Bidiyon Kasuwar Kano a Bisa Faifai: Taƙaitaccen Tsokaci. Maƙalar da aka gabatar a Cibiyar Hausa, Jami'ar Usmanu ɗanfodiyo, Sokoto.

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa**.** Zariya: NNPC

bambadiya.blogspot.com

www.rumbunilimi.com.ng

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Adabin Kasuwa a luggance na nufin adabi na kowa da kowa ko na yayi ko abin da ke jan hankalin jama'a a kodayaushe, to ana iya cewa akwai adabin da ke da akasin haka. Saboda haka, adabin kasuwa wani ~angare ne na adabin al'umma da kowa zai iya shiga cikin kogin ya yi iyo ko kurme, masani ko malami ko manazarci ko akasin haka. Ke nan irin wannan adabi wani abu ne ko dai waƙa ko wasan kwaikwayo ko ƙananan labarai, ko rubutattaun litattafai da aka tsara a wani zangon rayuwar jama'a, ake kuma tsintar su a tsakanin jama'ar ba tare da wani kandagarki ba. Ta fuskar sayar da su ba a yi wani tanadi na wurin da ya dace ba, ko dai a same su a kasuwa ko wurin hirar matasa ko tsakanin matan aure ko makarantu ko kuma ma duk inda jama'a ke tururuwa domin karatu da rubutu.

2. Idan aka ce dabi na Yayi ne, adabi ne da yakan rayu daga wani lokaci zuwa wani, wato akwai lokacin da yake tashe, akwai kuma lokacin da yake sallacewa.

3. Dalilan da suka haifar da samuwar Adabin Kasuwar Kano sun haƙa da:
   - Matsalar abubuwan karantawa a makarantu da kuma tsakanin sababbin makaranta kamar yadda muka yi bayani.
   - Halin da kamfanin NNPC ya shiga daga farkon shekarun 1980 na rashin buga littatafan hira.
   - Taruruwar 'yan makaranta da waɗanda suka kammala makarantun, sun kuma rubuta littattafai masu yawa, ba wurin buga su, balle a san da su.
   - Shirin gidan Rediyon Tarayya Kaduna na 'Shafa Labari Shuni' da wasu da dama a gidajen rediyon jihar Kano da Katsina da Sokoto da wasu wurare da dama ya taimaka wajen fito da waɗansu daga cikin marubutan da ke ~oye.
   - Buga littafin Talatu na bakin kasuwa da yadda ya sami kar~uwa ya sanya wasu, ƙila suka ce su ma bari su gwada bugawa da sayarwa.

## Kashi Na 2 Ci Gaba Da Wanzuwar Rubutaccen Zuben Hausa

### Tabbatuwar Rubutun Zube

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Ci Gaba Da Wanzuwar Rubutaccen Zuben Hausa
    2.3.1 Gasar Shekarar 1988
    2.3.2 Gasar Injiniya Bashir {araye (2007-2010)
    2.3.3 Gasar Rubutun Zube Ta BBC
    2.3.4 Gasar Zubutun Zube Ta MMB Da Pleasant Library
2.4 Kammalawa
2.5 Taƙaitawa
2.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa

A wannan sashe an yi duba da irin cigaban da aka samu dangane da wazuwar rubutaccen zube na Hausa daga shekarar 1988 da kuma gasar da ta biyo baya.

### 2.2 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi za a fahimci ci gaban da aka samu dangane da wazuwar rubutaccen labari Hausa daga shekarar 1988 da gasar da ta biyo baya domin ingata lamarin.

### 2.3 Ci Gaba Da Wanzuwar Rubutaccen Zuben Hausa

Rubutaccen adabin na Hausa ya ci gaba da habaka. Wannan sashe an sake bibiyar yadda aka samu ci gaba dangane da wazuwar rubutaccen labari Hausa daga shekarar 1988 da gasar da ta biyo baya domin ingata lamarin.

#### 2.3.1 Gasar Shekarar 1988

Tafiya sannu-sannu, aikin bunƙasa adabi sai daɗa kankama yake yi. A cikin shekarar 1988, Hukumar Kula da Kyautata Fasaha da Al'adun ta gudanar da gasa mai kamanci da waɗanda suka gabata. Ita ma kamar sauran hukumomin da suka gabatar da gasannin, tana da manufar bayar da kyaututtuka ga wanda duk ya nuna bajinta, da kuma samar da littattafai masu samar da nishaɗi. Haka kuma, hukumar tana da ƙudurin samar da haɗin kai tsakanin al'umma, Abbas ( 2009).

Abubuwa da dama sun faru bayan ƙare wannan gasa musamman ta fuskar gasa. Cika alƙawarin da aka yi wa marubuta na cewa za a ba su kyaututtuka a kuma buga labaran da suka rubuta a matsayin littafi, a ƙarshe haƙar marubutan ba ta cimma ruwa ba, domin ba a ba su kyaututtukan ba kuma ba a buga labaran a matsayin littafi ba.

Kamar yadda aka sami marubuta da dama a wasu gasannin da suka gabata, hakan aka samu a wannan gasa, domin kuwa marubuta tare da ƙirƙirarrun labaransu da dama suka fito don nuna gwaninta da baiwar da Allah ya ba su a fagen rubutu. A ƙarshe hukumar ta tace kuma ta ɗauki na ɗauka, inda ta fasalta gasar a matsayin rukunai biyu kamar haka:

**Rukunan Farko: Rayuwa Ta Zamani**

| **Sunan Marubuci** | **Sunan Littafi** |
|---|---|
| Mahmud Barau Bambale | Kowa ya Bar Gida |
| Ibrahim Sheme | Kifin Rijiya |
| Yusuf Adamu | Dukan Ruwa |

**Rukuni Na Biyu: Rayuwa Ta Soyayya**

| **Sunan Marubuci** | **Sunan Littafi** |
|---|---|
| Shafiu Magaji Usman | Jamilu Mijin Jamila |
| Mahmud Barau Bambale | Komi Nisan Dare |
| Ban samu sunan marubucin ba | Dabaibayi |

Wannan gasa ta sami naƙasu, saboda gazawar hukumar da ta shirya ta wajen ajiye kwafin waɗannan labarai da suka shiga gasar, kuma hukumar ba ta iya buga littafi ko ƙwara ɗaya ba ballantana bayar da lada ga waɗanda suka zage damtse wajen nuna bajinta kamar yadda aka yi masu alkawali. A ƙarshe marubutan waɗannan labarai su suka sake tsara waɗansu daga cikin labaran sannan suka buga su, Gusau (2009) da Abbas, (2009).

## 2.3.2 Gasar Injiniya Bashir {araye (2007-2010)

A kwana a tashi, ƙungiyoyi da hukumomi sai ƙara ~ullowa suke yi domin ginawa tare da bunƙasa adabin Hausa musamman ta fannin rubutun zube. A cikin shekarar 2007, kwatsam sai aka sami ~ullowar gasar rubutun ƙaagaggen labari mai taken, Gasar Injiniya Muh'da Bashir {araye.

Shi dai Injiniya Muhamamd Bashir {araye wani tsohon kwamishina ne a jihar Kano a zamanin mulkin shekaru huɗu na farkon mulkin Malam Shekarau (2003-2007). Allah ya yi mashi rasuwa, kuma mutum ne mai sha'awar adabin Hausa, musamman a fannin ƙagaggun labarai. Bayan rasuwarsa ne ɗaya daga cikin matansa, watau Hajiya Balkisu Bashir {araye ta sanya wata gasa a madadin maigidanta da ya rasu, tare da ƙudurin za ta dinga gabatar da ita shekara-shekara, kuma za a fara a wannan shekara ta 2007.

Hajiya Balkisu Bashir {araye ta yi ƙoƙari tare da cika wa mijinta burinshi na sha'awar ƙagaggun labarai ta hanyar sanya gasa a tsakanin marubuta ƙagaggun labarai. A ƙarshe ta danƙa alhaki tare da jan ragamar gudanar da gasar ƙarƙashin ƙungiyar marubuta ta Nijeriya, reshen Abuja (ANA). Wannan ƙungiya ta gindaya ƙa'idojin shiga gasar da cewa, littafin hikaya ne kawai za a shiga da shi. Har ila yau ƙungiyar ta yi shelar lada ko goro da za a ba duk marubucin da ya zo na farko ko na biyu ko na uku kamar yadda Hajiya Bilkisu ta alkawarta. Duk wanda ya zo na ɗaya zai kar~i tsabar kuɗi naira dubu ɗari da hamsin (N150,000). Na biyu zai kar~i naira dubu ɗari (N100,000). Shi kuwa na uku zai sami kuɗi naira dubu hamsin (N50,000) (Aminiya, 2007).

Marubuta da dama sun zaburo musamman ganin wannan gara~asa, tare da ƙagaggun labaransu a ƙarƙashin ƙungiyar ta ANA. Kimanin littattafai goma sha tara 19 ne suka shiga gasar, amma bayan an tankaɗe kuma an rairaye an fitar da littattafai uku kacal da suka fi nuna bajinta a cikin sauran, kuma aka danƙa masu kyaututtukan kuɗi kamar yadda aka alkawarta masu a ƙarƙashin wani gagarumin shagali da aka gudanar a Hotel na Abuja. Littattafan ukun farko da aka za~a kuma suka kar~i kyaututtuka su ne:

| **Sunan Marubuci** | **Suna Littafi** |
|---|---|
| Ibrahim Sheme | 'Yartsana |
| Balaraba R. Yakubu | Matar Uba Jaraba |
| Maje El-Hajeej | Kankana |

(Aminiya, 2007).

A cikin shekarar 2008 {ungiyar nan ta gasar rubutu ƙarƙashin gidauniyar tunawa da Injiniya Muhammad Bashir {araye ita ce ta sake ~ullowa da wata gasa a cikin wannan shekara ta 2009. Ita ma kamar waccan, mai ɗakin marigayi Injiniya Bashir {araye, watau Hajiya Bilkisu ta ɗauki nauyin gudanar da ita tare da bayar da na goro ga mutum ukun farko da suka nuna bajinta fiye da kowa.

A wannan karon, shugabannin shirya gasar sun gindaya sharaɗin rubutun ƙiƙira na labarun zube ne kawai za a shiga gasar da su. Gasar ta sami kar~uwa matuƙa a hannun marubuta ainun, domin sun ~ullo daga

kowace kusurwa da labaransu iri daban-daban. Bayan tacewa da alkalan gasar suka yi, sun fito da littattafai guda shidda a ~angaren zube waɗanda suka tsallake siraɗin amma guda ukun farko aka miƙa wa marubutan kyaututtuka kamar haka:

| **Sunan Marubuci** | **Littafi** |
|---|---|
| Bashir Usman Tofa | Mu sha Dariya |
| Muhammadu L. Barista | Walƙiya |
| Hafsatu Abdulwaheed | Saba ɗan Sababi |
| Dakta Bukar Usman | Marainiya |
| Dakta Bukar Usman | Jarumin Sarki |
| Dakta Bukar Usman | Yarima da Zabbi |

Kamar yadda muka ambata tun daga farko, ukun farko suka sami kyuatar Naira dubu ɗari da hamsin ga na farko (N150,000) na biyu ya sami naira dubu ɗari (N100,000) a yayin da na uku ya kar~i dubu hamsin (N50,000). Amma wanda ya zo na huɗu da na biyar da na shidda ba su sami kyauta ba. (Aminiya, 2009).

A taron da ƙungiyar marubuta ta ƙasa watau (ANA) ta yi a cikin shekarar 2009, kuma wadda ke kula da alhakin gudanar da gasar ƙagaggun labarai ta marigayi Injiniya Bashir {araye ta fitar da sakamakon waɗanda suka shiga gasar a wannan karon a fannin wasan kwaikwayo, kuma suka taka rawar gani. A wannan fage littattafan da suka taka rawar gani a wasan kwaikwayon sun haɗa da:

| **Sunan Marubuci** | **Littafi** |
|---|---|
| Ado Ahmad Gidan Dabino | Malam Zalimu |
| Kabiru Isa Anka | Kowa ya yi da kyau |
| Khalid Imam | Sodangi |
| Ibrahim M. Da K. Gwarzo | Gyara kayanka |
| S.B. Yakasai | Tsakanin ɗan Adam |

(Hira da Gidan Dabino da Aminiya, 2009).

### 2.3.3 Gasar Rubutun Zube Ta BBC

A shekarar 2016 ne hukumar gidan rediyon BBC da ke London suka assasa sabuwar gasar rubutun gajerun labarai ta mata zalla tare da bayar da maƙudan kuɗi ga waɗanda suka cinye gasar. Zubin farko dai waɗanda suka yi nasara su ne:

| **Sunan Marubuci** | **Littafi** |
|---|---|
| Aisha Muhammad Sabitu | Sansanin‘Yan Gudun Hijira |
| Amina Alhassan Abdulsalam | Sai Yaushe |
| Amina Gambo | In Da Rai |

An ƙara irin wannan gasar a 2017 inda kuma aka samu waɗanda suka yi nasara kamar haka:

| **Sunan Marubuci** | **Littafi** |
|---|---|
| Maimuna Sani Beli | Bai kai zuci ba |
| Bilkisu Sani Makaranta | Zawarcina |
| Habiba Abubakar da Hindatu S. N. | Sana’a Sa’a |

### 2.3.4 Gasar Rubutun Zube Ta MMB Da Pleasant Library

A daidai lokacin da hukumar gidan rediyon BBC ke shirya wannan gasa ta biyu a 2017, wata hukuma ta Pleasant Library da Makarantar Malam Bambadiya sun fitar da tsarin tasu gasar wadda ita ma ta rubutun gajerun labarai ce cikin Hausa. An kuma fafata inda daga baya aka samar da sakamako kamar haka:

| **Sunan Marubuci** | **Littafi** |
|---|---|
| Kabiru Yusf Fagge | Matalauciyar Rayuwa |
| Hassana Abdullahi Hunƙuyi | A Sasanta |
| Zakariyya Haruna ɗanladi | Da Sandar Hannunka |

Gasar Rubutattun labarai ba ƙaramin muhimmin al’amari ba ce a fagen adabin Hausa. {irƙiro gasar rubutattun labarai da Turawan mulkin mallaka suka yi, ya taimaka ƙwarai ga ci gaban adabin Hausa, domin maƙasudin shiryawa da gudanar da gasar duk an cimma nasara.

Maƙasudin ~ullo da gasa ta rubuta ƙagaggen labari kamar yadda Turawan suka bayyana ya haɗa da gano yanayin al’adu da adabin mutanen Afirka, musamma ƙasar Hausa. Daga baya kuma al’amarin ya zama domin a magance matsalolin ƙarancin littattafan koyo da koyarwa da ya addabi makarantun bokon ƙasar Hausa.

Sanadiyar gudanar da gasa a Afirka ta Yamma, musamman a wasu sassa na ƙasar Hausa ta samar da nasarori masu tarin yawa waɗanda suka haɗa da samar da wadatattun littattafan koyo da koyarwa a kusan kowace makarantar Boko da ke ƙasar Hausa daga wannan lokaci zuwa yau.

Wani muhimmin abu da shigo da gasa ya samar shi ne, fito da haziƙan marubuta a duniyar rubutu. Dalilin gudanar da gasar aka sami haziƙan

Hausawa 'yan ƙasa suka fito fili tare da rubutattun littatafansu, kuma sunansu ya shiga duniya aka san su. Misalin su Abubakar Imam Kagara da Ibrahim Sheme waɗanda suka riƙe muƙamai da dama a fannoni iri daban-daban duk saboda hazaƙar da suka nuna a fagen rubutu.

Muhimmancin fito da gasa bai tsaya nan ba sai da ya kai ga sanya wa al'umma sha'awa a zukatansu na ganin sun zaburo domin bayar da tasu gudumuwar ko ta fagen karanta irin labaran da gasar ta samar ko kuma domin su bayar da tasu gudunmuwar wajen rubutun labarai. Ba jama'a kawai suka sami wannan sha'awa ba, har da ƙungiyoyi da hukumomi masu zaman kansu sun nuna sha'awarsu ta wajen bayar da gudunmuwa ko dai su buga littatafan ko kuma su shirya gudanar da gasar, misali ƙungiyar marubuta ta ƙasa (ANA).

Shiryawa da gudanar da gasar rubuta labari ta taimaka matuƙa wajen fito da jigon adabin Hausa a manya da ƙananan makarantun bokon ƙasar Hausa tare da yayata shi a fannoni mabambanta, domin ta wannan hanya ce ɗalibai da malamansu suka sami koyon tsara labarai na kansu tare da yin nazarin wasu littattafai na adabin Hausa.

Wani muhimmin al'amari da shiryawa tare da gudanar da gasa ya samar shi ne, samar da sababbin littattafai a fagen nazarin rubutattun labarai na Hausa. Kafin fara gudanar da gasa, babu wani littafi mai kamanci da rubutaccen labari na zamani, saboda masu ilimi na wancan lokacin suna ƙyamatar al'amarin, domin suna yi mashi kallon hadarin kaji, saboda cewa suke yi ƙarya ce, kuma ƙarya haramun ce ga addini.

Ire-iren rubutattun littatafan labarai da gasa ta samar sun taimaka matuƙa wajen samar da nishaɗi da fa'idoji waɗanda ba su misaltuwa, musamman ta fannin ɗabi'u da kyautata tarbiyya da zamantakewa. Baya ga waɗannan kuma an sami hanyar bunƙasar ilimi ta fannoni da dama.

Ya zuwa yanzu, ~ullo da gasa da Turawan mulkin mallaka suka yi, ya bar gado ga samuwar muɗaba'u daban-daban da suka tsayu ga wallafa littattafan da aka rubuta a kan labarai. Baya ga wannan, Adabin Kasuwar Kano ya sami tushe a fagen kuma ya zama abin nazari daga wannan tsari na gasa.

**Auna Fahimta**

Domin fahimtar ko darasin ya zauna sai ɗalibai sun fayyace abubuwa kamar haka:

1. Wacce hukuma ce ta shirya gasar 1988?
2. Wanne sharaɗi masu shirya gasar Injiniya Bashir {araye (2007-2010) suka gidaya?

3. Gasar Rubutattun labarai ba ƙaramin muhimmin al'amari ba ce a fagen adabin Hausa. Tattauna

## 2.4 Kammalawa

A wannan darasi an ƙoƙarta sanin irin ci gaban da aka samu game da wanzuwar rubutaccen zuben Hausa da yadda aka gudanar da gasar shekarar 1988 da wadda ta biyo baya ta Injiniya Bashir {araye (2007-2010) da kuma yadda gasar rubutun zube ta BBC ta somo. Da yadda aka gudanar da gasar rubutun zube ta MMB da Pleasant Library.

## 2.5 Taƙaitawa

Darasin ya gabatar mana da abubuwa ne da suka haɗa da:

- Ci gaba da wanzuwar rubutaccen zuben Hausa
- Gasar shekarar 1988
- Gasar Injiniya Bashir {araye (2007-2010)
- Gasar rubutun zube ta BBC
- Gasar rubutun zube ta MMB da Pleasant Library

### Jingar Aiki

1. Me ya faru bayan tabbatuwar Adabin Kasuwar Kano?
2. Me ya jawo gasar shekarar 1988?
3. Wace gudunmuwa gasar Injiniya {araye ta samar a ƙasar Hausa?
4. Tattaunna yadda gasar Hikayata ta BBC ta kasance daga 2017.

## 2.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language. London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory. Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari). Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce, Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982). "Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa". Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009). Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd

Malumfashi, I. (2019). Labarin Hausa A Rubuce: 1927-2018. Zaria: ABU Press and Publishers

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa**.** Zariya**:** NNPC

bambadiya.blogspot.com
www.rumbunilimi.com.ng

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Hukumar Kula da Kyautata Fasaha da Al'adu.
2. Shugabannin shirya gasar sun gindaya sharaɗin rubutun ƙiƙira na labarun zube ne kawai za a shiga gasar da su.
3. Gasar Rubutattun labarai ba ƙaramin muhimmin al'amari ba ce a fagen adabin Hausa. Gasar rubutattun labarai da Turawan mulkin mallaka suka yi, ya taimaka ƙwarai ga ci gaban adabin Hausa, domin an magance matsalolin ƙarancin littattafan koyo da koyarwa da ya addabi makarantun bokon ƙasar Hausa. Gasar ta taimaka wajen fito da haziƙan marubuta a duniyar rubutu. Haka kuma an sanyawa al'umma sha'awa a zukatansu na ganin sun zaburo domin bayar da tasu gudumuwar ko ta fagen karanta irin labaran da gasar ta samar ko kuma domin su bayar da tasu gudunmuwar wajen rubutun labarai.

## KASHI NA 3

## Tabbatuwar Rubutun Zube

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Wasu Hanyoyin Nazarin Labaran Zube
  3.3.1 Jigo
  3.3.2 Warwarar Jigo
  3.3.3 Nazarin Jigo A Wasu Rubutattun Labaran Hausa
3.4 Kammalawa
3.5 Taƙaitawa
  Jingar Aiki
3.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 3.1 Gabatarwa

A wannan darasi za a bibiyi hanyoyin nazarin labaran zube waƙanda suka qunshi, jigo da warwarar jigo da nazarin salo.



### 3.2 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi ƙalibai za su fahimci hanyoyin nazarin labaran zube.

### 3.3 Wasu Hanyoyin Nazarin Labaran Zube

Hanyoyin nazari uku za mu bi domin mu aza misalin yadda za a iya kallon labaran zube. Akwai Jigo da Warwarar Jigo da kuma Nazarin Salo.

### 3.3.1 Jigo

Jigo kalma ce Bahaushiya da ke da ma'anoni mabambanta. Tun da farko Hausawa na yi mata kallon ginshiƙi da ke cikin ɗaki ko kuma gini. Haka ma suna kallon ta a matsayin tubali ko tushe ko fandishin da ke ɗauke da gini. Haka kuma suna yi mata kallon wani muhimmin kayan aikin da masu noman fadama ke amfani da shi wajen ban ruwa. Idan aka dubi waɗannan ma'anoni da Bahaushe ya bayyana game da jigo za a ga cewa, ba wani abu suke nufi ba face mazaunin abu, ko mafarinsa ko kuma abu mai muhimmanci da ƙila in ba shi a cikin tsari wani abu ba zai wanzu ba. Misali, ginin da ba ya da fandishin da wuya ya yi ƙarko. Mai noman

fadama da ba ya da ƙwaryar da take kai ruwa ga gona, da wuya noman ya ɗore. Haka kuma ɗakin da ba ya da ginshiƙi da wuya ya yi ƙarko.

Ke nan wannan kalma ta jigo ita ce masu adabi suka aro suka mayar da shi a matsayin saƙo ko manufa ko abin da waƙa ko zube ko wasan kwaikwayo suka ƙunsa. A nan ana maganar abin da labarin ya ƙunsa ko yake magana kai ko kuma ruhinsa. Wato dai, duk wani abu da in ba shi a cikin labarin to da wuya labarin ya zauna ko ya yi armashi.

Saboda haka, idan ana magana kan jigon labarin zube, to ana nuni ne ga babbar manufar marubucin, wato wadda ita ce a zuciyarsa a lokacin da yake ƙoƙarin tsara labarin. Alal misali, labarin Ruwan Bagaja babban jigonsa bai wuce shashantarwa ba, ko kuma a ce nishaɗantarwa. Wato an gina labarin domin a sa dariya da nishaɗi. Ko kuma littafin Jiki Magayi da ya kasance bisa tunanin soyayya, ko kuma Shaihu Umar da ke faɗakarwa ko labarin Amina ko Mace Mutum da ke neman ‘yancin mata.

Abin da za a ƙara a nan shi ne, baya ga babban jigo ana kuma da ƙananan jigogi da suke taimakawa wajen gina labarin, su waɗannan kuma kowane mai nazari da yadda yake kallon su. Alal misali, a cikin lbarin Ruwan Bagaja akwai ƙaramin  jigon ƙara da ilmi da yawon buɗe ido da wasu da dama. Haka ma a labarin Shaihu Umar an sami ƙananan jigogi irin na ilmi da soyayya da makamantansu.

### 3.3.2Warwarar Jigo

Abin da ake nufi da warware jigo kuwa bai wuce mai nazari ya bi zaren da ya ɗinke labarin ba yana yi masa ƙulli ta yadda zai sami hadi guda, wato ya buɗe labarin nasa, sa’annan ya ja zaren ta amfani da babban jigon domin ya tabbatar saƙon bai fanɗare ba. Ana iya ganin haka a cikin labarin So Aljannar Duniya inda aka ɗinke zaren da kitsa soyayyar Baɗɗo da Yasir. Ko kuma ban dariyar da ke cikin labarin Ruwan Bagaja har zuwa ƙarshen labarin da za a dire da wani abu na daban.

Nazarin Jigo A Wasu Rubutattun Labaran Hausa*****************

Auna Fahimta
Domin fahimtar ko darasin ya zauna sai ɗalibai sun fayyace abubuwa kamar haka:
Waƙanne hanyoyi ake amfani da su wajen nazarin labarin zube? Kawo su.
Kawo taqaitaccen bayani game da jigo.

## 3.4 Kammalawa

A wannan darasi an dubi abubuwa da suka haɗa da hanyoyin nazarin labaran Hausa da suka haɗa da jigo da warwararsa da kuma yadda ake nazarin jigo a wasu rubutattun labaran Hausa.

## 3.5 Taƙaitawa

Darasin ya gabatar mana da abubuwa ne da suka haɗa da:

- Bayani game hanyoyin nazarin labaran Hausa.
- An dubi jigo da warwararsa.
- An kuma dubi yadda ake nazarin jigo a wasu rubutattun labaran Hausa.

**Jingar Aiki**

1. Mene ne jigo?
2. Yaya ake warwarar jigo a nazarin zuben Hausa?
3. Me ake nufi da warwarar jigo?

## 3.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language. London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Penguin Dictionary of Literary Terms and Literary Theory. Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari). Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce, Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982). “Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa”. Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009). Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd

Malumfashi, I. (2019). Labarin Hausa A Rubuce: 1927-2018. Zaria: ABU Press and Publishers

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa**.** Zariya: NNPC

bambadiya.blogspot.com

www.rumbunilimi.com.ng

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. jigo
warwarar jigo
nazarin salo

2. Jigo saƙo ne ko manufa ko abin da waƙa ko zube ko wasan kwaikwayo suka ƙunsa. A nan ana maganar abin da labarin ya ƙunsa ko yake magana kai ko kuma ruhinsa. Wato dai, duk wani abu da in ba shi a cikin labarin to da wuya labarin ya zauna ko ya yi armashi.
3. Warwarar jigo shi ne yadda mai nazari yake bin zaren da ya ɗinke labarin ba yana yi masa ƙulli ta yadda zai sami haɗi guda, wato ya buɗe labarin nasa, sa'annan ya ja zaren ta amfani da babban jigon domin ya tabbatar saƙon bai fanɗare b

# KASHI NA 4

## Tabbatuwar Rubutun Zube

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Wasu Hanyoyin Nazarin Salo A Labaran Zube
4.3.1 Za~in Kalmomi
4.3.2 Dabara
4.3.3 Mutum
4.4 Kammalawa
4.5 Taƙaitawa
4.6 Jingar Aiki
4.7 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

## 4.1 Gabatarwa

Salo kalmomi ne da mai rubutu ya za~a da gangan domin ya gina labarinsa ko waƙa ko kuma wasan kwaikwayo kuma za a iya nazarinsa ta hanyoyi guda uku. A wannan darasin za a yi nazarin waƙannan hanyoyi da ake bi domin nazarin salo a labaran zube.

## 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci hanyoyin nazarin salo a labaran zube.

## 4.3 Wasu Hanyoyin Nazarin Salo A Labaran Zube

Shi kuwa nazarin salo a labaran zube hanyoyi uku suke yi masa jagora:

- Za~in kalmomi
- Dabara
- Mutum

### 4.3.1 Za~in Kalmomi

Idan ana son a fahimci salo to ya dace a gane irin siffofinsa na asali. Ba wani abu ba ne salo face irin kalmomin da mai rubutu ya za~a da gangan domin ya gina labarinsa ko waƙa ko kuma wasan kwaikwayo. Idan aka ce salo zabi ne na kalmomi, ana nufin gwaninta ce mutum ya

za~i kalmomin da za su burge ko su sa tunani a wajen mai karatu. Alal misali a waka:
'Yar budurwa son ki nake,
Kin bugan sarka a wuya.

In na yo carar zakara,
Kyarkyarata gun ki take.

Shi ko wancan son da yake,
Duk bidar zakinki yake.

Daga waɗannan baitoci za a ga cewa mai waƙar ya zaƙi kalmomi ne da gangan domin ya gina waƙar cikin armashi da burgewa. Kalmomi irin su 'Sarka' da 'carar zakara' da 'kyarkyara' da 'zaƙinki' duk an za~e su ne domin su dace da irin salon da aka yi amfani da shi.

Haka batun yake a cikin tsarin rubutun zube. Dubi yadda marubucin Kifin Rijiya ya bayyana wahalar da Shaihu Aboki ya sha a duniya: 'Irin wahalolin da ya sha, da ƙulli-kucciyan da ya sha yi da haɗurra...' Ta yaya ake yin ƙulli-kucciya, wannan za~in kalmomi na musamman domin gina salo. Ko kuma yadda aka bayyana cin hanci a cikin labarin Ruwan Bagaja ta sakaya cin hancin ta amfani da dabara.

### 4.3.2 Dabara

Haka ana ganin salo a matsayin dabara ko gwaninta ko iyawa ko wata hanya ta burgewa a lokacin isar da saƙon marubucin. Dabarar a nan tana iya zuwa ta fuskoki daban-daban. Ko dai ta hanyar buɗe labarin ko gina cikinsa ko kuma dire shi. Alal misali, akwai salon da aka saba wajen buɗe labari irin: 'A wata kasa'**...** a 'A wani gari'**...** ko kuma **'**A wani shudadden zamani' ko **'**Wata rana'**...** da sauran su. Amma sai a ga marubuci ya kauce wannan tsari da gangan, ya kitsa nasa. Misali, a cikin labarin {arshen Alewa {asa, an buɗe ne da wani salo na musamman: Tin kwal! Tin kwal!! Tin kwal!!! Kai za ka ɗauka daka ne ake yi ba labari ba.

### 4.3.3 Mutum

Idan an ce mutum ne salo, ana magana ne bisa irin yadda Ubangiji ya tsira kowane ɗan Adam. Ba mutum biyu da suke kama da juna ta kowace irin fuska ko hali. Haka kuma tunanin kowane mutum daban yake da na ɗan uwansa. Ke nan abin da wani ya kitsa a labarinsa yana tafiya da salon rayuwarsa ne. Duk irin yadda mmarubuci yake gudun sanya halinsa ko rayuwarsa ba zai yiwu ba. Wannan ya ƙara tabbatar mana da cewa, halayyar ɗan Adam ita ke gudanar da salon da ake gani a cikin labarin da ya rubuta. Alal misali, salon ban dariya na Abubakar

Imam a cikin Ruwan Bagaja ko salon ƙaddara na Abubakar Tafawa Balewa a cikin Shaihu Umar ko salon tashin hankali a cikin labarin {arshen Alewa {asa na Bature Gagare abubuwa ne da suke ginu bisa rayuwar marubutan. Dangane da haka ake ganin, salon kowane mutum na bayyana ne daga ginuwar rayuwarsa.

**Auna Fahimta**

Domin fahimtar ko darasin ya zauna sai ɗalibai sun fayyace abubuwa kamar haka:

1. Kawo hanyoyin da ake bi domin nazarin salo a labaran zube.
2. Me ake nufi da dabara a nazarin salo?
3. Ya matsayin mutum yake a nazarin salo?

## 4.4 Kammalawa

A wannan darasi an koyi abubuwa da suka haɗa da hanyoyin da ake bi don nazarin salo a labaran zube da yadda ake za~in kalmomi da amfaninsu a nazarin salo. An kuma biyo da ƙoƙarin sanin me ake nufi da dabara a nazarin salo da yadda matsayin mutuum yake a nazarin salo.

## 4.5 Taƙaitawa

Darasin ya gabatar mana da abubuwa ne da suka haɗa da:

1. Hanyoyin da ake bi don nazarin salo a labaran zube.
2. Yadda ake za~in kalmomi da amfaninsu a nazarin salo.
3. Me ake nufi da dabara a nazarin salo?
4. Ya matsayin mutum yake a nazarin salo?

**Jingar Aiki**

1. Waɗanne hanyoyi ake bi domin nazarin salo a Hausa?
2. Ya ake za~in Kalmomi waje nazari salo labaran Hausa?

## 4.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Karin Nazari

Abraham, R.C. (1962). Dictionary of the Hausa Language. London: Hodder & Stoughton Ltd

Cuddon, J. A. (1976). The Pengui Dictionary of Literary Terms and Literary Theory. Oxford: Penguin Books

ɗangambo, A. (1984) Rabe-Raben Adabin Hausa (sabon tsari). Zaria: Amana Publishers

Gusau, S.M. (2000) Tatsuniya A Rubuce, Kano: Benchmark Publishers

Magaji, A. (1982). "Tasirin Adabin Baka A kan Rubutattun {agaggun Labaran Hausa". Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Malumfashi, I. (2009). Adabin Abubakar Imam. Sakkwato: Garkuwa Media Service Ltd

Malumfashi, I. (2019). Labarin Hausa A Rubuce: 1927-2018. Zaria: ABU Press and Publishers

Yahaya, I.Y. (1988). Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa**.** Zariya: NNPC

bambadiya.blogspot.com
www.rumbunilimi.com.ng

## 4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1.
Za~in Kalmomi
Dabara
Mutum

2. Dabara a matsayin salo tana iya zuwa ta fuskoki daban-daban. Ko dai ta hanyar buɗe labarin ko gina cikinsa ko kuma dire shi. Alal misali, akwai salon da aka saba wajen buɗe labari irin: 'A wata kasa'**...** a 'A wani gari'**...** ko kuma **'**A wani shudadden zamani' ko **'**Wata rana'**...** da sauran su. Amma sai a ga marubuci ya kauce wannan tsari da gangan, ya kitsa nasa. Misali, a cikin labarin {arshen Alewa {asa, an buɗe ne da wani salo na musamman: Tin kwal! Tin kwal!! Tin kwal!!! Kai za ka ɗauka daka ne ake yi ba labari ba.
3. Wannan na nuna cewa kowane mutum daban yake da na ɗan uwansa. Ke nan abin da wani ya kitsa a labarinsa yana tafiya da salon rayuwarsa ne. Duk irin yadda marubuci yake gudun sanya halinsa ko rayuwarsa ba zai yiwu domin halayyar ɗan Adam ita ke gudanar da salon da ake gani a cikin labarin da ya rubuta. Alal misali, salon ban dariya na Abubakar Imam a cikin Ruwan Bagaja ko salon ƙaddara na Abubakar Tafawa Balewa a cikin Shaihu Umar ko salon tashin hankali a cikin labarin {arshen Alewa {asa na Bature